Follow this link to join my WhatsApp group:
https://chat.whatsapp.com/LQfVU1ABdFI14btWRhUB1K

SAKACINA KO HALIN MAZA?*

*RUBUTAWA:-*
*JAMILA LAWAL ZANGO*

*FIRST CLASS WRITER'S ASSO....*

*SHAFI NA ƊAYA*

REPOSTING
Sanin cewar a kwai banbanci a cikin duniyar da Allah subuhanahu wata ala ya halitta masu ɗauke da halittu mabanbanta jinsi,bayan ya halicci duniyar mutane, da kuma waɗanda ba'a ji ko gani gare su sai dai duk wanda ya yi imani,ya na da yaƙinin samuwarsu a cikin duniyar da muke cikinta,da sauran halittu na dabbobi.Allah gwani wanda ba shi da abokin tarayya a cikin gwanintar halintunsa,ya halicci mutane ya kuma nuna babu wani banbanci a tsaƙanin su,sai wanda ya fi wani tsoron kiyaye abin da ya sharaɗa game da bautarsa,tabbas wannan haka ya ke a gurin Allah,amma kuma yayin da jinsi na bil'adama suka ɗauki sabanin haka,sun ɗora mizanin hankalin su suna auna banbanci na jinsi ta hanyar duba ga mulki,kuɗi ko kyawu na halitta.Su na kallon waɗanda suka mallaki waɗannan ababen na more rayuwa ga mafi ƙololuwar more rayuwa,wanda duniya ta yi maraba da zuwan sa kuma su ke kurɓan ruwan mafi ƙololuwar ɗaɗi a cikin ta.
Haka ta kasance ga wannan matashi mai cike da kyawu da kuɗi da kuma baiwar ilmi da Allah ya azurta shi dashi,ya na ji da kansa da kuma kalar rayuwar da ya tsinci kansa a cikin ta,bai san a kwai wani ƙunci ko wani ƙalubale da Allah ya ke jarabtar bayin sa,waɗanda suka yi imani domin ya gwada ƙarfin imanin su da shi.
Tabbas duniya ta na gara masa ƙwallo yadda ya ke so,domin ya fito daga cikin farin jadawali na tsarin rayuwarsa don ya yi gam da katar da bai fito daga cikin baƙin jadawali ba!Waɗanda da duniya ta ke musu kamun kazar kuku, su shiga halin ƙaƙa na iya tare da tunanin makomar rayuwar su.
Sanye ya ke cikin shadda ruwan bula gizina,sai ɗaukar ido da sheƙi take ga wani daddaɗan ƙamshi da ke tashi a jikin sa wanda ya ke sanyaya zuciyar duk wanda ya shaƙi ƙamshin.
Tuƙi ya ke cikin gwanance wa da kuma yanga,dan yadda yake jan motar ya ke kamar mai jin bacci ya na lumshe idanunsa masu kama da mai jin bacci.Gefen sa amininsa wato Ak ya ke zaune a kujerar mai zaman banza da wayarsa riƙe a hannunsa ya na dannawa.Jefi-jefi su na taɓa hira duk da hirar ta su,ba ta wuce na 'yan dakiƙa yayin da shuru yafi yawa a tsakanin

su,kasancewar ta kowannen su ya na ji da kansa, dan sun haɗu ta ko ina ga kyau kuɗi da kuma wayewa da tsantsar ilmi.

Wani irin ƙara motar ta yi ya ja birki ya tsaya cikin tashin hankali ganin wani tsoho ya shige masa gaba har ya buge shi da motar.Ya tsaya ya na kallon gurin da takaici,ganin yadda tsohon ya ke son ɓata mishi lokaci.
Da sauri ya kuma buɗe murfin ƙoofar zai fita ya na faɗin"Wannan wawan mutumin zai ɓata min lokaci,an gaya mishi bani da aikin yi ne?" Ya fice ba tare da ya kula Ak da yake mishi magana ba,da sauri Ak shima ya fito sanin halin shi sai dai kafin ya ƙara sa Am ya wanka ma wannan tsohon mari har guda biyu.
"Ba ka da hankali ne da wannan banzan ƙarfen na ka zaka ɓata min lokaci?Shashasha kawai!" 'Dan tsohon ya yi taga-taga ya faɗi har ya na fasa baki,da sauri Ak ya kama hannunsa ya mike sai kawai ya fashe da kuka,don shi kaɗai yasan halin da yake ciki.
"Haba A.m ya zaka mari wanda ya haifeka rashin mutincin na ka ya kai haka?Dubi halin da yake ciki amma baka tausaya mishi ba."
Harara ya watsa mishi kamar ba zai ce komai ba,har ya fara taku zuwa motar shi sai kuma ya buɗe baki ya ce,
"Kai baka ganin abin da ya yi min?Jiya na fara hawa motar nan amma ya ƙuje min mota.Nasan kaf zuriyarsa babu wanda zai iya siyan ko da tayar motar ce."A.k ya yi shuru ya na kallonsa cikin takaicin halin sa,na rashin daraja talaka da nuna tsantsar tsana da hantara,amma shi a ganin sa ya kama ta ya dinga kawaici saboda yasan waye Ak kuma waye asalinsa.
"Da izinin Allah sai ka sami dai-dai da kai ya faɗa ya na jin tsoro kasancewarta yasan waye shi ɗa ne ga Alhaji Muhammad Turaki,waye bai san wannan family masu ji da kuɗi da ilmi da wayewa.Cikin sa'a sai A.m bai ji abin da ya faɗi ba don ya juya ya nufi motarsa ya na tsaki.
A.k ya zaro kuɗi masu yawa ya miƙa mishi ya na ce wa." Gashi Baba ka yi haƙuri don Allah ka je asibiti a duba ka." Ya faɗa ganin duk ya ƙuje a hannunsa.Da sauri ya karɓe ya na godiya,ganin kuɗ'in da ya ba shi dan shi gaba ta kai shi ,dama ya fito zai je ya saida kekensa gashi kuma ya sami wannan kuɗi.
'Dan tsohon ya dinga saka mishi albarka ya na hawaye kamar zai yi mishi sujjada, juyawa ya yi ya nufin motar da A.m yake ƙoƙarin tayar wa,sai kuma ya tsaya ya na kallon titin da alamun abin hawa yake nema a ransa ya na jin kawai ya haƙura da abokantakansu don ya sama ma zuciyar sa salama,da irin cin kashin da A.m yake yi wa talaka a gaban sa.
A.m ya kashe motar ya fito ya na mishi maganar ya shigo,amma ko kallon inda yake bai yi ba sai ma juyar da kansa da ya yi,ya na kallon titi fuskar sa kamar an aiko mishi da mala'ikan mutuwa.
"Well." Ya ce tare da ɗaga kafaɗunsa ya juya ya na faɗin"Shike nan tun da baza ka taho muje ba ni na tafi,sai mun haɗu a ofis ka taho min da fayal ɗin da mukai maganar dakai,sannan ka shirya gobe ne tafiyar mu". Ya ta da motar ya bar gurin A.k na kallon motarsa har ta ɓace wa ganinsa,ya ja numfashi mai zafi ya fesar ya riƙe habbar shi ya na jiran ɗan acaba,sai kuma ya fasa hawa mashin ya fara taku ahankali ya na jiran adaidaita.Tafiya kaɗan ya yi ransa a jagule ya na jin zafin yadda yake nuna tsanar talaka karara baya kawaici a gabansa,yasan cewar bazai taɓa iya canza aminin nasa ba don tsanar talaka a jinisa yake kasancewar duk family d'insu basa son talaka ya rabe su,shi kansa don Allah ya bashi tarin baiwar ilmin kasancewar

Allah ya yi mishi baiwa da samin na'ura mai ƙwaƙwalwa,kuma saida suka mai da shi wani don yanzu ya na jin kansa a cikin jerin masu hannu da shuni.
Murmushi ya so ya suɓuce mishi sai kuma ya dake,ya kauda kansa tamkar bai ga motar A.m da ta yi ribas ta dawo ba,da ma yasan dole ya dawo kamar yadda suka saba duk sanda suka yi faɗa a tsakaninsu, wanda ba ya wuce sati don A.m bashi da haƙuri ko kaɗan gidan su da gurin aiki duk sun san haka,shi kuma A.k ba ya ɗaukar raini mafi yawancin lokuta mutane su na mamakin yadda abokantakarsu ta yi ƙarko a haka don kullum cikin faɗa suke kamar wasu yara Daddy shi ne ɗan sasanci,sam baya gajiya kasancewar ya na ji da shi saboda irin ci gaba da ya ke kawo mishi a cikin kampanin sa,ya sani cewar in har babu A.k to kampaninsa bazai ci ga ba.
A.k ya kauda kansa bai tanka mishi ba sai wayar sa da ya ciro da nufin ya kira direban sa ya zo ya ɗauke shi,don ya fasa shiga cikin a daidaita."Ganin ya taho kamar zai buge shi da motar amma bai kula ba,sai ɗauke kansa da ya na kallon gefe don cike yake dashi.
A.m ya leƙo ta tagar motar sa ya ce ya na murmushi mugunta,don daga ganin yadda ya yi ya san ya gaji matuƙa."Don Allah ka zo mu tafi kasan dole na dawo,Daddy ya kira ni ya na son ganin mu". Banza ya yi da shi ya ci gaba da tafiya,ganin haka ya fito  tare da kashe motar sai kawai ya kama shi da kokuwa zai tura shi cikin motar,kamar dai yadda suka saba duk lokacin da suka yi fad'a.
Bai wani ja ba ya shige cikin motar ransa a haɗe,dariya sosai A.m yake mishi don ya na matuƙar son aminin nasa saboda riƙo da gaskiya, kuma bashi da shishshigi a lamuran sa.
Tun da suka shiga cikin motar babu wanda ya yi ko tari a cikin su,da ma ɗabi'ar su ce shirin basu cika magana ba kasancewar kowa naji da kansa.
Wayar A.k ta yi ƙara alamun ana kira amma sai A.m ya kai hannunsa ya kashe wayar baki ɗaya,don yasan mai kiran taɓe bakinsa ya yi ya ci gaba da tuƙi cikin kwanciyar hankali.A k ya ja fasali tare da buɗe baki da nufin ya yi magana,amma da ya kula rigima yake ji sai kawai ya kauda kanshi bai ce ƙala ba don har yanzu ransa a ɓace yake da abin da A.m ya yi ma mutumim da ya haife shi.
Ko da suka ƙaraso tangamememm get ɗin gidan mai gadi ya buɗe musu get,A.m ya yi parking bai kula da gaisuwar da maigadin yake mishi ba ya shige cikin gidan,yayin da A.k yabi bayan sa kasancewar ba'a yi mishi shamaki da cikin gidan ba.

*******

Juwairiya zaune a gefen ƙanin ta Ibrahim ta zuba mishi idanu, ya yin da  hawaye suke gasar turarreniya a fuskarta,ji ta ke kamar ta yi hauka tsabar damuwa ta na jin wani irin baƙin cikin halin da suka tsinci kansu. Zura hannunta ta yi a  cikin kofin ruwa ta shafi fuskar Ibrahim da yake kwance rai kwakwai mutu kwakwai,sai kuma ta kama shi ganin yadda ya zaburat amkar zai shiɗe.
Mama da ke tsaye a bakin ƙofa fuskarta ɗauke da tsananin damuwa da ƙunci ta janye tagumin da ta yi tare da ajiyan zuciya mai ƙarfi."Anty Juwairiya mutuwa zan yi ga shi Baba ya ƙi dawowa."
Ya faɗa da wata irin murya da yake ƙoƙarin haɗa kalmomin da su."Baza ka mutu ba Ibrahim ciwo ba ya kisa."Mama ta ce cikin tausayin sa.
Juwairiya kuwa ta kasa magana sai kuka ganin gudan jinin na ta ƙanin ta tilo na cikin wani mawuyacin hali, ji take da ma ace ciwon a jikinta yake.Sun jima suna tsaye a kansa da

numfashin sa yake baraxanar ɗauke wa,hankalin su a tashe sai shafa masa ruwa suke yi suna kuka gunun ban tausayi.
Juwairiya ce ta miƙe ta na faɗin"Mama bai kama ta mu zuba mishi ido mu na kallon sa a cikin wannan halin ba,tunna Baba bai dawo ba zan fita na samo abin da za'a kaishi asibiti.Ta ce cikin kuka Mama ta kasa ce mata komai duk da ta na tunanin in da za ta samo kuɗin,amma har ta na shirin fita ba ce komai ba."Juwairiya na shiga uku!Ya sume."Ta ji muryar Mama cikin ƙaraji dai-dai lokacin da ta fice da ga gidan.

*Follow,read,comment,share.*

*SAKACINA KO HALIN MAZA?*

*RUBUTAWA:-*
*JAMILA LAWAL ZANGO*

*SADAUKARWA GA:-*

*SUMMY M NA'IGE*
_(Aminiya)_

*FIRST CLASS WRITER'S ASSO....*

*SHAFI NA BIYU*

Da sauri Juwairiya ta dawo ta rungumshi da hannunta ɗaya,ɗayan kuma ta na shafa mishi ruwa,  ajiyan zuciya ta sauke mai ƙarfi ganin ya buɗe ido,don hankalin su ya tashi maƙura gani suke kamar mutuwa zai yi ganin yadda idanunsa suka ƙakƙafe.
Juwariya ta miƙe ta na faɗin."Tun da  ya farfaɗo bari na je na naimo mishi magani."Miƙewa ta yi ba ta jira amsar da Mama zata ba ta ba ta fice da ga cikin gidan ta na sharar hawaye.
A hankali ta ƙarasa shiga cikin shagon na sa ganin yadda ya haɗe rai tun da ya hangeta ta na

tahowa,tamkar an aiko masa da mala'ikan mutuwa ya haɗe ransa babu wani walwala.Jikin ta ya yi sanyi sai ta tsaya a bakin ƙofar ta kasa mishi magana kuma ta ƙi ta tafi duk da kallon kora da hali yake mata.
"Lafiya ki ka yi min tsaye kofar shago kamar na saki ki?Ya faɗa ransa a ɓace"Don Allah ka taimake ni Bala kasan mai ya kawo ni a karo na biyu,wallahi suna cikin wani hali na rantse maka wannan karon zan naimi kuɗin ka na baka."Ta faɗa da muryar kuka fuskarta bayyane da damuwar halin da take ciki.
"Ni ina ruwana na gaji da baki bashi kuma ba kawo min kike ba,sannan na nuna miki hanyar da zaki bi mafi ɓulluwa kin nuna a'a wai ke ustaziya,to sai kije can amma ko maganin biyar ba zan baki ba."Tamkar zai kai mata duka yake magana ganin haka sai kawai ta juya,dan ta saka a ranta yau bazai bata ba.
"A'a Juwairiya tafiya zaki yi."Ya faɗa da sanyin murya ganin ta kama hanyar fita,sai kuma ya ƙara matso da fuskarsa gurin ta yace."Kin cika kafiya ki yadda ki amince ko sau ɗaya ne,Allah zan baki duk abinda kike so.Kin san ina son ki Juwairiya na san babu yadda za'ai na same ki,wannna dalilin ya sa nake so ki amince min kar soyayyata ta faɗi a banza."
Ƙarashe fita ta yi da ga shagon dan abin da yake so bazai samu ba.Mahaifiyarta kullum ta na mata nasihar ta tsare kanta da ga aikata zunubi mai girma wanda Allah yake fushi da wanda ya aikata,kuma ya yi hani ga bayinsa muminai na ƙwarai.
Gidan ƙawarta Mariya ta wuce ta same ta zaune akan tabarma a cikin falo ta na gugan kayan ta da dutsen guga na gawayi,sallama kawai ta yi ta zauna a kan tabarma ji take kamar zatai hauka."Juwairiya lafiya kike mai ya faru?"Mariya ta jera mata tambayoyin  da ta kasa ba ta amsa ba,sai ta janye hannunta da Mariya ta kama tare da share hawayen da ya gangaro mata. Mariya ta ƙarashe share mata sauran hawayen ji take ita ma kamar ta saka kuka,ta ɗago idanunta da suka kaɗa suka yi ja ganin ƙawar ta ta na kuka tace."Ki yi min magana Juwariya!Kin san ba na jure ganin ki a cikin wannan hali,abin da ya sa naƙi dawowa kin san halin Baba Sani na rasa yadda akai ya takurawa rayuwar ki baya son kowa ya raɓe ki,dan haushin koron da yake yi nake ji irin kullen da yake miki ko fa yaran sa baya yi mawa,lamarin sa akwai ayar tambaya ,dan ina tunanin akwai lauje cikin naɗi!"Ta ja fasali ta na kallon Juwairiya da kukan ta ya tsananta,tuna yadda ya tsane ta yake azabtar da rayuwarta.Mariya ta ci gaba da magana cikin ɓacin rai ta na cewa.
"Ina jin takaicin halin da kike ciki amma ki sani bawa bai isa ya canza ma wani rayuwar sa ba,kin ga da Baba Sani baya miki kulle sai na sama miki aikatau ni bashi nake yi ba hankalina kwance.
Juwairiya ta sauke ajiyar zuciya duk da baƙin cikin da take ji na ƙin barta ta yi aikatau,wanda mahaifinta ma ya amince amma ƙememe ya hana ta da ta na yi ƙila da basu shiga cikin uƙubar rayuwa ba,gashi tun da ta gama sakandiri ya hana ta karatu amma yaran sa duk sun yi.
Duk da lamarin na ci mata tuwo a ƙwarya amma ba ta ce ƙala ba,sai dai zuciyar ta cinkushe take da damuwa tare da tunani iri-iri.
Mikewa Mariya ta yi ta shiga kicin ta zuba tuwo da miyar kuɓewa ta kawo mata ta na faɗin."Gashi tun ɗazu na so na kawo muku amma ina tunanin wannan Baban naki,kuma Auwal tun da ya tafi islamiya bai dawo ba balle na bashi ya kawo miki."Ta miƙa mata tare da kwance ƙullin zaninta ta ciro naira ɗari biyu ta miƙa mata.
Tsabar murna sai kawai ta rungumeta tare da fashewa da kukan murna,Mariya na taimakon ta

ƙwarai ta na fatan Allah ya bata ta taimaka mata.
Rako ta ta yi ta siya magani sannan ta kaita dai-dai kwanar lungun gidansu.Da sauri Mariya ta saki hannunta ta na faɗin."Na shiga uku wallahi gashi nan duk da ƙin kaiki gida da na yi amma ya na nan ya na sa ido ya san ki fita,ke Juwairiya wannan ko mijin ki ne sai haka."Ta ruga da gudu har ta na tuntuɓe bayan ta gama maganar don Allah ya saka mata tsoron shi,bashi da mutunci in dai akan Juwairiya ne.
Juwairiya da jikinta ya fara rawa ji ta yi kamar ƙasa baza ta iya ɗaukar halintar ta ba,ta tsorata iya tsorata zabura ta yi kamar zata ruga sai kuma ta fasa ta na karanta wallahu galibun ala amrih ganin ya tunkaro ta.
Ya ƙaraso ya na mata wani irin kallo da shi kaɗai yasan ma'anarsa."Ina kika je?"Ya tambayeta da murya kakkausa tare da saka ƙafafunsa ya take mata 'yan yatsun kafar,ta rintse ido ta na jin wani iri madarar azaba ya na taso wa daga kan 'yan yatsun na ta ya na zagaye ilahirin jikinta,taso ta matsa domin akoda yaushe ya tsaya kusa da ita ta na ƙalubantar yadda yake matsowa daf da jikinta.Amma hakan ya ci tura ganin yadda ya take kafarta ya hana motsinta.
"Bana hana ki yawon maula da uwarki ta koya miki,bayan Yayana bai rage ku da komai ba."Ya faɗa ya na ƙara kusanci da ita fiye da na ɗazu.
"Don Allah kayi haƙuri bani ta yi wallahi ban roƙe ta ba,kuma Ibrahim zan bawa."Tace yayin da taƙi shaƙar numfashi ba ta son ta shaƙi iskar hucin bakin sa da take jin sa a fuskarta.Ya ɗa ga kafafun na ta ya na ƙare mata kallo hakan ya bata damar shirin arcewa ko takalminta bata ɗauka ba,dan ya zame lokacin da ya take ƙafarta.
Da gudu ta ruga amma sai ta faɗi ƙasa yayin da miyar tuwon ya zube,amma duk da zafin da take ji bai saka ta yadda tuwon ya zube ba,ta zabura ta miƙe hanyar gida dai dai sanda ta ji ya na faɗin."Ni da kene a duniyar na baza ki taɓa jin daɗi ba matuƙar ina raye,haka kawai na yi sakaci har tunanina ya faru mu zu ba mu gani
Juwairiya na shiga cikin ɗaki ta fashe da kuka mai tsuma zuciyar mai sauraro,a ranta ta na jin baƙin cikin halinsa bata san mai ta tsare mishi ba,amma ya saka ma rayuwarta ƙahon zuƙa.
Koda ta shigo Mama ba tace komai ba har ta sha kukanta ta ƙoshi don tasan mai ya faru,tunna babu abin da za ta iya shi yasa bata tanka mata ba,sai ta jawo kwanon tuwon ta ba Ibrahim sannan ta bashi magani ragowar taci ta ragewa Juwairiya duk da babu miya kuma ta ji ƙasa-ƙasa a tuwon.
Bayan ta gama kukan taji sanyi a zuciyar ta dama kukan shi ke sanyaya mata zuciya,duk lokacin da ya yi mata hakan don babu wanda yake ko tari a cikin iyayenta,su kansu tsoron sa suke yi duk da mahaifinta shine babba.
Miƙewa ta yi ta ɗauro alwala ta yi magariba sai ta yi zamanta ta na jan carbi yayin da hawaye ke zuba fuskarta,wani gefe na zuciyarta ta na hasaso mata lamura sosai game da Baba Sani.
Baba Sani ya yi tsaye a gurin bayan tafiyar ta ya na tunani sannan ya ƙarasa dakalin ƙofar gidan ya zauna ya na gadin masu zuwa gurinta,ko da ka kira sallar isha'i ya yi sannan ya dawo ƙofar gidan ya ci gaba da gadin gurin.
Sai misalin tara na dare mahaifin Juwairiya ya yi sallama ya shigo da ƙullin leda mai ɗauke da garin rogo gwangwani biyu da siga.Mama ce ta amsa sallamar ta ƙarbi ledan tare da shinfiɗa mashi tabarma,lokacin har baccin wahala ya fara ɗaukar ta don yunwa take ji matuƙa kuma kamar zazzaɓi yake son kama ta.
Jin sallamar ya sa ta buɗe idanu ganin leda a hannun Mama ya sa ta miƙe tare da ƙarban ledar

bayan ta yi mishi sannu da zuwa ta fice dan ta jiƙa garin.Ya kalli Ibrahim dake kwance ya na bacci ya shafa fuskarsa ya na faɗin." Ya jikinsa?Ina can amma hankalina ya na nan kin san jiya ƙafarsa ta bani tsoro."Yace ya na lasar bushashshen bakinsa dan rabon sa da abinci tun jiya da yamma da suka girka taliya leda ɗaya gashi ya wuni ya na faskare.
"Da sauki amma ya kama ta a maida shi asibiti gaskiya,yau ya bani tsoro ina ki kamar zan rasa Ibrahim saboda halin talaucin da muke ciki."Tace sai kuma ta rushe da kuka ta na fyace majina. A sanyaye Juwairiya ta ije garin da ta jiƙa ganin Mama ta na kuka ta koma gefe ta zauna ta na jin zafin Baba Sani dan ita gani take shi ya takurawa rayuwarsu da ya hana ta naimi aiki,in da ace ta na aiki rayuwar su ba ta yi muni haka ba,ga Mariya da take aikin suna jin daɗi kuma matar ta na taimaka musu.
"Ki bar kuka dan Allah da kin san halin da na wuni da kin tausaya min!Na dage tuƙuru ina faskare sai da na gama Malam Aminu yace bashi da kuɗi sai gobe,daƙyar na samu ya bani naira ɗari biyu wai shima kwana biyu ba cinikin iccen.
Shuru sukai cikin jimamin rayuwar su kowa ya na takaicin yadda suke tsotsan tsamiya,ganin Baba ya dawo Juwairiya ta miƙe tare da yi musu sai da safe ta tafi ɗakin da take kwana.
Washegari da safe misalin bakwai da rabi ta shafa addu'a,sannna ta miƙe ta nufi waje dan wanki zatai da aka kawo musu da safe kuma ana so anjima,murna sosai ta yi dan aka wo kuɗin wankin za su sami su yi girki.
Da sauri ta ƙarasa ta na faɗin."La Mama har kin fara."Bata ce mata komai ba sai botiki da ta miƙa mata ta ibo ruwa a randa.
Basu gama wankin ba har misalin tara da rabi bayan sun gama Juwairiya ta fita tayo musu cefanen taliya suka dafa da mai da yaji.Bayan ya dawo daga sallar asuba ya kwanta don ji yake ko ina na jikin sa ya na ciwo,bai tashi ba sai da aka gama girki shi ma sai da Juwairiya ta tashe shi,dan tasan yunwa ce ke damunsa.
Bayan yaci abincin ya miƙe tare da fita ya na son ya ga kanin nasa,akan maganar komawa da Ibrahim asibitin da kamar yadda likitocin suka faɗa.
Ya na ƙoƙarin shiga shashinsa suka yi kicibis saura kaɗan su yi karo,Baba Sani ya matsa ya na kallon ɗan'uwan nasa ya ce."Lafiya yaya baka da lafiya ne?Ji yadda ka koma kamar wanda ake iban shi ana miya."Yace da maganar shi ta izgilanci ya na karkaɗe jakar zuwa aikin shi,dariya kawai ya yi mai kama da yaƙe yace."A irin wannan rayuwar ka na sane da halin da nake ciki ni da iyalina,yanzu ko taimakon da kake yi min ka daina."Ya ƙarashe magana da takaicin yadda ɗan'uwan nasa ya daina taimaka mishi tun tsawon shekaru da irin butulcin da ya yi mishi. Hannun shi ya watsa ya kalleshi ya na kallon agogo."Sauri nake yi yaya kaga na yi latti kuma kasan yanayin aiki na,yi sauri ka faɗi abinda ke tafe da kai.Kuma da kake maganar ba na taimaka maka nauyi ne ya yi min yawa kowa ya ji da kansa."
"Haka ne Allah ya shige mana gaba,amma ya kama ta ka duba rayuwar Juwairiya kaga ni bani da shi da zan saka ta a makaranta,kuma kace ba aure zakai mata ba baka da ƙuɗin auren da ita."
"Haka na ce don ni yanzu ba ta aure nake ba,sabon gidana nake son na kammala.Ya bashi amsa a taƙaice sannan ya ɗora da ce wa."Kuma da kake maganar na saka ta a makaranta baka ga yadda take mara kamun kai ba can zata dinga watsewa da mutane,ka na sane da irin ƙorafin da nake maka a kanta ni nasan halinta da nake zaman gida."
Shuru ya yi ya na takaicin abinda ya faɗa ransa ya yi zafi,shi dai yasan kawai ya tsaneta ne

amma yasan wacece 'yarsa wani irin hali take dashi.
"Yaya na fa gaya maka aiki zan tafi amma ka tasa ni gaba kana ta wasiƙar jaki,ina sauri ne in kima baka da abin faɗe na tafi imna dawo saimu tattauna."Ya ce dashi ya na ƙoƙarin fita da sauri ya tare shi sannan ya ce."A kan maganar komawa da Ibrahim asibiti ne,kuma gashi bani da kuɗi dan Allah ka taimaka...."
"Haba yaya kasan fa bani da ƙuɗi nima hidima tayi min yawa kowa yaji da kansa,amma ga dubu ɗaya kuje Allah ya ba da lafiya."Ya miƙa mishi 'yan ɗari biyar guda biyu ya fice ya barshi a tsaye kamar sanda ya na tunanin butulci irin na ƙanin nasa.
A sanyaye ya shigo cikin sasan sa ya zauna akan turmi kamar babu laka a jikinsa,bai ce komai ba har zuwa wani lokaci sannan ya ja numfashi ya na kallon Mama dake ninke kayan da suka wanke har sun fara bushewa.
"Lailai ɗan adam butulu ne."Yace cikin raunanniyar murya sannna ya ɗora da cewa."Wai yau ni Sani yake wulaƙanta wa kan kuɗi ya manta yadda na wahala dashi dan ya sami ingantacciyar rayuwa.Mama ba tace mishi komai ba sai gyaran murya da ta yi,dan babu wani abu sabo a cikin halinsa duka sananne ne a gurinta.
Juwairiya na kwance bayan ta tashi ta yi sallar nafila ta yi addu'a ta koma ta kwanta,idanunta babu alamun bacci sai juyi take yi ganin haka sai kawai ta janyo carbi ta na ja,idanunta a rintse zuciyar ta na fatan samun maslaha a rayuwar su tunannin ta inda za'a sami kuɗi a mai shi asibiti,don likitocin suna tunanni aiki za'ai mishi a ƙafar.
Kawai sai ta ji ana ƙoƙarin buɗe ƙofar ɗakinta tsoro ya kama ta,tunawa da ta yi ta manta bata saka sakata ba da ta fita zuwa alwala.Tsananin tsoro ya kama ta ta rintse idanunta ta na tunani ta ya ya kai wani ya shigo cikon gidan su,dan Baba Sani ya gyara gidan kuma akwai ƙofa na masu kuɗi mai ƙarfi gidan.
Ba ta gama wannan tunanin ba ta ji mutum ya shigo ya nufi makwancinta,ta buɗe baki da nufin ta yi ƙara sai kawai taji an toshe mata baki da wata irin murya da nufin a ɓatar da tunanin mutum ga sanin mamallakin muryar aka ce."In kika yi ihu saina kashe ki?Ya faɗa tare da soka zungureriyar wuƙa dai dai cikinta,amma ta yadda bazai cutar da ita ba.
Wani irin tsoro da tashin hankali ya ziyar ce ta taji tamƙar numfashinta zai yi balaguro zuwa wata duniyar wacce take da banbanci  da wacce take rayuwa a cikinta."Da gaske abin da sautin amon kunnnuwana suke gaya min muryar Baba Sani take amo a cikin dodon kunnuwana?To mai ya shigo dashi cikin ɗakina a wannan sulusin daren?"Irin tarin tambayoyin da suke ta bijiro mata  a cikin zuciyar ta wacce ba ta samu ko da amsar ɗaya ba.
_Kar dai ku manta sunan labarin "SAKACINA KO HALIN MAZA" Mu haɗu a shafi na uku dan har yanzu shinfiɗa ne har  ba'a fara ba.Ga masu buƙatar shiga cikin group ɗina na whatsapp ga numba 08144072423_.

Kuma  ƙofa a buɗe take na ƙorafi gyara ko ƙarin bayani ga zakakuran marubuta,har yanzu ni mai koyo ce.
Kar dai ku man da wannan lintafin sadaukar wa ne ga zaƙauran marubuciya,kuma ƙawata (SUMAYYA NA'IGE) Allah ya ƙara fasaha ya sa ki fi haka,ina alfahari dake a cikin marubuta da irin taimakon da kike bani.

*FOLLOW, READ, COMMENT, SHARE*

Follow this link to join my WhatsApp group:
https://chat.whatsapp.com/LQfVU1ABdFI14btWRhUB1K

*SAKACINA KO HALIN MAZA?*

*RUBUTAWA:-*
*JAMILA LAWAL ZANGO*

*SADAUKARWA GA:-*

*SUMMY M NA'IGE*
_(Aminiya)_

*FIRST CLASS WRITER'S ASSO....*

*SHAFI NA BIYAR*

Juwairiya zaune a gefen Mama ta na yi mata kitso,Ibrahim ya na zaune a gefenta ya na wasa.Baba ya buɗe labulen ɗaki ya fito dai-dai lokacin da Baba Sani ya kwaɗa sallama daga nesa da su.Ganin sa Juwairiya ta zabura kamar za ta gudu,tun lokacin abin ya faru ta ƙara matuƙar tsoron shi ganin shi take kamar kumurci.

Baba Sani ya kalle ta da wani irin kallo wanda shi kaɗai ya san ma'anar sa,sannan ya miƙa ma Baba takadda yace."Gashi na gaji da biyan kuɗin wuta ni kaɗai,yau za su zo ka biya ko kuma a yanke na ka."Ya faɗa ya na kallon bangaren Juwairiya da ta rintse idanunta tun bayan da lamarin ya faru ta yi katanga da shi,ko ina ba ta zuwa islamiya ma ta haƙura gara ta din ga zama a gida da ta gan shi.

Baba ya yi kasaƙe ya na kallon sa na tsawon lokaci sannan yace."Ka sa su yanke nawa in dai baza ka iya biya ba,bani da shi kuma na ga ko waya babu wanda yake da shi a cikin mu hasken kawai muke amfani da shi."

" Oho ko ma me zaka ce kace na gaji da wahala."Ya sa kai ya fice ya na bambami.
" Ikon Allah na rasa me ke damun shi ya canza gabaki ɗaya.Allah ya ganar da shi."Yace sannan ya ɗauki gatarin sa ya fita.Juwairiya ta yi shiru ta na tunani a ranta zuwa can ta miƙe tare da shiga bayi ta saka kuka.

Mama ba tace komai ba illa baƙin cikin halin da yake nuna musu,wanda ta san tsananin ƙiyaryarta ya sa yake nuna musu hakan.Idanunta suka kawo ruwa amma sai ta yi ƙoƙarin sharewa,ba tare da Ibrahim ya gani ba.

Juwairiya ba ta fito ba sai da ta sha kukanta ta ƙoshi sannan ta wanke fuskarta ta fito,a ranta ita kaɗai ta san halin da zuciyarta take ciki.Duk da Mama ta gane kuka ta yi ba tace mata komai ba,domin ita ma da za ta samu dama kuka za ta yi ko zuciyarta ta rage raɗaɗin damuwar da take ciki.

Yanayin rayuwar da Juwairiya take ciki babu daɗi ji take kamar ta na rayuwa a gidan kurkuku!Kusan kullum sai ta yi kuka ta na matuƙar bakin cikin halin da iyayenta suke ciki,burinta bai wuce ace ta samu aiki ta na taimaka ma iyayenta ba.

Tsakanin ta da Baba Sani tun faruwar lamarin take jin wani tsanar sa mai tsanani ya na ƙara shiga cikin ranta,ko muryar shi ta ji sai ta yi ta'awizi a cikin ranta tsananin mamakin mugun halin sa take.

Duk yadda ta so ta taimaka wa iyayenta abin ya ci tura har takai su kwana basu ci ba,tashin hankalinta yadda Ibrahim yake yi,amma ƙiri-ƙiri Baba Sani ya hana matar sa basu abinci.

Ganin halin da suke ciki wani lokacin ta yi kuka kamar numfashin ta zai rabu da gangar jikinta.
Mahaifin Juwairiya na tsaye ya rataye gatarin sa a kafaɗa hankalinsa baya jikinsa,tunani yake sosai a cikin ransa ga wata irin yunwa dake ƙwaƙularsar.Tunani fal a cikin ransa ya na tunanin kuɗin aikin da za'a yi ma Ibrahim aiki a ƙafar sa.

Ya daɗe a tsaye ya na tunanin mafita daga bisani yaci gaba da saran iccen da yake yi cikin rashin kuzari,tare da rashin madafa sai tsaƙa da warwara yake a cikin zuciyar sa.

Ya ɗaga gatarin sa a sama ya na can ya na tunani bai ankara ba sai ji ya yi gatarin ya dawo tsakiyar kansa! "Innalillahi wa inna ilaihir ra ju'un."Iya abin da yace kenan ya zube a ƙasa a sume jini na ta zuba kamar famfo!

Hankalin Malam Audi dake gefen icce ya na bayar da iccen ya fahimci abin da ke faruwa, da sauri ya iso garesa ya na salati cikin tsananin razana tamkar zai fasa ihu ganin halin da yake cikin.
Mutanen dake gurin suka yo kansa suna salati ganin abin da ke faruwa,kama shi suka yi aka saka shi a cikin mota suka nufi a sibiti da shi.

Lokacin da labari ya riske Juwairiya hannunta saka a ka sai kuma ta yi ƙoƙarin daƙile zuciyar ta da take ninyar kwarma ihu,ta fara salati ta na faɗin."Inna lillahi wa inna ailaihir raji'un."Sai hawaye bayan ta yi nasarar faɗin haka ta yi koyi da faɗe na ubangiji da ya umurci bayin sa da su faɗi haka duk lokacin da wata musiba ta same su.

"Wayyo Allah rayuwa ta me ya sa daga wannan sai wannan?"Ta tambayi kanta cikin tsananin ruɗani.Gabaki ɗayan su sun ruɗe ganin halin da yake ciki kai ya kumbura kamannin sa ya canza,sannan an ɗaure kansa da bandeji duk ya ɓace da jini.

A lokacin da suka je ko magana baya yi idanunsa a rufe ba ya iya ko buɗe idanunsa,daga ganinsa ya na cikin wani hali babu alamun numfashi tare da shi sai bugun numfashin sa da yake sauka a hankali a cikin tsananin wahala.

Rintse idanunta ta yi a jikinta take jin kwatankwacin zafin ciwon dake jikin Baba,ta kasa kuka sai hawaye da yake gasar sauka a ƙuncinta ba tare da sanin ta ba.

Suna zaune har tsawon wani lokaci amma bai farka da ga baccin da yake ba,saboda allurar baccin da aka yi masa.Har misalin tara na dare sai a lokacin Baba Sani ya shigo ya na ta zare ido,a cewar sa yanzu ya dawo gida ya ji labari.

"Ni na rasa wannan lamari na ka Yaya kamar wani mai bakin uwa,kullum rayuwarka ƙara taɓarɓarewa take.Haba wannan wane irin musifa ne! Tun ba yau ba nake maka maganar kabar yin faskare amma kaƙi ga shi nan abin da ka jawa kanka."

Ire-iren kalaman da yake faɗi kenan ba tare da nuna tausayi a fuskarsa ba,sai dai nuna rashin damuwa da faɗin maganganu mara tsari.Juwairiya da ta kifa kanta da akan gadon asibitin ta na wani irin kuka.

Hankalin su ya yi matuƙar tashi ganin halin da yake ciki,Juwairiya kamar ta mutu haka take ji,ƙiri-ƙiri in aka buƙaci kuɗi Baba Sani yake ƙin bayar ba kullum da uzurin sa da yake faɗi.

Da ga baya Baba Sani yake zuwa ya na kwana da Baba.Baba Sani tsaye akan Yayan na sa da misalin ƙarfe ɗaya na dare,kallon sa yake da mugun nufi a ransa.Filo ya janyo tare da danne masa kai.

Allah Sarki bawon Allah da yake kwance a cikin mawuyacin hali ya fara mutsu- mutsu da ƙafafun sa,bai jima ba ya yi dip alamun babu numfashi a jikinsa.

" Gara ka mutu kowa ya huta kullum cikin wahala nake da kai da iyalan ka,sannan ɗan buƙata ta da nake son na biya na rasa.Kaje kawai Allah ya haɗa mu a kiyama!Abin da yace kenan ya kwanta da ninyar da safe ya fasa ihun ya mutu.

Washegari da safe Juwairiya tun da asuba take azalzala wa Mama da su je asibiti,irin mugayen mafarkin da take yi akan mahaifinta ya sa hankalinta ya tashi sosai.Mama ce ta ɗan ƙarfafata har suka dama koko suka sha,duk da dai Juwairiya ƙurɓar kokon take wanda ko siga babu hankalinta na gurin mahaifinta.

Ko wanka ba ta yi ba ta ɗauki ruwan kokon ta na addu'ar Allah ya sa ya iya sha,Mama dai ba tace mata komai ba duk da ranta babu daɗi.Ko da suka isa asibitin gaban Juwairiya ya yanke ya faɗi ras!Sai ta kira sunan Allah ta riƙe kofin kokon ta na wani irin tafiya zuwa ɗakin da yake tamkar wacce ƙwai ya fashe mata a ciki.

Gabaki ɗayan su suka yi mutuwar tsaye ganin Baba Sani tsaye, a ɗakin ya ɗora hannu a kansa ya na ƙwala ihu, da kuruwa tamkar yadda jahilan farko suke yi yayin da wata musiba ta afkawa ɗayan su.

Sautin kukan sa yake tafiya tare da bugun zuciyarta,ta rintse idanunta ta na addu'ar kar Allah ya sa mafarkinta ya zama gaskiya!In kuma da gaske ne ya za suyi da rayuwar su a duniya bayan ba mahaifin su?

Sai kawai ta fara ja da baya ta na girgiza kanta tare da nuna mahaifinta, ta na faɗin dai-dai lokacin da Mama ta saka kuka domin ta tabbata ya riga mu gidan gaskiya."A'a bai rasu ba wallahi mafarki ne!Don Allah kar kuce min mafarkina ya zama gaskiya.Mahaifina ya na raye bai mutu ba."

Sai ta ruga za ta fita waje tashin hankalin ta ta ya ya mahaifinta zai mutu ya bar ta da azzalimi!Mutuwar sa na nufin ya yi nasara akan ta zai cika mummunan nufin sa kenan?

Kar dai ku manta sunan labarin "SAKACINA KO HALIN MAZA" Mu haɗu a shafi na shidda dan har yanzu shinfiɗa ne har  ba'a fara ba.Ga masu buƙatar shiga cikin group ɗina na whatsapp ga numba 08144072423_.

Kuma  ƙofa a buɗe take na ƙorafi gyara ko ƙarin bayani ga zakakuran marubuta,har yanzu ni mai koyo ce.
Kar dai ku manta da wannan lintafin sadaukar wa ne ga zaƙauran marubuciya,kuma ƙawata (SUMAYYA NA'IGE) Allah ya ƙara fasaha ya sa ki fi haka,ina alfahari dake a cikin marubuta da irin taimakon da kike bani.

*FOLLOW, READ, COMMENT, SHARE*

*SAKACINA KO HALIN MAZA?*

*RUBUTAWA:-*
*JAMILA LAWAL ZANGO*

*SADAUKARWA GA:-*

*SUMMY M NA'IGE*
_(Aminiya)_

*FIRST CLASS WRITER'S ASSO....*

*SHAFI NA SHIDDA*

Duk yadda Juwairiya ta so ta kwantar da hankalinta akan mutuwar mahaifinta, abin ya ci tura!Da ta tuna mugun nufin Baba Sani sai ta ƙara rikicewa,irin yadda ta nuna na rashin tawakkali ya so ya fara tunzura Mama tun ta na ba ta haƙuri, ta taushe tashin hankalinta domin Juwairiya ta natsu amma ta kasa,sai uhu take ta na furta sunan Baba.

Ganin irin abin da take yi sai Mama ranta ya ɓace matuƙa,ta saki hannun Juwairiya dake son a kyaleta ta fita da gudu kamar wata kamun aljanu tace."Ku kyaleta ta yi duk abin da ta ga dama,ban san baki da tawakkali ba sai yanzu Juwairiya!Na ɗauka saboda ƙarfin imanin ki ni zaki din ga ba ma haƙuri,tare da jawo min aya akan na ɗauki haƙuri domin duk mai rai mamaci ne."

Juwairiya ta duƙa tare da ƙara sakin wani kuka dai-dai lokacin da Baba Sani ya ƙaraso gun ta ya na mata wani kallo,mai kama da tausayi ko akasin haka tare da sausauta murya yace."Ku kyaleta rashin mahaifi abu ne mai ciwo na tausaya miki matuƙa,domin hakan da kika yi sai kika tuna min lokacin da mahaifin mu ya mutu ina kuka mahaifinki Yaya Ahmed shi ya dinga lallashina!"

Sai ya saka kuka ya na faɗin."Allah Sarki!Allah ya jiƙan ka Yaya."Ya nufo Juwairiya dake kuka tamkar ranta zai fita,da nufin zai riƙe ta ya lallasheta.

Da sauri ta matsa ta na wani irin kuka kamar za ta shiɗe,ja da baya take kamar ta ga dodo.Ganin haka sai ya kyaleta a ran sa kuwa murmushin mugunta yake mata.Bayan an gama cuku-cuku aka ba su gawar Baba da har ta fara sandarewa.

Hankalin Juwairiya bai ƙara tashi ba sai da suka dawo gida ta ga inda yake kwanciya,wani ƙarin abin tausayi tun da Ibrahim ya ji mutuwar mahaifinsa ya ɗauke numfashi ko motsi ba ya yi.Lamarin sai ya jagule ma Mama ta rasa in da za ta sa kanta ta ji sanyi,ga wani irin kuka da Juwairiya take yi taƙi ta yi shiru.

Bayan an yi wa Baba sallah aka kai shi gidan gaskiya gidan da ko wane bawa yake da gadon sa domin ba'a wahala gurin mallakar sa.Cikin dare Juwairiya ta na kwance ta kasa bacci!A ranta ji take kamar mahaifinta kashe shi aka yi musamman yadda ta ga Baba Sani bai nuna tashin hankali game da mutuwar sa ba.

Ta na lura da shi har shinkafa ya siyo a dafa ma ƴan zaman makoki,wanda ko mutuwa za su yi ba zai taimaka musu da shi ba.

Kwana ishirin da rasuwar Baba amma har yau sun kasa manta shi a kullum ta ranar duniya sai sun yi kukan rashin sa,musamman Juwairiya da yake sokanar ta duk san da zai fita ya na cewa Allah ya nuna mi shi ranar auren ta,a she ba shi da rabon gani.

A lokacin da Baba ya yi arba'in Juwairiya ta saka ma ran ta za ta yi fito na fito da Baba Sani duk abin da ya shirya a shirye take ita ma.Tun lokacin  da Baba ya rasu bai ƙara shiga sabgar ta ba,duk da cewar ba ganin ta yake ba don ba ta fita ko ina.

Ganin ba su da cin yau bare na gobe sannan Mama ita ma kwana biyu ba lafiya take da shi ba,ya sa za ta gaya ma Mariya ta nema mata aiki ta din ga yi don da yunwa ya kashe ta gara dukan Baba Sani ya kasheta ita kaɗai.Ta san ya na hana su abinci ne don kawai ya cutar da rayuwar su ko ya samu biyan buƙatar sa,amma ba wai don ba shi da kuɗi ba tunna aikin gwannati yake yi.

Ranar da Baba ya yi arba'in sun sha kuka bayan sun yi mishi saukar alkur'ani suka haƙura da kukan suna mishi addu'ar Allah ya jiƙan shi.

Cikin sa'a bayan kwana biyu da gaya ma Mariya ta nema mata aikatau,ta zo da murnar ta an samu saboda ta na samun aikatau da dama kusan ita dillaliyar masu aiki ne.

Tafiyar da Baba Sani ya yi sai hakan ya ba Juwairiya damar ta fara aikin ta cikin kwanciyar hankali ba tare da kowa ya sani ba.Duk da ita Mama taso ta bari ya dawo su tambaye shi amatsayin sa na mahaifi,amma taƙi ta kafe daga karke wasu irin maganganu ta jefa ma Mama wanda yasa ta ji babu daɗi,a yadda take gaya mishi magana duk da ta san dama ba sa shiri,amma ko ba komai yanzu shi yake da matsayin mahaifinta kuma ko aure za ta yi shi yake da alhakin komai.

Faɗa sosai ta yi mata don ganin ta a maganganunta har da rashin kunya,wanda hakan bai dace ba musamman shi da yake da matsayi mai girma a ranta.Juwairiya ta ji maganganunta amma

yadda ta faɗe su haka ta watsar da su a gurin a ranta take faɗin."Ta ya ya za'ai na mutunta mutumim da yake da burin ɓata min rayuwa,ko da mahaifina ne ya bijiro da wannan iyakan abin da zai yi mishi kenan Mama,domin babu biyayya ga abokin sabon halitta!Kema da zaki ji abin da yake so a gareni sai kin yi mishi fiye da nawa."

Matar da Juwairya za ta yi ma aiki likita ce a shika ta na da yara uku,a kwai wata mace tsohuwa wacce take mata girki ita kuma Juwairiya aikin ta kula da yaranta mata biyu da namiji ɗaya,in da za ta din ga mata aiki ta na tafiya har islamiya ta saka su tare da yaranta.Ranar da kuma take da aikin kwana za ta kwana da yaranta da safe ta shirya su ta tafi makaranta,wanda ta ba ta zaɓi in ta gama shirya su za ta tafi gida duk da ita matar makaranta ta ba Juwairiya zaɓi ta koma ta zana jarrabawar fita sakandiri.

Juwairiya ta ji matuƙar daɗi na samun aikin duk da ta na jin tsoron abin da Baba Sani zai yi mata in ya fahimci ta na aikin.Taƙi amince mata kan shawarar da ta ba ta da ta koma makaranta,duk da ita ma ta na da buƙatar haka amma ta san Baba Sani ba zai bar ta ba.

Sai dai cewar da matar ta yi za ta dinga kwana da yaranta in ta na aiki ya so ya ɗan tsorata ta,amma da ta gaya mata a kwai Baba tsohuwa sai hankalinta ya kwanta don ta yi tunanin tare za su din ga kwana.

Juwairiya ta ƙara son ta yi aikin jin an ambaci kuɗi mai tsoka,sannan da suka tashi za su tafi sai ta ba ta kayan abinci da kuɗi naira dubu ta sallami Mariya da tsoka,saboda ta yaba da hankalinta musammam da ta ganta ba ta da ƙazanta.

Mama da ta ji aikin har da kwana sai ta fara yiwa Juwairiya faɗa kuma tace sam ba za ta yi aikin ba,ta na ta faɗa in da take shiga ba nan take fita ba.Ganin hakan sai ta saka kuka ta miƙe domin ta yi sallar magariba."Ba gara na zauna a gidan Anty Naja ba tunna na ji Mariya tace mijinta ustazi ne me gamu,akan ƙanin mahaifina dake son ya ɓata min rayuwa.

Juwairiya ta yi tunanin za ta shawo hankalin Mama,amma sai ta ga ta kafe a dokin naƙi in da ta ƙara mata da cewar sam ata fau ba za ta yi aikin ba.

A ranar da suka shirya da Anty Naja za ta fara aikin,Mama ta kafe ko da Mariya tazo suka lallashi Mama shi ma bai yi wani tasiri ba ganin haka sai ta haƙura,akan ta nema mata wani kawai wanda ba za'a din ga kwana ba.

Da maraice ta na zaune akan kujera ta na wanke-wanke sai suka ji sallamar Mariya da wata a bayan ta,da sauri ta ɗaga kanta  duk da cewar ba ta yi ma Anty Naja kallon kirki a ranar ba,amma ta sheda ta.

A kunyace ta amsa mata sallama tare da yi mata jagora zuwa ɗaki,ta ibo mata ruwa a kofi ta ije mata sannan  ta fice daga ɗakin ta na jan numfashi ta riƙe turaren Anty Naja da ya baɗe ɗakin na su,wanda Juwairiya ta so ya dauwama a ɗakin saboda daddaɗar ƙamshin sa.

"Ba ki sanni ba ko Mama?"Anty Naja tace bayan ta ɗauki ruwan da Juwairiya ta kawo mata cikin sakin fuska,kuma ta sha ruwan sosai ba tare da nuna ƙyanƙyani ko tafi ƙarfin shan ruwan randa,wanda hakan sai ya yi matuƙar burge Mama wani ƙarin burgewa ta baje akan tabarma har ta na cire hijabin ta da ɗankwalinta.

Hakan ya yi matuƙar ƙara burge Mama sai ta ƙara jin ta saki jiki da ita tace."Bam ma sanki ba yarinya,amma da na ganki da Mariya ƴar maƙocin mu na gane kece wacce aka yi maganar aiki da Juwairiya..."

"Ni ce Mama tabbas ni ce ina ta jiran ta ba ta zo ba,sai da ga ba ya Mariya ta zo tace min kin hana ta "Tace tare da ƙatse Mama ba tare da ta kai aya ba.
"Haka ne gaskiya aikin nan ki nemi wata kawai."Mama tace ta ɗan canza fuska kaɗan,ganin haka sai jikin Anty Naja ya yi sanyi amma saboda ya ba hankalin da ta yi na Juwairiya ta kasa haƙuri tace."Don Allah Mama karki hana ta wallahi ba ni da matsala da ga ni har mijina,kuma in kina tunanin kwanan da za ta yi ne mijina ba zama yake ba wani lokacin ni kai na sai na yi bacci yake dawowa."

Ta matsa kusa da Mama tare da riƙe hannunta ta yi rau-rau tace."Don Allah Mama kar kice a'a ban ɗauki Juwairiya a matsayin me aiki ba ƙanwa ce a gareni,kuma duk ranar da kika ga wani abu ya faru mara daɗi a tsakanin mu ki hana ta zuwa."

Ta yi shiru ko Mama za ta ce wani abu amma sai ta ga ta kauda kanta ta na tunanin wanda ba za ta iya cewa ta yanke ta barta ko a'a."Kin ji Mama ki amince don Allah!Na yi masu aiki da dama amma basa iya riƙe min amana,bayan haka sace-sace suke min."

Duk maganganun da take yi ba ta ce mata komai ba,aranta ta na tunanin karta amince a za a sami matsala da Baba Sani duk da shi ma ya na da laifi,in da ace ya na taimaka musu da ba za ta yi aiki ba.
'Ki na ji Mama da ban so na gaya miki wani sirrina ba,amma nuna amincewar ki ya zama dole na sanar miki domin ki taimakeni ki ceci aurena.Mai aikina mijina ya kama ta da yarana tana basu kirjinta suna tsotsa ita kuma ta na saka musu hannu a gabansu.Hankalinsa ya tashi ƙwarai ba yan ya miƙa ta ga hukuma ya kawo su asibitin da nake aiki,hankalina ya tashi ƙwarai na yi kuka kuma mun yi rikici da shi daga ba ya yace dole na bar aiki ko mu rabu.Ina son aikina saboda da shi nake taimaka iyayena,sannan ina son aurena na yi-na yi a dai na saka ni aikin kwana amma ba zai yiwu ba.

Mijina ya bani zaɓin na bar aiki na kula mishi da yaransa ko ya rabu da ni,domin yaƙi barin na ƙara ɗaukar me aiki.Mun yi rikici da shi sosai daga baya ya haƙura na samu mai aiki amma daga wannan ya kama ta da wani matsala zai rabu da ni."Tace cikin hawaye ta ja numfashi sannan ta ɗora da cewa.

"Mariya ita ta ja ra'ayina akan Juwairiya saboda ta gaya min ta na da hankali,da ƙyar na amince

da na ganta na yadda da maganar Mariya ki taimake ni Mama in har kika amince zan zama tamkar ƴarki,zan taimaka ma rayuwar ku."

Jikin Mama ya yi sanyi sosai har ba ta san sanda ta amince ba jin aure na shirin mutuwa,duk da watarana ita ma aure za ta yi."Na amince Allah ya kyuata amma ƴar nan ya kamata ku din ga kiyaye wa,ni ma matsalar ba daga gareni ba ne a kwai ƙanin mahaifinta ba lai-lai ba ne ya amince amma ta fara mu gani."

Sosai ta ji daɗi ta buɗe jakarta ta ciro dubu ishirin da biyar tace."Ga kuɗin ta na wata biyu dubu ishirin sai ki fara koda sana'a ne,sannan dubu biyar na baki kyauta kuma gobe in Allah ya sa tazo za ta taho da tsaƙo."

Mama ta ji daɗin kuɗin da ta bata ta na ta murna da saka mata albarka har ta yi mata sallama,ta kama hannun Juwairiya tace."Sis sai kin zo gobe ko?Don Allah ki zo da wuri ƙanninki suna ta maganarki."Tace tare da shafa kanta.
"Gaskiya ta na da kirki sosai."Mama tace ta na juya kuɗin da ta bata,sai kuma ta aje kuɗin ta kalleta tace "Kin san me ba zan taɓa kuɗin nan ba sai mun ji me Baban ku Sani zai ce."Da sauri ta miƙe kawai ta na faɗin."Ki ba ni naje na yo miki sare-sare ki fara sana'a ni fa ko me zai yi sana yi aikin nan,tunna shi ba taimakon mu yake yi ba don haka ba shi hurumin da zai hana mu."

Ta yi maza ta fice daga ɗakin kafin Mama tace komai sam ba ta jin tsoron abin da zai ce in dai ba kasheta zai yi ba ta rantse sai ta yi aikin.

Kamar yadda ta gaya mata mijinta ba mazauni bane haka kuwa ta gani,don tun da ta fara aiki ba ta gan shi ba sai tanƙamemen hoton su da yake manne a falon wanda tun da taje ranar da Mariya ta kaita ta gan shi a hoto,wannan dalilin ya sa hankalin ta ya kwanta ko da ta ga Baba me aiki aikin ta take yi ta tafi ba ta kwana.

Ta na aikin ta cikin kwanciyar hankali ga abinci da take ci kullum taci mai kyau ta sha mai kyau,don Anty Naja ba ta da rowa ko nama taci sai ta rage mata saboda yadda Juwairiya take kula da yaranta ga ta da tsafta ko ina na gidanta tsaf ya na tashin ƙamshi.

Kusan sati biyu ta na aiki cikin jin daɗi kuma har zuwa wannan lokacin Baba Sani be dawo ba,kullum in dai za ta dawo Anty Naja na sawa a yi girki da su ta saka mata a kula kuma da yawa,don haka ba sa matsalar abinci ga ɗanye da take badawa a  kai ma Mama in dai za ta yi aikin kwana.

Ranar Juma'a da safe bayan ta gama aikin ta ta shirya musu abincin karyawa ta ibi nasu kamar yadda ta yi mata umurni,kasancewar ta gama aikin kwana za ta yi hutu har ta bawa Juwairiya hutun kwana biyu.

A hanya Juwariya ta na tafe ta na ta yi mata addu'a don tsakanin su Allah ne kawai zai biya

ta,saboda irin kyautata mata da take yi fara aikin ta ta bata kaya masu kyau sosai da abin alheri ko hijabi kala biyar ta bata,sannan ko baƙi ta yi bata ce mata me aiki sai dai tace ƴar'uwanta ta na da matuƙar kirki sam bata nuna wani abu ko rashin mutunci.

A dai-dai ƙofar gidan su ta tsaya cikin firgici ganin Baba Sani ya ɗare kan motar sa ya na riƙe da ƙatuwar bulala,sai juya ta yake ya na zare ido ransa a ɓace da ga ganin yadda ya ɗaure fuska alamun ba mutunci.

Kar dai ku manta sunan labarin "SAKACINA KO HALIN MAZA" Mu haɗu a shafi na bakwai.Ga masu buƙatar shiga cikin group ɗina na whatsapp ga numba 08144072423_.

Kuma ƙofa a buɗe take na ƙorafi gyara ko ƙarin bayani ga zakakuran marubuta,har yanzu ni mai koyo ce.
Kar dai ku manta da wannan lintafin sadaukar wa ne ga zaƙauran marubuciya,kuma ƙawata (SUMAYYA NA'IGE)

Allah ya ƙara fasaha ya sa ki fi haka,ina alfahari dake a cikin marubuta da irin taimakon da kike bani.

*FOLLOW, READ, COMMENT, SHARE*

Follow this link to join my WhatsApp group:
https://chat.whatsapp.com/LQfVU1ABdFI14btWRhUB1K

SAKACINA KO HALIN MAZA?*

*RUBUTAWA:-*

*JAMILA LAWAL ZANGO*

*SADAUKARWA GA:-*

*SUMMY M NA'IGE*
_(Aminiya)_

*FIRST CLASS WRITER'S ASSO....*

*SHAFI NA BAKWAI*

Tsananin mamaki ya kama shi ganin yadda Juwairiya ta gan shi amma sai ta yi tsaye ta na kallon shi, ba tare da nuna wani tashin hankali a fuskar ta ba ko tsoro.

Ya ɗan ƙare mata kallo cikin mugun nufin sa amma sai ya ga duk da ramar da ta yi,ta ƙara mishi kyau ɗan tafiyar da ya yi.

Juwairiya da tsaya ko zai ce wani abu amma ganin ya yi shiru,ya sa ta nufi hanyar shiga ƙofar gida za ta shige.Da dauri ya sha gaban ta a ransa ya na mamakin dai na tsoron shi da ta yi,tun ranar da ya nemi haɗa jiki da ita.
"Da ga gidan uban wa kike?"
Ya tambayeta da fuskar shanu y na zare mata idanunsa da suka kaɗa suka yi ja,saboda tsabar fitina da ya saka ma kansa.Ta ɗan ja ta tsaya tare da matsawa nesa da shi ganin yadda ya matso daf da ita.

"Ba na hanaki yawon maula ba,shi ne don kin ga ba na nan kika mai da shi sana'ar ki?"Ya tambayeta tamkar zai kai mata bugu.

"Ni ba maula naje yi ba,aikatau na samu nake yi domin na ciyar da kammu."Ta faɗa mishi ba tare da jin tsoro ko shakku a ranta ba.

Wani irin azababben mari ya wanka mata wanda ya sa ta yi taga-taga za ta faɗi,amma ta dake duk da azabar da ta ji kamar za tai fitsari a tsaye sai ba ta nuna mishi ba,don a shirye take ta shirya tsaf!Ko kasheta zai yi.

Matuƙar mamaki ya kama shi wai yaushe ya yi sake har ta raina shi haka,amma sai ya ƙara ɗaure fuska yace."Na ga kwana biyu kin raina ni Juwairiya saboda na nuna miki manufa ta a kanki,to wallahi har yanzu ina kan baka na saina cika muradina gara ma ki amince ki sami maslaha a rayuwarki."
A wannan lokacin ta ji wasu tagwayen hawaye sun cika mata fuska,zuciyarta ta amince da

lai-lai shi ba mutum bane don ta yi tunanin rasuwar mahaifinta zai saka ya haƙura da ƙudirin sa.

"Ka sani ko mutuwa zan yi ba zan lamunce ka biya buƙatar ka a kaina ba!Ina matuƙar kaico a rayuwata da ka fito a matsayin ƙanin mahaifina.Ko mutuwa zan yi sai dai na mutu."Tace mishi ta na ƙoƙarin shigewa gida.

Sororo ya yi lai-lai ya yi sake tunna har taga wallar shi ta na faɗa mishi mugayen kalamai,masu tsauri a cikin idanunsa ba tare da shakku ko shakkar sa ba.

"Tun da kika ce haka mu zuba ni dake,bari na tuna miki akan ki zan iya komai tun da kika girma na ɗora kwaɗayina akanki Ki kuka da kanki zan iya komai don na cimma manufata."

Ta buɗe baki za ta yi magana wani irin takaici ya toƙare mata maƙogaro,sai hawaye da suka fara turereniya a fuskarta da ta tuna ƙanin mahaifinta yake mata wannnan halin,sai ta ruga a guje ta shige cikin gida ta na kuka.

Mama dake ƙoƙarin hura wuta a murhun gawayi idanunta duk sun yi ja, suna zubar hawaye saboda wutar taƙi kamawa sai saka leda take yi.Sai ganin ta ta yi ta shigo da kuka ta shige cikin ɗaki ta buɗe baki da nufin ta yi magana,duk da cewa ta san dalilin kukan saboda ta ji dirin motar sa sanda ya dawo sai kuma ga shi ya shigo.

"Saboda ba na nan shi yasa kika saka ta ta na yawon maula ta samo muku abinci ko?Na rasa wani hali kike so ki koya mata shi yasa na tsaneki saboda mugun halinki."
Ta yi shiru ba tace komai ba dama ɗabi'ar ta kenan duk sanda zai yi mata rashin mutunci ba za ta tanka ba,haka ma yanzu mutuwar Yayan sa bai saka ta canza ba.
Har ya gama bambamin sa ya fice bata ce ƙala ba,amma ta na jin gara su haƙura kawai da tashin hankalin da zai jawo musu.Bayan ta gama kukan ta ta share kamar kullum don Mama ba za ta taɓa lallashinta ba.

"Juwairiya ina ganin a haƙura da aikin nan kawai."Tace cikin ƙunar zuciya ta na kallon ta."Gaskiya Mama sai dai kiyi haƙuri,amma ba zan haƙura tunna shi ba taimaka ma na yake ba."

"Amma kina ganin tijarar da yake mana ko?Kin san halin shi ba shi da kirki,ni fa bana son tashin hankali ya dinga jibgar ki a banza."
Juwairiya shiru kawai ta yi a ranta ta saka komai zai faru sai dai ya faru,amma aikin Anty Naja yanzu ta fara.Hankalin Mama ya tashi da safen ranar da ta gama hutun ta bayan Juwairiya ta yi sallah ta tafi aikin ta,ba ta kula da kiran da Mama take ƙwala mata ba.

Da yamma da ta dawo Baba Sani ya shigo da bulalarsa ya yi mata duka,har bata iya tashi amma ba hana washegari ta koma aikin ta ba.Ganin irin dukan da yake mata Mama ta hana ta aikin,sai dai wannan karan ta bijire ma umurnin ta don ta rantse ko kashe ta zai yi ba za ta bar aikin ba.

Tsakanin ta da mijin Anty Naja ba ruwanta da shi tun da ta fara aikin so uku ta gan shi,duk sanda ya shigo ya ga yaran a kusa da ita sai ya fara musu faɗa ya kora su cikin ɗaki ya na harararta ya na mazurai,a yadda yake mata ta lura ya matuƙar tsorata da halin masu aiki.

Ganin haka ta ƙara kame kanta ta na mamakin yaran duk da suna zuwa islamiya amma ba su wani iya karatu ba,don ko babban dake da shekaru tara ko alhamdu bai iya cikakka bare ya damu da sallah ba,sai kallon catoon da suke yi kullum ba ƙauƙautawa,ganin haka ta dage da koya musu da saka su su yi salla,abin da ya ƙara saka Anty Naja son ta a cikin zuciyar ta.

Ganin ƴan canjin da yaransa suke samu abin ya burge shi har yake amsa gaisuwar ta a sake,wani lokacin har kyauta yake mata na kuɗi yace ta kaiwa mahaifiyarta don Anty Naja ta gaya mishi mahaifinta ya mutu.

Kusan kullum Juwairiya ta dawo sai taci na jaki a gurin Baba Sani jikin ta duk shatin duka ne,amma hakan bai saka ta karaya ba ta ci gaba da aiki don yanzu suna ci ga Mama dake sana'ar ta rayuwar su ta na tafiya cikin rufin asirin Allah sai dai takurawar da Baba Sani yake mata,wanda hakan ya na damin Mama ga shi taƙi ta dai na aikin.
A haka rayuwa take gara musu yau fari gobe tsumma,yayin da kullum burin Baba Sani ya cika burinsa amma Allah bai ba shi damar ida mugun nufin sa a kanta ba.Ganin haka sai ya ɓullo mata da nuna mata kuɗi ya na jan ra'ayin ta akan ta amince mishi ko sau ɗaya ne,amma taƙi duk ta gan shi sai ta nemi tsari da sharrin sa don ganin sa take kamar wani sheɗani.

Ta ɗauki tsawon shekaru biyu ta na aiki a gidan Anty Naja,a lokacin ta girma ta ƙara wayewa ga hankali da natsuwa kullum cikin hijabi take bata cirewa sai in mutanen gidan ba sa nan,ko ita Anty Naja ba za ta ce ga yanayin jikin ta ba,don tun kafin takai haka da Baba Sani ya saka mata ido ta yi tunanin ko jikinta yake ruɗarsa,bare yaanzu da ta zama ƴan mata ta cika ta batse ga Anty Naja da take ba ta kaya masu kyau kuma ta ba cin me kyau,har mai na shafawa da na wanke kai take siyar mata.
Maza da dama sun sha bayyana soyaryarsu gurin ta wasu kuma suje gurin Baba Sani,amma sai ya taƙarƙare yace Juwairiya ƴar mace ce sannan ba ta da kamun kai har kwana take a waje.Ya faɗi mugun abu da ba ta mata suna ya gaya musu,wasu suna jin haka za su tafi wasu in suka nace ya yi musu korar kare don ya rantse,in har ba ta amince mishi ba to ita da aure sai dai ta ga ana yi ko kuma in ya mutu.

Juwariya yarinya mai kimanin shekaru sha tara.Ta na da haske amma ba can ba,fuskarta mai kyau irin zagayayen fuska gareta,da dogon hancin ta haƙoran ta masu kyau ga ƴar wushiryar ta a tsakiya,wanda in ta yi dariya yake ƙara ma kyau matuƙa!Da dimful ɗinta.Bata da jiki amma a kwai shafe sannan  doguwa ce ba can ba,amma ta na da tsawo wanda yake ƙara mata kyau.

Ƙirar jikinta me kyau ne ko ita ta na alfahari da hakan wato irin jikin nan ne mai ɗaukar hankali waɗanda ko wane namiji yake burin samu mace mai irin sa.Wannan dalilin ya sa kullum take cikin hijabi do ko ƙawayenta suka shigo suka gan ta ba hijabi,sai su yi ta zuzuta ta su na yaba

kyawun jikinta.

A wata ranar  Iitinin da safe bayan mutanen gidan sun gama karyawa suka wuce gun aiki,kasancewar da garin a kwai zafi sannan Anty Naja ta tura mata da tsako a cikin wayarta me botira da ta siyar mata,don ta din ga kiran ta ko kuma in ta tafi aiki da wuri ta gaya mata abin da za ayi,don yanzu girkin su ya dawo hannunta saboda Baban Abnaj yafi son girkinta.
Waina da miyan karas za'a yi da farfesun rago,ganin ta na da aiki ya sa ta zage damtse ta na yi tun ta na cikin hijabi har ta cire ta na ta aikin ta,ta kunna wayarta ta na sauraron karatun kur'ani cikin suratul ma'ida.Ta shafa'a ta na ta aikin ta sai ƙanwar Abnaj mai suna Ibtihal ta danna remote ta ɓata saitin tibin,Abnaj ɗan shagwaba ya saka kuka ya zo ya na sanar da Juwairiya akan ta zo ta gyara musu.

Hannunsa ta kama suka nufi falon da nufin ta gyara mishi,ta na tsaye a gaban tibi ta na ta ƙoƙarin yadda za ta gyara amma ta kasa gashi ita ba ta san yadda ake yi ba,sannan gashi har sun fara kuka akan a gyara musu.
A hankali ya buɗe ƙofar ya shigo da sallama a bakinsa,Juwairiya da hankalin ta ke kan tibi ba ta san ya shigo ba,ko in ce dukan su sai bayan ya ɗauki tsawon lokaci ya na kallonta cikin mamaki a ransa ya na mamakin dama a kwai wannan halittar a gidan sa?Don shi zai rantse bai taɓa mata kallo ko na sakan bane ya san dai ta na da kyau a fuska.

"Oyoyo Daddy!"Abin da yaran suka ce kenan wanda ya ɗauki hankalinta ta miƙe a razane ta yi diri-diri,tamkar za ta shige cikin ƙasa yayin da wani irin kunya ya lulluɓeta.
Ganin yadda ta diririce sai ya shige ɗakin sa akan ya ɗauko abin da ya saka shi ya dawo saboda mantuwa da ya yi,wato wasu fayal da ya ije da nufin ya tafi dasu sai gashi ya manta da su kuma ana buƙatar su.Ashe da rabon ya yi gam da katar!Don shi ya ga matar aure dama tuni ya yaba da hankalinta.

Ko da ya shiga cikin ɗakin wani irin kasala ya ji y rufe shi ya faɗa kan gadon shi ya na jin wani irin shauki na ta ya na zagaye ilahirin jikin shi.Ko da ya shiga ɗakin faɗa kan gadon sa ya daɗe ya na jin wani girmar lamari har na tsawon lokaci,sannan daga bisani ya miƙe ya ɗauki fayal ɗin ya fito.

Kawai sai ya tsinci kansa da bin hanyar kicin ɗin ya ɗan tsaya nesa da kicin ɗin zuciyar sa na bugu da ƙarfi,take yake jin lamura suna sauya mishi har ya fara dana sanin dawowar sa gida gashi komai na son ya canza musamman akan yarinyar da take ba shi girma

"Abnaj fito na gyara muku tibin ku barta ta yi aikin ta,kun dame ta da surutu."Yace da yaransa da suke kicin ɗin suna ta zuba da Anty Juwairiya kaza,ita kuma ta na ta yi musu dariya ba yan ta basu kwan da ta soya musu.

Yaran suka bi shi suna murnar zai gyara musu tibi,bayan tafiyar sa ziciyar Juwairiya ya buga dam!Da ta kalli ƙwayar idanunsa cikin rashin sani ganin yadda ya kafa mata idanu lokaci guda,abin da ta hango ya matuƙar tsorata ta wanda bai yi kama da so ba sai tsantsar sha'a

warta da ta hango.In ko haka ne abincin ta ya ƙare a gidan.

Bayan fitar sa ta ɗaga labule ta na kallon farfajiyar harabar gidan,sai kawai ta ji hawaye ya na sauka a kan ƙuncinta bai yi kama da mutumim banza ba saboda ya na da dattako.To me ƙwayar idanunsa suke nuna mata?Ita kuma irin na ta jarrabawar kenan?

Kar dai ku manta sunan labarin "SAKACINA KO HALIN MAZA" Mu haɗu a shafi na takwai.Ga masu buƙatar shiga cikin group ɗina na whatsapp ga numba 08144072423_.

Kuma ƙofa a buɗe take na ƙorafi gyara ko ƙarin bayani ga zakakuran marubuta,har yanzu ni mai koyo ce.
Kar dai ku manta da wannan lintafin sadaukar wa ne ga zaƙauran marubuciya,kuma ƙawata (SUMAYYA NA'IGE) Allah ya ƙara fasaha ya sa ki fi haka,ina alfahari dake a cikin marubuta da irin taimakon da kike bani.

*FOLLOW, READ, COMMENT, SHARE*

*SAKACINA KO HALIN MAZA?*

*RUBUTAWA:-*
*JAMILA LAWAL ZANGO*

*SADAUKARWA GA:-*

*SUMMY M NA'IGE*
_(Aminiya)_

*FIRST CLASS WRITER'S ASSO....*

*SHAFI NA TAKWAS*

Tun daga wannan ranar Juwairiya ta ga canji a tattare da shi,ya sakin mata sosai kuma ya na matuƙar kyautata mata,ko hira yake da matar shi sai kiji ya tsoma ta ciki yace"Wai haka aka yi Juwairiya ita za ta faɗi gaskiya."

Ranar da ya fara mata hakan ta yi matuƙar razana ta kalli Anty Naja ta ga ko me za tace amma sai taga sai dariya take ta na jin daɗi har ta na ƙara tambayar Juwairiya,wani tsabar takaici kaɗa kanta kawai ta yi ta shige kicin ɗin wanda dama shi ya ƙwala mata kira don kawai ya tambaye ta.

Bayan sati ɗaya sai gashi ya dawo gidan da wuri da yake a ranar matar sa na gurin akin ta na night duty acan za ta kwana.Bayan ya yi sallar magariba ya kulle ko ina na gidan ya shigo,tun da taga ya dawo da motar sa ya wuce masallacin kofar gidan sa gabanta ya faɗi hankalinta ya tashi,domin ita canjin da ta gani a gurin sa ya na tsorata.

Bai fito ba ya na karatun kur'ani har kiran sallar isha ya tafi masallaci,sannan bayan ya yi sallah ya dawo ya zauna a falo shi da yaransa suna kallo shi kuma ya na aiki a laptop ɗin sa.
"Abnaj je ka kira min Antyn ka Juwairiya kace ta zo ta bani abinci."Yace mishi ba tare da ya kalle shi ba,burin sa ya ganta ya san ta ɓoye kanta a ɗaki don kar ya ganta.

Yaron ya ruga da gudu zuwa can ya dawo yace."Ga ta nan zuwa."Ya ci gaba da kallon sa bata jima ba ta fito da dogon hijabin ta har ƙasa.Ita sai yanzu dake matuƙar dana sanin gadin mijin wata da yaran ta da take,don a a kwai haramcin haka a cikin addini mace baliga da namiji ba muharramai ba dama na ukun su sheɗan ne.

Nesa da shi ta tsaya kamar za ta yi mishi magana sai kuma ta juya ta shige kicin ta ɗauko abincin shi ta ije mishi za ta juya."Ba kiji ba Juwairiya."Yace da ita ganin za ta shige ɗakin da take kwana har ta na haɗawa da gudu-dugu.

Tsayawa ta yi bata re da ta juyo ba ta na watsa da yatsun hannunta gani take kamar zai haiƙe mata kamar yadda ƙanin mahaifinta ya yi mata,amma sai ta ga ya ƙaraso ya tsaya ɗan nesa da ita ya miƙa mata sabuwar waya mai kyau a kwali ya ɗan daure fuska."Ga shi na ji Antynki tace Abnaj ya saka miki waya a ruwa ta lalace shine na hutar da kuɗin ta,amma fa ki kiyaye ki dai na basu don nan gaba in kika bari suka lalata sai na haɗa da bulala kafin na canza miki wata."Yace ya na kashe mata ido.
Zare ido ta yi ganin wayar da ya siya mata irin wanda take gani a hannun su masu kyau da tsada,ina ita ina wannan wayar ta na ƴar gidan Malam Shehu kuma me za ta ce ma Anty Naja."

Kamar ya  san me take tunani sai ya kaɗa kansa yace."Karki damu na san me kike tunani zan yi mata bayani.Kuma ba ni da nufin na cutar dake alkhairi ne zuciyata,don Allah ki karɓa kin san babu kyau mai da hannun kyauta baya."Yace da ita ya na wani marairaice fuska sai kace maraya.

"Gaskiya ka bar shi bana so ina gani a matsayina na  ƴar aiki bai kama ta na riƙe irin wayar nan ba,don daga ganin ta na san za ta yi tsada kuma in Anty Naja ta gani me zan ce mata?"Sai ta tsinci kanta da furta hakan yayin da takai aya ta tsare shi da ido ta na tambayarsa.

Shi ma ya ɗan razana jin tambayar da ta yi mishi kansa ya ɗan sosa ya kafe ta da idanunsa yace."Haba Juwairiya kina abu kamar ba mace ba,kice mata saurayin ki ya baki mana."

"Ka yi haƙuri don Allah ba na son kyakykyawar alaƙar mu da matarka ya ɓace,kai sheda ne mace ce na ƙwarai kuma ta yi min halacci."Tace dashi da murya raunanniya yayin da hawaye suka fara turereniya  a fuskarta.
Ganin haka sai jikinsa ya yi sanyi ya ɗan yi shiru ya na nazarin maganar ta zuwa can ya ja numfashi yace."Laifi ne don nace ina sonki ni fa bani da nufin na cutar dake,kawai ina son ki zamo uwar ƴaƴana ne."Tsananin tsoron da ta nuna ta na me gwalo ido sai abin ya ba shi dariya.

Tafe take cikin sauri bayan ta tashi daga aikin zuciyarta tunanin sabon halin da mijin madan ɗin ta ya fito dashi,yake damun ta har ta fara tunanin ko ta aje aikin ƙila in Anty Naja ta gane ba lalle-lalle ne ta fahimce ta ba.Kallon tsadaddiyar wayar dake riƙe a hannunta da ya bata take kallo wanda ya rantse ya maya in har ba ta ɗauka ba to zai ba wa Antynna ta da take tsoron sani ta bata da kanta.

Abin mamaki dai-dai za ta shiga gida ta ji an dameta da hon,kamar ba za ta juya ba sai kuma ta juya in da ta ga mijin Anty Naja a cikin mota ya na ɗaga mata hannu,wato biyo ta ya yi ba tare da sanin ta ba ya ga gidan su.Tsabar takaici ba ta kula shi ba ta shige cikin gida.

Koda ta gaya ma Mama abin da ke faruwa hankalin Mama ya tashi ƙwarai ta yi shuru kawai ta na jinjina abin a ranta,ta ɗauki tsawon lokaci ba tare da tace komai ba zuwa can ta nisa tace."Ina ga ko haƙura da aikin nan tunna mun sami jari Juwairiya,ni nafi son kiyi aure shine mutuncin ki.Kin san maza basu da ta ido zai iya furtawa hakan ya jawo miki matsala gara mu yi rabuwar mutunci,in ban da shi ma ina ke ina kishi da Anty Naja mace me mutunci."
"Nima haka na gani Mama hankalina ya tashi ƙwarai."Tace da ita ta na juya wayar da ya ba ta."Kinga gobe ki mayar mishi da wayar shi,kice ni na ce ki mayar masa na tabbata ya tsorata ki ne amma ba zai yi gigin bata wayar ta baki ba,in dai ba ya na so ya kira ma kansa ruwa bane."
"To Mama in sha Allahu zan mayar masa,ni ma bana son na riƙe irin wayar nan don Allah kaɗai ya san abin da Baba Sani zai faɗawa jama'a."
"Haka ne Allah ya fishi."Ta bata amsa tare da miƙewa don ɗauro alwalar kiran sallar magariba da ke ta kwaɗawa masallacin kusa dasu.
Washegari da ta je gidan bayan fitar matarsa ya dawo kamar yadda ƴan kwanakin yake mata,ta

na ganin shi ta ƙara tamke fuska kamar ba ta ganshi ba ta ji gaba da aikin ta.
Ta yi tunanin zai yi mata magana amma sai ta ji shiru na tsawon lokaci,da sauri ta waigo sai ta ga ita yake kallo kamar bai taɓa ganin ta ba.Miƙa masa wayar ta yi tace."Mahaifiyata tace na dawo dashi,kuma don Allah ka yi min rai ka fita sabgata domin ba za ta amince aci amanar Anty Naja ba."
"Ni kuma sai na shiga wani hali ko?Wannan dalilin ya sa kika ƙi ɗaukar wayata jiya da daddare sai ma kika kashe wayar.Dama masoyi ya na zama maƙiyi Juwairiya?"Ya ƙarashe maganar da sigan tambaya,a yadda ya furta maganar sai ta ji ranta babu daɗi,ganin namiji mai natsuwa ya na mata magiya akan ta so shi.

Wani irin abu ta ji a ranta in da ace matarsa ba ta shiga tsakani ba,babu yadda za'ai taƙi auren shi sai dai ba za ta zama butulu ba.Ganin taƙi kallon sa bare ya saka ran za ta yi magana,sai ma hawaye da ta soma ganin haka ya ɗauki wayar da ta ije mishi ya fice ya san ta na sonshi,amma tsoro ne ya cika mata zuciya in ko haka ne zai je har gida ya nemi aurenta.

Kwana biyu haka suke wasar ƴar ɓuya ganin haka sai ya dena shiga sabgar ta ko dawowa gida ya dai na,ya na shirye-shiryen zuwa gidan su ya nemi auren ta.
Ranar wata yammacin talata ta tashi daga aiki kasancewar an yi rana sosa,da yake lokaci ne na damina garin ya fara haɗa hadari.Juwairiya sauri take ta isa gida saboda ta kauce ma baƙin hadarin da yake tasowa ya na canza garin da yake duhu sosai.
Hon ta ji an danna mata ta waiga sai ta ga Daddyn Abnaj ne ya na mata murmushi yace."Maza shigo na kaiki gida kar ruwa ya zane min masoyiyata."Ta yi kamar ba za ta shiga ba amma ganin har an fara iskar hadari ya sa ta buɗe gidan baya ta shige,tare da haɗe girar sama da ƙasa don karya tambayeta dalili

Hakan sai ya ba shi dariya sosai bai ce komai ba suka fara tafiya, sai ya sai ta madubin motarsa dai-dai in da take zaune."Wato na zama direban ki ko."Ya jefa mata tambaya dai-dai lokacin da ya fara tafiya.
"Ina wuni."Tace ba tare da ta amsa mishi tambayar ba.
"Ba zan amsa ba ina fushi."Yace ya na kallonta ta gilashin motar.
Ba tace mishi komai ganin hakan ya sa ya fara magana da murya mai taushi."Matsalar ƴan mata kenan da kun ga namiji ya na ƙaunarku,shikenan kun samu zaren ja amma babu komai nima lokacina ya na nan zuwa,don na fara hango sona a cikin ƙwayar idanunki."
Ta ɗan saki ranta saboda ta fara sabawa da shi ya wan janta da ɗawainiya da yake musu ta ja numfashi ta sauke ta fara magana da cewa."Ku kuma maza ba amana ka san kusancin dake tsaƙanina da matar ka,amma ka bijiro da wannan lamari haba kai ma ka auna ka gani bai dace ba."

"Kija min aya da ya hana hakan ko hadisi."Ya faɗa a raunane kuma a taƙaice.Babu amma Bahaushe ya na girmama al'adarsa hakan ya saɓa ma al'adar Bahaushe."Sitiyarin motar ya buga da ƙarfi yace "Kin ji ko in da karatun naki ya tafi ina miki zan can addini kina yi min wata magana can,kawai na gane bakya sona ki ce na haƙura kina da wani hakan zai sa na bawa zuciyata haƙuri duk da na san za ta shiga wani hali."

Yanayin da ya yi maganar sai ya bata tausayi amma ta san abin da yake so ba mai yiwuwa ba ne.Murfin motar ta ɓalle za ta fita ganin sun ƙaraso gida ya yi parking,sunan ta ya ƙira da wata irin murya.Ta waigo ba tare da tace ƙala ba,sai ƙasa da kanta da ta yi wato alamun ta na sauraren sa.

"Ki yi tunani zuwa ƙarshen sati nan nake so na turo magabata na,ina ganin za ki dakata da akin nan kafin kizo a matsayin ƙanwa kin ga sai ki ɗora daga in da kika tsaya ki na samun lada rututu!

Ɓalle motar ta yi ta fice dai-dai lokacin da ya miƙa mata ƴan rafar ɗari biyar kusan kimanin dubu ishirin ba tare da ta karɓa ba ta fice,musamman da ta ga Baba Sani tsaye a ƙofar gida shi da wani mutum ya zura mata ido.

Ganin jikinta ya soma rawa ya kalli in da take kallo,sai hakan ya yi mishi daɗi domin faɗuwa tazo dai-dai da zama,ya buɗe murfin motar ya fito ya nufi su Baba Sani dake kallon Juwairiya kamar ya shaƙe ta.

Da sauri ta matsa za ta bi ta bayansa ta shige cikin gidan da ya bake ƙofar,amma sai ya daka mata tsawa tare da jan hijabinta."Ina zaki ƴar iska maza dawo,iskancin naki ya kai har a kawo ki gida a mota.Kawai sai ya saka salati da ƙarfin sa ya ci gaba da cewa."Inna lillahi gara da ka mutu Yaya Ahmed in da ka na raye Juwairiya ita za ta ƙashe ka.Karuwa kika zama fa ke ko kunya duniya ba za ki jiba tunna baki ji na Allah ba."

"Ashsha!Subuhanallahi haba Malam ya za ka dinga jifan ta da waɗannan muggan kalamai?Iya sani na Juwairiya yarinyar kirki ne ta ɗaɗe ta na tare damu ta na mana aiki.Yanzu haka mun daidaita ne nake son ka bani auren ta,ma'ana na  yaba da hankalinta ina sonta."

Wayyo Allah faɗin haka da ya yi wato ya na son Juwairiya ji Baba Sani ya yi kamar ya watsa mishi fetur ya kyasta ashana domin baƙin cikin sa biyu ne a kan maganar.Na farko ta ya ya za 'ai mutum me hannu da shuni yace ya na sonta,sannan kuma baƙin kishinta ya taso ya lulluɓe mishi zuciyarsa kawai sai ya ƙara kuka ya na faɗin ma abokin da suke hira cewar."Kaji ko wai na ba shi aurenta bayan ya gama iskanci da ita ni nasan ya na naɗe tabarmar kunya ne.Amma ta ya ya zai auri mazinaciya!Ba Juwairiya dake tsaye ta na kuka ba har ta Daddyn Abnaj sai da yaji wani irin abu ya soke shi ya rintse idanunsa ya na jin kamar ya shaƙo wuyar Baba Sani,take ya fahimci wani abu wato na zaman ƙunci da suke yi iya zaman su da ita bata taɓa basu labari ba,duk da ya san cewa ba lai-lai bane ta gaya musu kasancewar ta na da zurfin ciki.

Ya kalli Juwairiya da ta ƙara sautin kukan ta ganin mutane sun fara taruwa Baba Sani yaci gaba da magana da ƙarfi ya na nanatawa,sai ta ruga da gudu dai-dai lokacin da Baba Sani ya kai mata bugu a bayanta.

Ba ta san ya suka ƙare ba ya dai shigo gida ya na ta faɗa tare da ja mata jifa'i kala-kala, Juwairiya ta so ta tanka saboda abin da ya yi mata a gaban mutumim da yake girmama lamarin ta,amma Mama ta hana duk san da ya gaya mata baƙa ta buɗe baki za ta yi magana Mama za

ta hana ta,har ya gaji da rashin mutuncinsa ya fice.

A ranar Juwairiya ta ci kuka sosai ta ji ta ƙara mugun tsanar shi a ranta.
Washegari ganin taƙi shiryawa taje aiki Mama ta shigo ɗakin ta tsaya ta na kallonta tace."Juwairiya ba zaki je aiki bane naga rana ta yi."
 "Na haƙura da aikin Mama gara na zauna a gida dama kin san mun yanke shawarar na daina zuwa,sai ga abin da Baba Sani ya yi min a gaban shi Allah kunya nake ji matuƙa.Karuwa ya kira ni."Sai kawai ta saka kuka ta na jin zafin kalmar da ya danganta ta da ita."
Mama a ranta har tafi Juwairiya damuwa amma sai ta ɗan gyara murya tace."Ki yi haƙuri komai lokaci ne watarana sai ya yi dana sani,amma da kin daure kije kila ma ya shafa miki lafiya don na tabbata ba zai ƙara miki maganar soyayya ba,ganin yadda ya tozar taki."
 "To Mama shikenan a haka rayuwata za ta ƙare duk wanda ya fito neman aurena sai Baba Sani ya ɓata lamarin gaskiya na gaji."Tace cikin hawaye yayin da ta tuna katoɓarar da ta yi na faɗin hakan,kamar ta nuna ta na son auren kenan sai ta zari hijabinta da sauri ta fice zuwa aiki.

Ko da ta isa bata sami Anty Naja ba duk da ta san dama abu ne me wuya ta same ta,abin mamaki ta yi sallama ta shiga fuskarta babu walwala,sai ta same shi zaune akan one siter ya zuba tagumi ya na kallon hanya,ganin ta ya saka shi sakin ajiyar zuciya mai ƙarfin gaske.
 "Shigo mana Juwairiya hankalina ya tashi matuƙa na yi zaton wannan mara kirkin Baban nan naki ya hanaki zuwa "Yace da ita ganin ta dogare a bakin ƙofa,ta ɗan tsaya ta na kallon shi sai kuma ta ƙara haɗe fuska haushin sa take ji don shi ya yi shishshigi a lamarinta,har ya saka Bab Sani ya yi mata wannan tozarcin.

"Gaskiya ban ji daɗin abin da ya faru ba!Haba sai kace ba ƙanin mahaifinki ba.Lamarinsa ya tsoratani baƙin cikina yadda yaƙi yadda da maganata akan ina sonki da aure.Kawai ki gaya min dangin ku naje can na nemi aurenki."

Yace da ita ya na kare mata kallo don ya fahimci a wani hali take,takaici ya kamata jin abin da ya faɗa sai ta miƙe hanyar kicin ba tare da tace mishi komai ba.

Gabanta ya sha tare da riƙe mata hijabi yace."Na fa fara ƙosawa da halin ko in kula da kike min haba waike dutse ne a ƙirjin ki ba zuciya ba!Ki ji tausayina ko don halin da kike ciki ki zaɓe ni a matsayin mijin ki hatta mahaifiyarki ba za ta zauna a wannan gida ba.

Takai hannu da nufin ta ƙwace hijabinta sai ya riƙe hannun cikin kalar tausayi ya na jin kamar ya yi mata kuka,ganin sam ba ta da rangwame akan soyayya.Baki ta buɗe da nufin ta yi magana sai suka ji sallamar Anty Naja ta shigo da sauri da alamun gajiya tare da ita.

Da sauri ya saki hannunta ya matsa gefe ya na zare ido,ita ma cikin tashin hankali ta tsaya ta kasa haɗa ido da ita ta na jiran tashi n hankalin da za ta fuskanta.
Amma sai dukansu ta basu mamaki ta faɗa kan kujera ta na lumshe ido "Wash Allah! Na gaji matuƙa Juwairiya bani ruwa don Allah."Tace cikin sakin fuska ba tare da ta fahimci komai ba."
Da sauri Juwairiya ta shige kicin ta na mamakin sokanci irin nata haba ta ya ya za'ai tace bata

fahimci komai ba.Bayan ta kawo mata ruwan ta haɗo har da abin motsa baki,ta shige kicin ta ci gaba da aiyukan ta can sai ga shi ya shigo yace."Ina jiranki in kin gama zaki tafi ina hanyar da nake tsayawa sai mu ƙarashe tautaunawar.

Ganin ba zai saduda ba Mama tace ta haƙura da aikin in ta bata kuɗin aikin ta na wata haka kuwa aka yi,bayan ta yi mata albashi ta ƙara mata harda zannuwa masu kyau biyu nata sai ɗaya Mama ta ɗinka,kasancewar suna da biki a  family ɗin su kuma tare da Juwairiya za su tafi garin Kano.

Hankalin Anty Naja ya tashi matuƙa ganin ba ta zo aiki ba,ta shiga ruɗani ta din ga tunanin ko ta yi mata wani abu amma bata gano ba.Shi ma hankalinsa ya tashi sosai duk da yaso sai sun gama daidaitawa a tsakanin su sai tabar aikin,amma ta yi sauri gashi ya na son yaje gidan ya na tsoron tijararren ƙanin mahaifinta

Sai ya azalzala ma Anty Naja ta shirya ya kaita har ya na mata barazana da ya na nan akan bakan sa in dai ba Juwairiya ba sai dai ta bar aikin,ai kuwa ba shiri ta shirya suka taho ya ijeta a kofar gidan ta shiga ciki ya zauna da yaransa ya na jiran ta fito,burin sa ya ga Juwairiya.

Juwairiya na tsakar ta na girki Mama ta na zaune ta na jan carbi ta yi sallama ta shigo,da sauri Juwairiya ta saka hannu ta rufe fuskarta ta na dariya.
Anty Naja ta harareta ta na kallon Mama tace."Da ma Mama haka Juwairiya take bata da kirki? Kawai ta guje mu ba tare da mun yi mata wani abu ba,hankalina ya tashi ƙwarai Mama gaskiya ba ta kyauta ba."

Ta ƙarashe maganar ta na kallon Juwairiya sannan ta ɗora da cewa "Ko mun yi miki wani abu ne?Ai gaya mana ya kamata ki yi ba ki ɗauke kafafunki ba.Ni da yara da Daddyn su Abnaj duk hankalin mu ya tashi."

Mama ita ba tace komai ba tace komai ba sai dariyar yaƙe take mata,bayan sun shiga ɗaki suka yi gaisuwa a tsakanin su sanann shiru ya biyo baya.Sannan Anty Naja ta katse shirun tace."Me ya faru Mama kwana biyu bata zo aiki ba na yi tunanin ko wani ba lafiya,amma da nazo naga kowa lafiya.Ko na yi laifi ne Mama."

Matuƙar kunya sai ya lulluɓe Mam ta ji kamar ta nitse ta rasa yadda za ta fara mata bayani,har Juwairiya ta yi sallama ta shigo,ganin Mama ta kasa mata bayani ta kalli Juwairiya tace."To ko auren ne ya zo,in kuma wannan ne Mama ai ni ce me haɗo kayan ɗaki ko?"Ta ƙarashe maganar ta na me tsigar tambaya.
I ta dai Juwairiya ba tace komai ba ta na ta wasa da yatsunta,Mama ta daure tace."Ba shi bane ban san dai yadda zaki ɗauki zancen bane shi yasa na kasa sanar miki,amma ranar wanka ba'a ɓoyan ciji."

Gaban Anty Naja ya faɗi daram!Sai ta ji zuciyar ta ta raya mata lai-lai a kwai abin da suke ɓoye mata,duk da bata san ko menene ba amma taji ta firgita Allah ya sa ba wani lamari me girma ya

faru ba.
Ganin ta yi shiru ba tace komai ba jikinta ya yi sanyi Mama dai ta daure tace."Dama mijinki ya bijiro da wata magana ya na son auren Juwairiya har ya shigo da maganar gida,mu kuma muka ga rashin dacewar haka saboda irin halaccin da kika yi mana shi yasa nace ta dakata da aikin kawai ki nemi wani."Tace ta na karantar fuskarta.

Kar dai ku manta sunan labarin "SAKACINA KO HALIN MAZA" Mu haɗu a shafi na Tara.Ga masu buƙatar shiga cikin group ɗina na whatsapp ga numba 08144072423_.

Kuma ƙofa a buɗe take na ƙorafi gyara ko ƙarin bayani ga zakaƙuran marubuta,har yanzu ni mai koyo ce.
Kar dai ku manta da wannan lintafin sadaukar wa ne ga zaƙauran marubuciya,kuma ƙawata (SUMAYYA NA'IGE) Allah ya ƙara fasaha ya sa ki fi haka,ina alfahari dake a cikin marubuta da irin taimakon da kike bani.

*SAKACINA KO HALIN MAZA?*

*RUBUTAWA:-*
*JAMILA LAWAL ZANGO*

*SADAUKARWA GA:-*

*SUMMY M NA'IGE*
_(Aminiya)_

*FIRST CLASS WRITER'S ASSO....*

*SHAFI NA TARA*

Abin mamaki da yake macece wayayyiya sai bata nuna komai ba duk da irin tarin luguden da zuciyar ta take mata,ta na jin kamar ta fita ta shaƙo shi munafiki kawai haba ya kamata a ce ta

ɗago tuntuni saboda yadda yake yabon ta da kalamai magana ɗaya biyu ya sako sunanta,amma da yake ba ta da wayo sai ba ta ɗago ba ta danganta kular da yake bata a dalilin ta na kular mishi da yara,sam ba ta yi tunanin zai ce ya na sonta ba ganin basu da komai ƴar Malam Shehu.
Wayancewa ta yi ta na dariyar yaƙe tace."Haba Mama ni na yi tunanin wani lamari ne me girma yasa kika hana ta,amma akan wannan ɗan ƙaramin abin zaki hana ta,in dai a kan wannan ne karku damu ai gara ya auro wacce na sani da ya ɗauko min wata.Kuma karku manta shi fa mijin mata huɗu ne,don Allah karku ce zaku hana mishi aurenta."

Yanayin yadda take maganar ya nuna da ƙarfin hali kawai take yi,amma ta na ƙoƙarin ƙaƙalo dariya.
 "Haba ƴar nan ai ana barin halas don kunya kawai ya nemi wata,amma Juwairiya ba tsarar auren sa bane."
Anty Naja ta dage ta riƙe kishinta ta na ba ma Mama baki akan ta haƙura ta yadda ayi auren,sannan ta ɗora da ko ba zasu bashi ba don Allah Juwairiya ta dawo aiki.

Daga ƙarshe ta yi ma Mama sallama ta fita har ta na tonon Juwairiya ta fito tare suke da angon ta yazo biko,ita dai ba tace komai ba a ranta take mamakin wani irin hali take dashi.Bayan ta jaddadawa Juwairiya tazo aiki ta yi musu sallama ta fita.

Bayan ta fita ta buɗe murfin mota ta shige tare da haɗe girar sama da ƙasa a ranta ta na mamakin raina mata wayo da ya yi wato ya turo ta ta yi mishi bikon budurwar shi,bayan ta sheda Juwairiya yarinyar kirki ne sai tace amanarta suke ci.
 A yadda ya ga yadda ta fito sai hankalinsa ya tashi don bai yi tunanin za su gaya mata abin da ke tsakanin sa da ita ba,sai ya yi dana sani da tuntuni ya tare ta da maganar.
Bayan sun fara tafiya ya kalleta yadda ta ƙara cin magani fuskarta ba rahama yace cikin ƙarfin hali ya yi mata tambayar."Ya take ko ba ta jin daɗi ne?"

Haba kamar jira take ya yi tambayar lokacin da take kallon waje ta fara bala'i in da take shiga ba nan take fita ba tace."Munafiki da zamu taho ai da ka gaya min biko zan je na yi maka.Da ma amanata kuke ci kai da ita da ta amince ƙila sai dai in ji ta tare a gidana ko."

Nan ta ɓalle ta na gaya mishi kalamai zafafa mara sa daɗin ji,in da take shiga ba ta nan take fita ba a hanya ta zage shi tatas! Ta yi mishi wankin babban bargo.Shi dai shiru ya yi mata don ya san ya ibo ruwan dafa kansa kuskuren shi ɗaya da bai sanar mata ba,kuma bai ɗauka su Juwairiya za su yi suɓul da baka su gaya mata ba.
A haka suka kwana sam ba ta barshi ya rintsa ba,shi kan shi bai san ta iya rikici ba,sai ayau ya san ta na da zafi mata da kishi humh ba'a magana.
Washegari Juwairiya ta na zaune ba ta da ninyar zuwa aiki amma Mama ta matsa mata akan taje.Sai dai yadda ta ga gidan ta san ba su kwana lafiya ba.

Tun daga falon take kallon yadda ya hargitse ko ina an birkita shi sai gabanta ya fara faɗi ta san

cewa a kwai wani girman lamari da ya faru.
"Munafuka kema me ya kawo ki gida!Maza fita matsiyaciya me kwacen miji kawai,in banda ke jahila kina ƴar talaka za kiyi tunannin mijina zai aureki."Anty Naja take magana cikin zafi sannan ta ɗora da cewa."Fita kar na ƙara ganin ki a gidana,sai abi wani sarkin amma mijina yafi ƙarfin ki.

Ko da ta dawo ta sanar ma Mama tace."To shikenan Allah ya sa haka yafi alkhairi.Hankalin Baba Sani ya kwanta ganin Juwairiya ta bar aiki kullum ta na gida,hakan sai ya yi masa daɗi musamman da yake tunanin yanzu komai zai kwaɓe musu.
Juwairiya ta yi tunanin Baban Abnaj zai biyo bayan ta,amma shiru kake ji Malam yaci shurwa wato matarsa taci ƙarfinsa.Ganin haka sai suka kama sana'a sosai da kuɗin da Baban Abnaj yake basu,yanzu har abincin siyarwa suke yi Ibrahim ya na kai wa ƙofar gida.Kuma suna samu ba laifi don da shi suke cin abinci.

*********

Kimanin shekaru huɗu da auren su suna zama cikin so da ƙaunar juna,sai ƴan saɓanin da ba'a rasa ba a tsakanin ma'aurata.Kullum A.m ya yi kasaƙe ya ji Zainab tace mishi ta na da ciki amma hankalinta ba shi a gurin tunna ba ta taɓa yi mishi maganar baby ba.

Lamarin sai ya fara damunsa musamaman da ƙannin shi da sa'annin shi suna da yara,amma shi matarsa ko ɓatan wata ba ta taɓa yi ba.

Sai kuma Allah ya ɗauki son ƴara ya ɗora mishi in ya gan su kamar ze zare.Ya na matuƙar son yara kullum ya na hanyar gidan ƴan'uwan shi ya na manne da yaransa.Daddy ɗin shi ya fara ƙorafi ya na tsoron kar A.m ya ɗauko rashin haihuwa sai ya fara mishi ƙorafi sosai kullum ya na kiran waya akan suje likita ya duba su.

Ganin yadda ya ɗauki son yara ya ɗora ma kansa sai Zainab ta yi gum da bakinta ba ta taɓa suɓutar baki ta nuna mishi ita ce ba ta son ta haihu take shan ƙwayoyi ba.
Sun ɗan fara samun saɓani yadda yake kwaso yaran ƴan'uwan shi ya kawo gidan ya siyo musu kayan wasa.Ranta ɓaci yake sosai ta na ganin hakan kamar takuratawa rayuwarta ne,duk yaran da ze kwaso ba ta musu komai sai masu aiki.Gaskiya Allah ya jarabce shi da son yara sosai.

Wataranar Alhamis Zainab ta tashi da ciwon ciki kamar za ta mutu,hankalin A.m ya tashi matuƙa ganin a sume ya ɗauke ta ya saka a mota suka nufi asibiti.
Bayan an karɓe ta aka yi mata ƴan gwaje-gwaje tare da turata ɗakin hoto,duk abin da ake ta na kwance kamar gawa ba ta san in da kanta yake ba.Likita ya gano mahaifarta ce ta samu matsala sakamakon tarin ƙwayoyi da ta din ga ɗinkira ma kanta masu ƙarfi na hana haihuwa.Wanda sakamakon haka mahaifar na gabda ruɓewa in da likitan ya ba A.m shawarar ayi mata aiki a cire mahaifar.

Tsananin tashin hankali A.m ya shige shi ya din ga kallon likitan kamar ƙarya ya yi mishi."Me yasa Zainab za ta aikata hakan?Hakan na nufin ba ta son shi ne har take shan maganin hana ɗaukar ciki don kar ta haihu?"
Irin tarin tambayoyin da yake yi ma kansa kenan amma ba shi da amsarta,daga bisani ƙeƙeshe zuciyarsa ya yi kan ƙaryata likitan ya san Zainab ba za ta aikata hakan ba,musamman yadda ta ga Daddyn shi ya mutu akan ya ga ya haihu,sannan yadda yake nuna mata ya na son ta haifa mishi baby ta na nuna masa Allaha ne be kawo ba.To hakan na nufin yaudararsa take.

Sai ya yi zuru ya na kallonta da take saukar da numfashi cikin rashin haiyaci ta na bacci,sakamakon allurar baccin da likita ya yi mata.Sai ya shafi fuskarta ya na me tausaya mata halin da ta shiga.

"Gaskiya ban yadda da maganar likita ba ina ta ya ya zan rayu ba tare da na ga ɗan cikina ba,duk da na san Allah ya ba jarabtar bayinsa amma gara wata jarrabawar ba wannan ba.Ya na ganin halin da Daddy ɗin shi yake shiga saboda rashin ɗa duk dukiyar da ya tara ya tafi a banza.In in haka ne ya zan yi da shares ɗin da na saka ma yarana tun kafin su zo duniya a ƙasashen waje.

Nan take zuciyarsa taƙi amincewa da abin da likitan ya faɗa duk da ya san asibitin su ƙwararru ne.
Kusan awa ɗaya ta na baccin wahala sannan ta buɗe idanunta.Da sauri ya riƙe mata hannu ya na shafar kanta."Kin tashi babyna sannu. Yace ya na ƙoƙarin temaka mata tashi ta zauna.

Bayan ya haɗa mata tea ya ba ta tasha ta lumshe idanunta ta na ji har yanzu wani abu ya na karta mata a cikinta,ita kaɗai ta san irin tarin azaba da raɗaɗin da take kwankwaɗa.

"Ya jikin sannu kin ji abin da likita yace game da ciwon ki?"Ya tambayeta da murya mai sanyi ya na gyara mata ɗaurin ɗankwalin ta da yake son ya warware.Ba tare da tunanin komai ba tace."A'a hubbina."A taƙaice ta ba shi amsar don ba ta son dogon surutu.

Ya ɗan ja numfashi ya fesar ya jinjina girman lamarin baya so ya gaya mata,bai san yadda za ta karɓi lamarin ba cewar ba ta haihuwa mahaifarta ya fara ruɓewa wanda dole sai an yi mata aiki.To amma ya na son ya gane shin da gaske ita tasha maganin hana ɗaukar ciki har ta illanta musu kanta,ba yan haka da ya bari sai ta warke.

"Likita yace ba zaki taɓa haihuwa ba yanzu ma mahaifarki za'a yi miki aiki a cire."Yace da ita ya na son yaga yadda za ta ƙarɓi lamarin.
"Inna lillahi.Tace tare da bayyano wani tashin hankali a fuskarta nan take fuskarta ta sauya sai hawaye,ta yi ƙasa da kanta ta na son ta yi magana amma ta kasa sai hawaye dake ta gasar sauka a fuskarta.A zuciyar ta kuwa illa tarin nadama da faɗin"Na cuci kaina!"
"Ina son na sani da gaske ke kika illan ta mahaifar ki Zeey sabosa bakya son ki haihu da ni,ko dama ba kya sona ne ko a kwai wani ƙudiri a ranki."Yace bayan ya yi ƙasa da kan shi dai-dai da kunninta saboda baya son aji me yake faɗi.

Ta dago ta kalle shi fuskarta cike da hawaye ganin yadda fuskarsa ya bayyana da tashin hankali,don in ba ta yi ƙarya ba har hawaye ta gani a fuskarta.

"Na shiga uku yanzu in yace ya na son ya haihu ga shi ni bana haihuwa ya zan yi?Kuma wallahi ba zan taɓa iya lamun ce na gan shi da wata mace ba.Gara ma ace na ga ranar mutuwata!Tace a zuciyarta ta na kukan nadama.

"Ka yi haƙuri hubbi ka yafe min na san na yi wa rayuwata illa ba zan taɓa haihuwa ba!Girman lamarin ya yi wa zuciyata girma.Duk akan sonka ne ina son karka juya min baya inna fara haihuwa na saki sanann jikina ya canza,kuma na sha jin kana faɗin baka son jikina ya canza kafi son na kasance yadda nake.Kuma a wannan lokacin ban shirya haihuwa ba gani nake yara kamar takurane a gareni duba ga irin yanayin aikina."Sai ta fashe da kuka ta na ƙarawa taci gaba da cewa."Wallahi ba zan iya buɗe idanuna na ga wata mace a matsayin muharramar ka!In kuwa ranar ta kasance to kasa a ranka zan kashe kai na na kasheta sannan na kasheka.In taƙaice maka mutuwar kasko za muyi,don ina sonka ba zan juri wata a kusa dakai ba." Tsananin tashin hankali ya shige shi tare da nadamar furta mata waɗannan kalamai da yake na baya son yanayin ta ya canza,duk da be yi tunanin za su yi tasiri a gareta ba har ta aikata wannan abu su yi dana sani.

Ya zura hannun sa a aljihun wandon sa ya na kallon yadda fuskarta ya canza zuwa tsabar tashin hankali,ita kanta ya san ta yi nadama amma kuma mara amfani.
Ganin be ce mata komai ba ya na tunanin wanda shi kansa be san tunanin da yake ba,sai ta ci gaba da cewa."ko ma me ya faru duk akan sonka ne A.m ina kishin ka zan iya komai a kanka,son da nake maka ya sa na lalata mahaifata."
Ta kalle shi idanunta ya na zubar hawaye ta kama hannunsa ta haɗa da nasa tare da kai bakinta dai-dai saitin kunninsa."Don Allah ka yi min wani alƙawari,ka amince za ka yi min sannan gaya maka."
Ya damƙe hannunta ƙaƙam ya na hawaye matuƙar tausayinta ya kama shi ganin duk akan son shi ta shiga cikin wannan halin domin ta burge shi.
"Na yi miki alƙawari amma wa ya gaya miki in mace ta haihu mijinta ya na tsanar ta ni fa ina yaba miki kyawun halittar ki amma ba wai ba na son ki haihu ba.Yanzu ya zan yi da iyayena da suka ɗora idanunsu akaina suna son suga jikar su?"
a tambayeta ya na ganin tsananin wautar ta da ta aikata hakan,ita ma da ma wannan kan gabar take so yazo sai ta ƙara damƙe hannunsa tace." Ka yi min alƙawari ba zaka taɓa juya min baya ba kuma wannan ya zama sirri tsakanin mu cewar nice ba na haihuwa,sannan ka gaya ma dangin ka cewar matsalar da ga gareka take.Bayan haka ba za ka taɓa yi min kishiya ba,in kuma ka yi to lai-lai nice ajalinmu baki ɗaya."
Ta faɗa da farko da son ya ɗauki alƙawarin muryarta a shaƙe ta na murza hannunsa,amma daga ƙarshen maganarta sai ta ƙarashe da murya kamar wacce take ba shi umurni ko tsoratarwa.

Rungumeta ya yi ya na jin matuƙar tausayin ta duk da girman lamarin amma sai be ga wata illa a ciki ba,musamman da ya ga duk akan sa lamarin ya faru don haka zai amince ya gaya wa

iyayensa da hakan, dama shi a duniya be ga wata mace wacce za ta haɗa kanta da Zey ɗin sa ba ita kaɗai ya ji ta burge shi kuma zai ci gaba da son ta ba tare da ya haɗa ta da wata ƴa mace ba don babu ita a duniya.

"In dai akan wannan ne karki damu na miki alƙawari,zan shirya mana viza zuwa ƙasar indiya a duba min ke don ban yadda cewar ba zaki taɓa haihuwa ba.Ƙara ruƙunƙume shi ta yi ta na faɗin."I love you nureel ƙalbi.!"

Loakacin da suka ji Zainab ba lafiya hankalin su ya tashi take a ka cika asibitin domin sun ɗauka ko ciki ta samu.Mahaifinta da ba shi ƙasar ya na jin ta na asibiti ya biyo jirgi ya dawo,ya na ta addu'ar Allah ya sa ta samu juna biyu,saboda ya na tsoron kar ita ma ba ta haihuwa kamar Mominta,duk da ya so ya ƙara aure ta yi ruwa ta yi tsaƙi ta hana.

Wani irin gata suke nuna mata sosai musamman gidan su A.m duk tunanin su ya sami ɗa ne,saboda tunanin su ya sa suke yi mata abinci irin na masu ciki suna kawo mata.
Hakan sai ya sa jikin A.m ya yi sanyi ya na tausayin su don haka ya shirya musu biza suka wuce Indiya domin a duba lafiyarta.
Kwanan su biyu suka huta sannan suka fara ganin likita,sai dai gwajin farko da suka yi mata aikin gaggawa suka sa aka shigar da ita tiyata,saboda mahaifar ta fara ruɓewa ta na narkewa a jikinta wanda hakan zai iya kawo mata matsala.A.m ya shiga tsananin tashin hankali duk yadda yake cikin tashin hankali sai ya kwantar da na sa ya na lallashinta ganin ta na son ta yi ƙaramin hauka.

Be baro ƙasar ba sai da ya tabbatar ta warke garau babu wanda ze ce an yi mata aiki.Sannan suka wuce zuwa yawon shaƙatawa don ya kwantar mata da hankali.
Zainab ta yi kuka har ta ba uku lada daga ƙarshe suka tattaro suka dawo cike da alhini.
A lokacin da A.m ya sanar ma family ɗin sa sun shiga cikin tsananin tashin hankali barim ma Daddy da har sai da ya yi kuka,ya rungume A.m ya na shafa bayan sa da tsabar tausayi da ya cika mishi zuciya." Yanzu son kai ma ba zaka ga ƙwanka a duniya ba.Allah Sarki ni da kai ne kawai ba mu da rabon haihuwa."Sai ya ci gaba da sharara hawaye.

Mahaifin shi ya jinjina lamarin tsananin tausayin ɗan na sa ya kama shi."Ni yanzu nafi tunanin matarsa an ya anyi mata adalci ina ga ka bata zaɓi kawai,domin na tabbata da ita ne ke da matsalar aure zaka ƙara in kuma ta amince za ta zauna dakai kaga ba'a shiga haƙƙin ta ba."Yace ya ba kallon ɗan nasa cikin tausaya wa.

A.m ya ji matuƙar tausayin iyayen nasa ganin yadda suka tashi hankalin su,suna jimami da alhini anya ya kyuata musu kuwa.Sun ba shi tausayi matuƙa wanda ya sanyaya jikinsa amma ko ma menene ya riga ya yi mata alƙawari.
"Haka ne Baba nima na bata zaɓi,amma tace ba za ta iya rayuwa ba ni ba."Ya ba shi amsa kansa duƙe." To shikenan Allah ya kyauta ai faɗan likita ba na Allah ba ne,sai kaga Allah ya canza lamuransa "Sun yi matuƙar jimami suka fauwala ma Allah lamuran sa ƴan'uwan shi suna ta yi mishi tayin ya karɓi yara daga cikin ƴaƴan su,duk da ya na son hakan sai dai ya san Zey

ɗin shi ba za ta yarda ba.

Zaman nasu sai yaƙi jituwa tun daga lokacin sai suke samun saɓani da ya fara mata faɗa, sai ta saka kuka tana faɗa masa don ya ga ba ta haihuwa ne.
Tun ya na haƙuri har ya fara kai su gaban iyaye mahaifin shi kullum haƙuri yake ba shi ya na nuna mishi halin mata,dama tunna baya haihuwa ya shirya karɓan fiye da haka a gurinta.

Rashin zaman ta a gidan shi yake ƙara damun sa kullum ya dawo aiki ba ze sameta  a gida ba sai tarin ƙazaman ƴan aiki masu kama da mayu a gurin kallo.Shi ya manta rabon da yaci abinci me daɗi in dai ba gida yaje ba ko,gidan amininshi A.k.Kullum ba ta da gurin zuwa sai ƙawa ta gayyace ta bikin ƙawarta ana birthday ɗin ƴar ƙawarta aikin ta ne kullum yadda ka san ana tsikarin ta in ta zauna a gida mace kamar me aljanun fita yawo.

Ya dawo da misalin karfe huɗu da rabi rabi na yamma yanayin garin hadari yake haɗawa ya canza iskar garin ta na bada wani iska mai sanyi-sanyi babu abin da yake so ya sha ruwan tea me ƙamshi ya shige cikin bargo ya yi bacci shi da ƴar matar shi.

Sai dai abin takaici ya na shigo da motarsa ya ga ba nata motar tsaki yaja ya yi parking ɗin motar a kasale ya fito be kula sannu da ma'aikan gidan suke mishi ba ya shige ɗaki.

Sharab!Ya zauna a falon sa ya na jin wani irin ƙunci ya saka yatsu biyu ya tallabe gemunsa ya lumshe ido da takaici,burinsa ya buɗe idanunsa ya sauke su akan kyakykyawar matar shi amma sai ya yi tozali da mero me aiki da tiren abinci ta kawo mishi tsaye ta na kallonsa.
"Ke!Uban wa kike kallo."Ya daka mata tsawar da yasa ta watsar da tiren abincin za ta ruga,sai kuma ta dawo da sauri ta tsaya ta na ƙoƙarin gyara gurin ganin iri n aika-aikar da ta yi.
" Anty ce tace na kawo maka abinci in ka dawo."Tace da shi bakinta na rawa ta na ci gaba da kallonsa.Ji ya yi tamkar ya shaƙeta ya miƙe kamar ze kai mata duka da gudu ta ruga..
"Zainab kina bani tarin matsala na gaji da kwashe-kwashe da kike min gaskiya."Ya faɗa idanunsa suka ƙara rinewa saboda tarin damuwar da yake ciki.

Bata dawo gidan ba sai zuwa ƙarfe tara na dare ta shigo da gudu saboda ruwan da ake yi tamkar da bakin ƙwarya,a lokacin A.m na zaune akan kujera two seater ya matsu ta shigo yau sai ta gane kuranta.
Ba ta kula da shi da yake zaune da waya a hannunsa ya na dubawa ba,ta tsaya a falon ta na ƙoƙarin cire kayanta da ruwa ya soma jiƙata saboda tafiyar da ta yi zuwa cikin gidan.
Gyaran murya ya yi wanda yasa ta fahimci ya na falon gaban ta ya ɗan faɗi,amma ta dake bata ce komai ba sai ƙoƙarin ta na cire doguwar rigar da ya matseta kamar za ta yi amai,ta na ƙwala ma Mero kira.

Wani ƙarin haushi ya turniƙe shi ita sam ba ta kishin jikinta ganin shigar da ta yi,sannan ta na cire kayanta amma take kiran me aiki tazo kai Zainab lamarinta a kwai gyara.
Bayan ta cire rigar ta umurci Mero ta ɗauko mata wani wani kayan ta saka,sannan ta nufi gurin sa da yake zaune saboda tsaban takaici be kalleta ba bare ya tanka mata,sai kallon agogon

hannunsa yake.
Ba tare da nuna damuwa ba taja tiren abincin da ya saka Mero ta kwashe wan can ta kawo mishi,saboda tsabar yunwa da yake ji amma ya kasa cin abincin sam babu tes jira yake a gama ruwan ya ya yi take away.

Fara ci ta yi ta kalle shi tace."Habibi ba ka ci abinci ba lafiya."Banza ya yi da ita yaci gaba da kallon wayarsa ya na danne-danne a cikinta.

Kai hannu ta yi ta taɓa wuyan shi ko ta ji da zafi a tunaninta ba shi da lafiya,amma sai ta ji jikinsa normal.Taɓe bakinta ta yi ta ci gaba da cin abincin a ranta ta na faɗin."Miskilancinne ya motsa bari na kama kaina."

Kusan minti talatin ya na kwance be tanka mata ba har ta gaji da zama yaƙi kunna kallo ta san ta na kunnawa, ze taso mata tunna dama a yadda ta gan shi jira yake ta taɓo mishi,sai ta miƙe sif za ta shige ɗakinta ta hau charting.
Idanunsa a lumshe ba tare da ya buɗe ba yace."Da ga ina kike?"Yace a cikin wata irin murya me kama da da baya son maganar.
Dawowa ta yi ta zauna ta duburbuce ta fara in ina.Ya ƙara jeho mata wasu tambayoyin da cewa."Sai yanzu kika dawo ba na hana ki dawo min gida da daddare ba?Me yasa baki wuce gidan kuba.Kuma da izinin uban wa kika fita?"

Gabaki ɗaya ta tsorata ta kuma ruɗe ganin yadda yake jeho mata tambayoyin da ta kasa amsa koda ɗaya ne.
Miƙewa ya yi ya matso kusa da ita ya na kallon kayan da tasa ya ɗauka ya na kallonta a wulaƙance."Ba na hanaki saka irin kayan nan ba wai ke me yasa bakya kishin kanki yanzu fa a gaban ƴar aiki kika canza kaya,sam bakya kishin sirrina Zainab hauka kike son na yi a kanki na fara gajiya da halinki."

Duk cikin maganganunsa ba wanda ta ji haushi sai tambayar ta daga ina take da ɗan yi jim ta kuma dake ta ba shi amsa da cewa."Ina tunanin mun gama magana akan fita ba sai na tambaye ka ba saboda gaskiya ban ga a na wannan takurar a gidan mu ba.Kuma fa gidan ƙawar Anty Usaina muka je yau ake birthday ɗin ɗanta."Ta ƙarashe maganar ta na son ta ja hankalin shi ya sausauta fushin da ya ɗauka.
Ya ƙara jan tsaki me ƙarfi dama ya san tatsuniyar gizo ba ta wuce ta ƙoƙi.
Tsawa ya daka mata yace "Malama karki raina min wayo na gaji da waɗannan banzan bidi'oin da kika saka a ranki.Kin raina ni matuƙa Zainab baki ɗauke ni da daraja ba a matsayina na mijinki,watakila haka kika ga ana yi a aure a matsayinki na matar aure ba zaki shigo gidana ba sai tara da mintina."
Kaɗa kansa ya yi ya miƙe yaci gaba da cewa."Kin san nace miki in har kika fita ba da izinina ba,ban yafe miki ba kuma mala'ikun rahama suna tsine miki harki dawo sai ki kiyaye."
Hararan shi ta yi tace cikin gunaguni."Taɓ ni ai na gaya maka ba zan amince a takurawa rayuwata ba.Haka kawai to meye amfanin ilmina na lura so kake ka mai dani irin gidahuman matan nan marasa ilmi,waɗanda suke bari namiji na raina su wai duk in da zani saina

tambayeka Allah ya kyauta."
Da takaicin yadda ta raina shi bata shakkar shi yace."Ba ma fita ba na hanaki driving sai dai duk in da zaki a yi driving ɗin ki."Ya na faɗin haka ya fara taka matakalan bene ze haye.
A sukwane ta jawo rigar shi ta baya cikin fushi tace."Wallahi ba za ta saɓu ba wai bindiga a ruwa Ka mata ni zan yadda wani shashashan direba ya tuƙa ni,karka manta kusan motocina daga gidanmu na zo da shi bare ka yi min iko,in ma akan wace ka siya min ne ba zan ƙara hawa ba amma ba wanda ya isa ya kafa min dokoki."

Nu na ta da yatsa ya yi ya na cewa."Ba na hana ki kuma na yi miki warning akan riƙe min riga da kike yi ba,to wannan ya zama na ƙarshe da zaki ƙara wannan gangancin.Kuma kika kuskura kika zage ni sai kin raina kanki,don jikin ki ze gaya miki."

Dariya ta yi me sauti ta ba shi amsa da faɗin."A lai-lai da ka tabbata ɗan ƙwaya kamar ni zaka buga aiko ruwan sama se inna so bare wani gardi can.Duk mutanen gidan ku kuwa sai an koya musu hankali ai ban yi kalar matar duka ba.Ko ka manta matsayin uba na."Ta numfasa sanann ta ɗora ta na kallon shi da tsananin ɓacin rai ya sa shi tsaye ya na kallonta.

" Kuma da kake faɗin karna zage ka inna zage ka me za ka yi?"Tace mishi cikin zallar rashin kunya ta na karkaɗa ƙugunta.A.m ya yi ƙuta yace.
" To ki kwatanta ki gani fitsararriya kawai."
Baki ta turo mishi tare da murguɗawa." Ni ba fitsararriya ba ce banza mara m....".

Wani irin mari ya gaura mata wanda yasa ta ɗauke lokaci guda ta yi taga-taga za ta faɗi amma ta dake tare da kwarma wani uban ihu,abin ka da farar fata lokaci guda fuskarta ta sunduma domin marin ya gigitata sosai.
Amma saboda taurin zuciyarta ta cakume shi ta na ihu ta na zagin sa shi kansa ya yi mamakin kafiyarta,ture ta ya yi ya shige ɗakinsa tare da bugo ƙofar kai tsaye bayi ya wuce ya sakar ma kan shi ruwa,domin ta haɗa mishi zafi kwanyar shi har wani tafasa take yi.

Kar dai ku manta sunan labarin "SAKACINA KO HALIN MAZA" Mu haɗu a shafi na goma.Ga masu buƙatar shiga cikin group ɗina na whatsapp ga numba 08144072423_.

Kuma ƙofa a buɗe take na ƙorafi gyara ko ƙarin bayani ga zakakuran marubuta,har yanzu ni mai koyo ce.
Kar dai ku manta da wannan lintafin sadaukar wa ne ga zaƙauran marubuciya,kuma ƙawata (SUMAYYA NA'IGE) Allah ya ƙara fasaha ya sa ki fi haka,ina alfahari dake a cikin marubuta da irin taimakon da kike bani.

*FOLLOW, READ, COMMENT, SHARE*

*SAKACINA KO HALIN MAZA?*

*RUBUTAWA:-*
*JAMILA LAWAL ZANGO*

*SADAUKARWA GA:-*

*SUMMY M NA'IGE*
_(Aminiya)_

*FIRST CLASS WRITER'S ASSO....*

*SHAFI NA GOMA*

Bayan ya fito da ga wankan ya na jin yadda sautin kukanta yake tashi ya na mishi kuwwa a kunninsa,sai ya ji be kyauta ba da ya mari rabin ransa take ya zira doguwar riga ya fita don ya rarrasheta.

Ɗakin ta ya shiga ya ganta ta na ta kuka ta na haɗa kayanta tare da ƙoƙarin kira a wayarta,sai dai da alamu ba ta samu wanda take kira ba.Wayar ya fisge tare da rungumeta cikin tsigar rarrashi.
Dukan sa ta fara a ƙirjinsa ta na ƙoƙarin raba jikinta da na sa,da kyar ya samu ta sausauta kukan ta ɗan yi shiru ta na sheshsheƙar kuka cike da shagwaɓa.

Da ƙyar ta ya samu ta yi shiru amma ta rantse mishi duk ranar da ya ƙara kai hannunsa jikinta sai ta haɗa shi da Daddy ɗin ta,shi dai aikin lallashi yake ya na gaya mata maganganu masu daɗi har da kama kunninsa ya na faɗin ya tuba.

Bayan sun shirya suka kwanta cikin ƙaunar junan su kamar babu abin da ya shiga tsakanin

su.Yanayin garin sai ya basu damar yin bacci cikin shauki suna maƙale da junan su.
Washegari suka tashi kamar babu wani abin da ya shiga tsakanin su na saɓani.Bayan ya yi wanka ya fice gidan amininsa ita ma ta gallah wanka ta fice aiki.
Parking ɗin motarsa ya fito ya caɓe Anwar ɗan gidan A.k da ake goyo don yanzu ya iya tafiya.
Juya shi ya yi ya na dariya tare da ɗauko tsarabar sa ya ba shi wanda duk ze zo sai ya kawo musu,sannan suka shiga cikin gidan sai ga ƴayarsa ita ma ta rugo da gudu ya ɗauketa haka dai ya shiririce ya na musu wasa har ya ɗauki tsawon lokaci.
" Yau kai ne a gari in ji maƙi baƙo ka ga angon Zainab to sannu da zuwa."Matar A.k tace ta na dariya bayan ta kawo mishi ruwa.
Shafa kansa ya yi ya na dariya yace."Gaskiya kince wani abu irin wannan kirari haka,kin san ƙawar taki bata da dama ba ta bari na naje ko ina gaskiya kin cancanci tukwici."
Dariya ta yi tace."Gaskiya makka da madina nake so a kai ni."Tace da shi."Duk kin je sai sai in kina buƙatar zuwa sai na saka sunan ki a cikin jerin masu zuwa."Dariya suka yi duka.
Sannan ta wuce ta na gyara dinning domin cin abincin rana.Bayan A.k ya fito daga ɗakin baccin sa ya ba shi hannu suka tafa tare da tsokanar junan su A.k yace."Ina madam Zey."Ya shafa gemun sa ya ɗan canza murya yace ƴar rigima za ka ce min na san yanzu ta wuce gurin aiki."
Dariya ya yi shima ya na kallon shi."Ai hali ne ya zo ɗaya an haɗu ne da an dace."Su kai dariya tare da ƙara tafawa."Madam ta gama shirya abinci ka zo muci."A.k yace da shi yamutsa fuskarsa ya yi ya na kallon shi, nan take sai hankalin A.k ya tashi musamman da ya ga ya maida kan shi a jikin kujera ya na kallon shi.Nan take ya fahimci amininna sa ya na cikin damuwa.

" Ya dai aboki a kwai matsala ko yanayin ka ya nuna a kwai abin da ke damun ka."
Ya kauda kansa gefe ya na faɗin."Kai ma ka san matsalar a kan Zainab ce ta na ba ni ciwon kai lamarin ta a kwai gyara.Na rasa yadda zan ɓullo mata ga kafiya da taurin kai."
A.k ya watsa hannun shi in akan wannan ne be wani dame shi ba yadda ka san auren dole a ka yi musu kullum cikin faɗa."In dai akan wannan ne ba ni da matsala daku kai ba haƙuri ita kuma kafiya ni lamarin ki ya na bani mamaki.Kun fi kusa kun san yadda zaku sasanta kan ku."
Ya faɗa ba tare da wata damuwa ba don ba yau ya saba kawo mishi ƙarar ta ba,kuma ko yaje ba saurarsa take ba gashi shi baya iya haƙuri da fushin ta haka kawai su yi ta sa maka ɓacin rai.
"Ko zamu keɓe ina da wata magana da zan ɗan tautauna a tsakanin mu kuma sirri ce."A.m yace da muryar raɗa ya na kallon gefen matarsa don ya yadda da aminin na sa ba zai gaya mata ba.
"Ki kawo mana abincin falona."Yace sannan suka shge cikin ƙaton falonsa da ya sha gyara ya na ta ƙamshi.Bayan sun ci abinci sun natsa har sai da suka yi salar azahar sannan suka natsa tare da taɓa hirar kasuwancin su.
A.m ya gyara zama ya na kallonsa cikin fuskar tausayi ya fara magana duk da wani gefe na zuciyarsa ta na masa gargaɗin karya faɗa masa amma ya fara magana da cewa.
" A kwai wani sirri da na ɓoye a raina na san zaka fahimce ni kuma ka ba ni shawara me kyai kamar yadda ka saba,ina ganin kamar na yi wa iyayena rashin adalci da na ɓoye musu cewar ni ne ba na haihuwa bayan ba haka lamarin yake ba.

"Na yi wa Zainab alƙawarin ba zan yi mata kishiya ba kuma ba zan taɓa gaya ma iyayena cewar ba ta haihuwa ba,amma na yi tunanin za ta canza halayenta mu yi zaman lafiya amma kullum ƙara bijiro da abin da zai saka mu samu saɓani,jiya duk ruwan da ake ta na waje wai sun je fati kamar ba matar aure ba,gabaki ɗaya ba ta damuwa da halin da zan shiga in ta ɓata min."

Ya yi shiru ko zai ce wani abu amma be tsinka shi ba sai kallon shi da yake yi ganin haka sai ya ɗora da cewa." Jiya ta kai fagen da na mareta wanda daga baya na yi dana sani.Ka ba ni shawara kar Zainab ta haukani."

A yanayin yadda ya yi maganar sai ya ba shi tausayi,sai dai ya na mamakin wai Zainab ɗin ce bata haihuwa kuma ya yi mata alƙawarin va ze gaya ma iyayen shi ba,sannan ba ya yi mata alƙawarin ba ze ƙara aure ba to wane irin shawara yake son ya ba shi don ya san be wuce yace ya ƙara aure ya samu matar da za ta ba shi yaro ba.
"Gaskiya ka yi wauta kana tunanin in kai ne ba ka haihuwa za ta yadda ta zauna da kai?Kuma ka cuci iyayenka kullum muka haɗu da Daddy sai ya yi min ƙorafin rashin haihuwar ka ya na tausaya maka,ga kuma masoyinka da yake ɓatar da kuɗin shi gurin yi maka sadaka da neman maka magani."

Ya numfasa ya na kallon shi a tsanake yaci gaba da cewa."Wace shawara kake son na ba ka bayan ka yi mata alƙawarin ba zaka ƙara aure ba kasan dai zuriya ta hanyar aure ake samun su,don haka Baban soyayya kaje kuci gaba da soyewa kawai shine shawarar da zan baka."

Abin da A.k yace mishi kenan ya miƙe don ransa ya gama ɓaci.A.m shima miƙewa ya yi don ba shi da abin da ze ce kan shi ya ɗau zafi,shi dai ya san koma mene ne ba zai karya alƙawarin da ya yi mata ba.

Bayan sun fito ya kalli matar A.k da take tattara gurin da yara suka ci abinci ya na dariya."To ni madan zan wuce."Dariya ita ma ta yi "Wato an gama gulmar mu ko ba komai nima ina nan zuwa gidana musha namu."
A.m ya ƙara dariya yana cewa."Baku da dama ne shi yasa musamman mutuniyar ki.A.k ya ja hannun shi ya na faɗin.Muje ka ji in ka biye mata sai ta ɓata maka lokaci da surutun ta suka fice.
******
Juwairiya ta ƙara samun aiki a gidan wata mata mai suna Hajiya Binta,matar ta na da kirki matuƙar gaske yaranta bakwai.Kusan dukkan aikin gidan Juwairiya take yi,saboda yawan yaranta take wahala a gidan sai dai amma babu laifi suna ƙaruwa da ita.Matsalar ta ɗaya mafaɗaciya ce sam ba ta da haƙuri kamar zawo take,duk yadda take taka tsan-tsan amma sai ta rori abin da za ta yi mata faɗa.

Saboda ba ta saba da irin aikin ba sai yake ba ta wahala ƙwarai,in ta dawo aiki ba ta iya taɓuka wani aikin watarana ma sai tasha maganin ciwon jiki.

Ganin irin wahalar da take sha Mama ta ba ta shawarar ta haƙura da aikin,amma ta nace sai ta

yi musamman da ta ga kuɗin aikin na ta da tsoka.

Yaran matar kwata-kwata basu da mutunci ga rashin kunya abu kaɗan za su hauta da zagi suna ci mata mutunci,mahaifiyarsu kuma ba ta son ganin laifin ɗanta hakan ya sa ba ta kula su.
Abin da ya ƙara tsorata ta ganin sun girme mata ƙaramar cikin su ita ce take tunanin za su zo tsara da juna.

Hatta wankin su ita take yi musu don tsabar rashin mutunci harda pant da breziya suke ba ta wanki,amma ta yi haƙuri ta jure burinta ta samu abin da za su dinga ci.

Sai dai rashin mutuncin da suke mata da ta fahimci ba me ƙarewa bane ta yi tsalle ta fara nuna musu sam ba za ta ɗauka ba.
Hakan ya saka suka ƙara saka mata ƙahon zuƙa,domin zuciyar su tsabar hassada ce suna ƙyashin kyan da Allah ya yi mata musamman da suka ga sun ɓata jikinsu da mayukan bilicin.

Abin da Hajiya Binta ta tsira ya sa Juwairiya ta ji aikin ya fita a ranta,saboda kullum ta zo sai ta tuhumeta da cewar ta yi mata sata.Hakan ya tinzira ta ta saka a ranta duk ranar da ta ƙara za ta bar mata aikin ta.

Haka kuwa aka yi taƙi zuwa aikin bayan kwana biyu da barin aikin sai ga motar ƴan sanda da Hajiya Binta akan Juwairiya ta sace mata sarƙar gwal ɗin ta.
Juwairiya ta shiga cikin tsananin tashin hankali ganin yadda ɗan sandan yake ƙoƙarin tasa ta zuwa ofis ɗinsu,hankalinta ya tashi matuƙa ya dinga kuka tana rantsuwar ba ta ɗauka ba.Tsananin tashin hankalin da Mama ta shiga ba'a magana duk da ta san halinta,amma sai ta shiga ruɗu ta din ga tamabayarta da in ta san inda yake ta fito mata da shi,hakan ya saka Juwairiya cikin tashin hankali ta dinga wani irin kuka gani take kamar Mama ba ta yadda da ita ba.

Baba Sani ya sami abin da yake so don haka ya ƙara zuga Hajiya Binta kan ta tafi da ita ofishin ɗan sanda,burinsa ya cika dama tintuni yake addu'ar Allah ya sa haka ya faru.

Mama na gani aka tafi da Juwairiya ta na wani irin kuka gani take kamar dukan ta zasu ta yi har sai ta amsa laifin da ba ta aikata ba.Ganin an tafi da ita Mama ta nufi hanyar shiga cikin gida ranta na wani irin suya,hango halin da Juwairiya take ciki da yadda take kuka ta na kiran sunan ta,sai kawai gani akai ta yanke jiki ta faɗi ƙasa.

Hankalin Mariya ya tashi matuƙa wacce take zaune a ƙasa ta na kuka sosai,gani take kamar ita ta saka ta a cikin wannan hali saboda hanyar aikin da ta yi mata.

Ita da mahaifiyar ta suka kama Mama suka shigar da ita gida,sai dai daga baya kan dole suka kwasheta zuwa asibiti ganin numfashinta na ɗaukewa gashi ta na aman jini!

Baba Sani ya yi matuƙar jin daɗin faruwar lamarin duk da ba shi da shiri akan hakan sai dai ya

na ganin yanzu ne burinsa zai cika akanta,don ya tabbata basu da wanda zai yi belin ta hakan zai ba shi damar ɗora mata sharaɗin zai yi belinta amma sai ta amince za ta yadda da buƙatarsa,don haka ma yaƙi zuwa ogishin da nufin sai sun yi mata dukan kawo wuƙa ta galabaita saboda ya san ta a kwai kafiya.

Juwairiya na zaune a cikin cell ɗin ta ƙudundune kanta a cikin jikinta tun da suka kawota take kuka,tunanin halin da Mama take ciki yake damunta wani irin sauro da yake damunta da ihu da cizo,yasa take ta zubar jawaye ga yunwa dake ƙwaƙularta."Rabbi inni lima anzalta ilayya min khairin faƙir."Abin da bakinta yake faɗi kenan  cikin tsananin tashin hankali.

Tun da Hajiya Binta ta kawota ba ta ƙara zuwa ba sai washegari da safe lokacin ta matuƙar galabaita,bayan sun tuhumeta amma taƙi amsa laifinta dukan tsiya suka yi mata sannan aka maida ta.

Da rana sai ga Baba Sani ya shigo ofishin ya na zare ido,gurinta yazo ya na kallonta." Kin ga abin da kika jawo ma kanki kosaboda shegen taurin ranki.'Yace ya na kallonta duk da ita ba shi take kallo ba saboda taƙi ta kalleshi wani irin tsanar sa take ji matuƙa.

" Har yanzu kina da dama zan iya fitar dake amma sai kin amince za ki yadda da buƙatata."Yace da ita ya na kashe murya.
Wani irin kallo ta watsa mishi " Allah ya yi min tsari da mugun nufin ka,da na amince gara na tabbata a gurin nan ko ya zamo shine ajalina."
  "Ok haka kika ce ko?To ai shikenan kuɗina ya huta tunna kin zaɓi rayuwar zuwa gidan mutane kina sata."Yace tare da watsa mata harara ya fice daga ofishin,kuka ta saka tare da cigaba da addu'ar ta ta na roƙon Allah ya kawo mata mafita.

Kwanan ta uku a gurin ranar da Hajiya binta ta shigo ta buƙaci a saki Juwairiya taga sarƙarta,duk da cewa ƙazafi aka yi mata amma ko haƙuri basu bata ba.Ita dai da gudu ta dawo gida tasan yaran Hajiya Binta suka ƙulla mata wannan ƙullalliyar amma Allah ya fisu kuma addu'a takobin mumini.

Ƙarin tashin hankali da ta zo Mama ba ta a gida Ibrahim ne yake sanar da ita ciwon Mama,wani kukan ta saka ta fita zuwa gidan su Mariya domin Mariya bata gaya mata Mama ba lafiya ba.

Yadda ta ga Mama hankalinta ya tashi ƙwarai rungume Mama ta yi ta na kuka sosai.Mama ce ta buɗe ido jin muryar Juwairiya hankalinta ya ɗan kwanta ganin ta fito,don ba ta san halin da take ciki ba shi ya sa jikinta yake rikicewa.

Likita ne ya shigo ya miƙa ma Mariya takadda yace."Gashi ki siyo wannan maganin ya kamata ku din ga kwantar mata da hankali, domin ta na da hawan jini ga ciwon zuciya, matuƙar ana ɓata mata rai to watarana zuciyar za ta buga!"
Wani ƙarin tashin hankali Juwairiya ta shiga jin Mama na da waɗannan ciwuka rungumeta ta yi tana kuka."Mama kema mutuwa za kiyi?Don Allah karki mutu ki barni!Rayuwata za ta shiga

cikin garari.Allah na gode maka ka bani ikon cin jarrabawa,amma karka ɗauke min mahaifiyata ka barni da azzalimi."

Mariya ta kama ta ta rungume ta na buga bayanta hawaye ya na kwaranya a fuskarta tsananin tausayi ya cika mata zuciya ganin halin da take ciki."Kin ga ni Mama za ta barni ko!Wai me ya sa rayuwata tazo a baƙin jadawali ne?Nake kurɓar ruwan bakin ciki mafi zafi da ƙuna a zuciya."Tace cikin kuka." A'a Juwairiya karki faɗi haka!Kada ki kasa cinye jarrabawarki kin san Allah ya na jarraba mutum dai-dai imaninsa.Kar zuciya ta sa ki yi saɓo.Ina ji a jikina zaki ji daɗi a rayuwarki.Allah zai ba Mama lafiya."Ta gaya mata ta na shafa bayanta.

Daƙyar Juwairiya ta daina kuka sai ajiyar zuciya hannun Mama ta kama ta riƙe ta na kallonta.Duk wani hidima na asibitin su Mariya da mahaifinta suka yi har kuka ta yi ta na gode musu domin Allah ne zai biya su.

Bayan Mama ta samu sauƙi aka sallame su akan Mama za ta din ga zuwa ganin likita ta na karɓar magani,hankalin Juwairiya ya tashi ta na tunanin ina za ta din ga samun kuɗin da Mama za ta din ga zuwa ganin likita.

Kan dole ta ƙara saka Mariya ta nema mata wani aikin don sana'ar da suke yi sun cinye tsugune kawai suke,da fari Mama taƙi yadda ta ƙara yin wani aikin amma daga ƙarshe dole ta haƙura ganin yunwa na so ta yi musu tabo.

Kwasam ta haɗu da wani matashin saurayi mai suna Mas'ud Allah ya jarabci Juwairiya da son shi yaro ɗan gata da sanyin rai ga kyautatawa.Shigowarsa rayuwarsu ya sa sun samu canji sosai,duk da ya ga ita yar talaka ce amma be saka yaƙi sonta ba don da Allah yake sonta.Mas'ud ya na temaka musu sosai ya na aiki a Jami'ar Ahamdu Bello a library kuma ɗan samaru ne iyayen sa sun rasu sun bar mishi dukiya sosai,sannan ɗan kasuwa ne.

Juwairiya ba ta taɓa jin ta na son mutum ba sai akan sa, gabaki ɗaya ta ji ta na son ta aure shi sai dai tasan hakan ba me yiyuwa bane,don babu yadda za'ai Baba Sani ya barta ta aure shi sai dai akan yadda take jin sonsa, za ta iya fito na fito a tsakanin su ko gidan me unguwa za ta iya kai shi.

Haba tunna ya ga ya na zuwa gurinta ya saka tashin hankali yayin da shi ma Mas'ud ya kafe,ganin shi ma ɗan zamani ne sai yace bai tashi uren Juwairiya ba don bashi da kuɗi,nan take yace mishi kar ya damu ya amince zai yi mata komai.

Ranar da Mas'ud ya kira Juwairiya ya gaya mata Baba Sani ya amince da auren su har ya ba shi izini ya turo magabatansa,kawai jin sa Juwairiya ta yi amma ba ta yadda da abin da yace mata ba.Ganin haka sai ya ƙyaleta kawai in ta ga zahiri ta yadda.
Da misalin huɗu da kwata ɗan Baba Sani ya yi sallama ya shigo ya yi kiran Juwairiya taje shashin Baba Sani ya na kiranta a ɗakin matarsa.

Gabanta ya faɗi amma sai ta saka hijabinta ta nufi ɗakin ganin a kwai baƙi ya sa ta ji a ranta a kwai abin da ke faruwa sai ta tsaya daga kofa ta na sallama."Yauwa Juwairiya shigo."

Baba Sani ya faɗa da murya sanyaya a hankali ta yaye labulen ta shigo tare da tsaya daga nesa ta na kallon mutane jikinta ya bata dangin Mas'ud ne.

Miƙo mata alkur'ani ya yi tare da canza fuska kalar tausayi yace." Dangin yaron nan Mas'ud suka zo neman auren ki,amma ni bazan cuce su ba sun yi min tambayar kina da tarbiya nace gara suji a bakin ki, don nasan ke ƴar mace ce sannan kin yi yawon aiki gidajen masu kuɗi,duk mazan gidan sun sanki a matsayin ƴa mace ga abin kunya na satar da kika yi,har aka kulle amma ga kur'ani ki rantse musu hakan be faru ba "

Taɓ ji ta yi ƙasa ta gaza ɗaukarta ta ji wani irin hajijiya ya kamata." Inna  lillahi wa inna ilaihir raju'un."

Kar dai ku manta sunan labarin "SAKACINA KO HALIN MAZA" Mu haɗu a shafi na goma sha ɗaya.Ga masu buƙatar shiga cikin group ɗina na whatsapp ga numba 08144072423_.

Kuma ƙofa a buɗe take na ƙorafi gyara ko ƙarin bayani ga zakakuran marubuta,har yanzu ni mai koyo ce.
Kar dai ku manta da wannan lintafin sadaukar wa ne ga zaƙauran marubuciya,kuma ƙawata (SUMAYYA NA'IGE) Allah ya ƙara fasaha ya sa ki fi haka,ina alfahari dake a cikin marubuta da irin taimakon da kike bani.

*FOLLOW, READ, COMMENT, SHARE*

*SAKACINA KO HALIN MAZA*

*RUBUTAWA:-*
*JAMILA LAWAL ZANGO*

*SADAUKARWA GA:-*

*SUMMY M NA'IGE*
_(Aminiya)_

*FIRST CLASS WRITER'S ASSO....*

*SHAFI NA GOMA SHA ƊAYA*

Ganin taƙi karɓar kur'anin hawaye ya na zuba ƙuncinta ya yi murmushin mugunta,ya juyo ya na kallonsu sannan ya ƙara saka kuka har da hawaye share-share yace." Kun ga abin da na gaya muku ya zama gaskiya? A matsayina na ƙanin mahaifinta babu yadda ban yi da ita ba akan ta zama macen ƙwarai, amma taƙi jin maganata!"

Juwairiya da take cikin wani yanayi na tashin hankali mara misaltuwa,ta rintse idanunta ta na jin wani irin ƙaton abu ya taso daga ƙirjinta ya tokare mata kirji ya kuma ƙi wucewa.

Tana son ta ji saukar hawaye akan ƙuncinta ko ya rage mata raɗaɗin da zuciyarta take ciki.Kunnuwanta ba za ta iya jure jin kalamai da yake yi ba,ya na aibanta ta ita da mahaifiyarta.

Ta muzanta iya muzanta da ƙyar ta yi nasarar jan jikinta ta fita zuwa shashin su,ta bar shi da bayin Allah da suka yi zuru suna kallon shi,yanayin su bai nuna sun yadda da maganar da yake musu ko akasin haka.

Da gudu ta faɗa ɗakin tare da ƙanƙamre Mama ta na wani irin kuka." Mama duniya ta min zafi! Ina jin wani irin baƙin ciki a cikin zuciyata,wallahi nafi buƙatar mutuwa fiye da rayuwata! Wai me na yi wa Baba Sani ya tsane ni haka!Gara ya kashe ni da ɗacin da yake saka ma rayuwata."

Mama ta rungumeta ta na shafa bayan ta don gani take kamar hauka ta yi." Lafiyar ki ɗaya kuwa?Ki yi shiru ki yi min bayanin yadda zan fahimta."

Kusan minti goma ta na kuka ganin ta kasa magana sai ajiyar zuciya take,a ranta ta na jin baƙin cikin rabuwa da masoyinta,don ta san yadda ya aibata ta babu yadda za'ai su yadda ɗan su ya

aureta.

Da ƙyar Mama ta samu ta daina kukan sannan  ta yi mata bayani.Ran Mama ya ɓace sosai ba ta san sanda ta ji jawaye ya na zuba a ƙuncin ta ba." Na gaji da halin da yake min! Zuciyata ta fara gajiya amma ba komai Allah ya fi shi da ikon Allah sai ya yi nadama,akan halin da yake miki."

Sosai Juwairiya take kuka koda Mas'ud iyayensa suka koma gida suka sanar mishi a abin da ya faru,hankalinsa ya tashi matuƙa duk ƙoƙarinsa na ya fahimtar da su,amma sun ƙi ƙarshe wan mahaifinsa ya gyara zama yace." Ko da a ce yarinyar ba halinta bane,to ƙanin mahaifinta ba ya son ya baka ita ka kyale musu yarinya ga ƴan'uwan ka nan sai ka zaɓa a cikin su."

Ransa ya ɓace matuƙa da ma ya ba shi izinin ya turo dangin sa saboda ya faɗa musu haka. Motarsa ya ɗauka sallama ya yi bai ko tsaya Mama ta amsa ba ya faɗa gidan,a yadda ta gan shi ta san ba shi cikin hayyacin sa.

Da sauri Juwairiya ta ruga da gudu don ta saka hijabi ganin ya shigo." Mama ya Baba Sani zai yi haka? Juwairiya ya aiba ta a gaban iyayena. Wai me kuka yi mi shi ya tsane ku?"Ya faɗa yayin da idanunsa suka kawo ruwa.

Cikin jimamin lamarin Mama ta share hawaye ta kalli Mas'ud da ya haɗa kansa da gwiya hawaye na zuba a fuskarsa,sai ya ba ta matuƙar tausayi ta san yadda yake son Juawairiya duk da iyayensa suna da shi amma a haka yake son ta.

Ka yi haƙuri ka san matar mutum kabarin sa Allah be nufi Juwairiya matar ka bace,ka bi zaɓin iyayen ka ni na san duk korar mata masoya da yake in har lokacin ta ya yi bai isa ya hana ba."

" Gaskiya Mama ba zan iya jure rashin Juwairiya ba zan je na sami Baba Sani duk abin da za'a yi sai dai ayi haka kawai ya din ga cusgunawa rayuwarku.Ya katse ta da faɗin hakan ransa a ɓace tare da miƙewa.

" Zo Mas'ud don Allah karka je a yadda ranka yake a ɓace za'ayi ɓatatta,ka san halin shi ba shi da haƙuri ni ce na haifi Juwairiya ina me baka haƙuri ka haƙura da ita,shi kaɗai ne wanda take gani a matsayin na ta in har aka ɓata mishi wa za ta riƙe?Ka yi haƙuri Allah be nufa za ka aure ta ba."

Kawai sai gani ta yi ya saka kuka ya na kallon Juwairiya da ita ma take kuka na tausayin halin da suke ciki." Juwairiya zuciyata za ta shiga cikin wani hali na rashin ki.Ki yi min addu'a Allah ya ba ni mace me irin halin ki,ni na san ke wace ce ko idanunki mutum ya kalla ya san kina da tarbiya da natsuwa.Ina sonki zan haƙura da auren ki saboda umurnin Mama."

Fita ya yi har da gudun sa ya na sharen hawaye Juwairiya ta miƙe da gudu ta shige ɗaki tare da saka kuka.Sam ita ba ta ga dalilin da Mama  za ta hana shi ba,ba ta san me Baba Sani yake

nufi da ita ba shi ya sa take girmama shi,abin da ya sa taƙi ga ya mata ta san duk ranar fa ta gaya mata ƙudirin sa akan ta, ƙila zuciyarta za ta buga domin abin ya yi muni.

Tun daga wannan ranar ba ta ƙara gani Mas'ud ba ko wayar da ya siya mata Mama ƙwacewa ta yi ta ije,don a yadda ta ga take-taken ta za ta iya kiran shi kuma shi ma haka.Tun ta na saka ran ze dawo har ta cire sai dai ta wahala kafin ta cire son shi a ran ta,sannan da ga baya taci gaba da al'amuranta.

Mariya ta sami miji za ta yi aure anan kusa da layin su za ta yi auren don haka su Juwairiya su ne ƴan mata.Su Juwairiya an sha gayu da lalli an yi kyau sosa,ana ta hidimar biki don ba zama an saci ɗan ɓarawo.
Zaune suke ana hirar ƴan mata Juwairiya ta kalli Mariya yadda ta sha kyau yace."Su amarsu kin ganki kuwa,dama komai munin amarya ranar bikinta sai ta haska."

Fari ta yi musu ta na dariya tace." Ku zauna kuna rungume filo ni dai Allah ya hutashshe ni na shige daga ciki,ku tsaya kuna ruwan ida kwayi kwantai."
Wani irin dundu Juwairiya ta duma mata ta nafaɗin." Ji min ƴar baƙin fata wato fatan da kike mana kenan tunna kin shige daga ciki ko? To in sha Allah muna bayan ki."Sauran ƴan matan suka taso mata ita dai Mariya dariya take musu,sannan tace." Ai ke Juwairiya Baba Sani ya hana ki aure da tuni kin haihu ma.Amma ba komai Allah ya na tare dake lokacin ki ne kawai ba yi ba."
Shiru ta yi sai hawaye yayin da mutanen ɗakin suke ta ba ta baki.
A haka suka sha bikin Mariya aka kaita ɗakin ganin Juwairiya za ta tafi ta kama ta tare da saka kuka.Sai kuma ta ba Juwairiya tausayi ta rungumeta ta na share mata hawaye.

Mariya ta share hawaye tace." Maganar da mukai dake akan aikin nan kije Allah za kiji daɗi kin ga ni na yi aiki da su."Juwairiya tace." Ke ni raba ni da aikin nan don na yisu amma ban ji da daɗi ba."
" Allah ki gwada wannan kin ga yanayin halin da kuke ciki,ga shan maganin Mama dole kina buƙatar kuɗi."
" To zan shawarci Mama duk abin da tace sai na je."Da wannan Juwairiya ta tafi gida cike da kewar ƙawarta wacce ta temaka mata.

Koda ta yi ma Mama magana shiru ta yi zuwa can tace." An ya zan barki kiyi aikin nan nifa tsoro nake yi kina ganin rashin mutuncin da Hajiya Binta ta yi miki,amma tuna kin ce Mariya tace ta na da mutunci sai ki je Allah ya tsare ki."

Numfashi ta saki tace." To bari na gwada mu gani."

Juwairiya ta fara aikin cikin jin daɗi ga karatu da take samu ake yi wa yaran lesson da islamiya matar ma ba ruwanta.

Watan ta biyu a gidan ranar ta kammal aikin ta za ta tafi matar tace." Don Allah Juwairiya ki

tsaya zamu je gidan biki ni da yarana,zuwa yamma zamu dawo sai ki tafi in kuma na yi dare zan kaiki a mota."

Duk a ranta ba ta so ba amma sai ta amsa da."  To." Ta koma ta zauna yayin da ita kuma ta shirya da yaranta suka fita.

Tun da suka tafi har aka kira sallah ba ta dawo ba,ranta ya fara ɓaci don ba ta son ta yi dare kar Baba Sani ya dawo ya kuma ƙara mata wani sharrin.

Jin ƙarar mota sai ta yi maza ta leƙa ta windo ta na tunanin ita ce,sai dai cikin takaici ta koma ta zauna ganin mijinta ne ya dawo.
Ya shigo da sallama ya amsa ya na kallonta." Juwairiya har yanzu ba ki tafi ba?"Ya tambayeta ya na kallonta." Eh tunna ka dawo bari na tafi "
" No ki kira ta nima ƙara fita zan yi."
Don takaici ko amsa mishi ba ta yi ba to me ya dawo da shi koma wa ta yi ta zauna.

Ya shiga cikin ɗakin sa mintina biyar ya fito sai kawai Juwairiya taga ya yi kanta gadan-gadan! Da sauri ta miƙe tare da saka salati dai-dai lokacin da ya fisgota ya haɗa ta da jikin sa da ƙarfi.

Kasancewar shi namiji me jiki da ƙarfi ya yi nasarar kayar da ita ƙasa tare da yi mata rumfa,yayin da dabbe ya kaure ko kaɗan ba ta yi tsammanin ya na da wannan halin ba.Kuka ta saka ta na rokon shi,amma bai kula ta ba yaci gaba da ƙoƙarin ida nufin shi.

" Inna lillahi Faruk!Me zan gani dama amanata kuke ci?"Ta furta cikin ƙaraji! yayin da ta yo kan juwairiya ta hau ta da bugu.

Juwairiya ta yi kuka ta yi ihu ji take kamar numfashinta zai fita domin kanta ta hau ga ta da ƙiba,da ƙyar ya samu ya ɓamɓare Juwairiya ta samu ta gudu.

Da ƙyar ta samu ta isa gida ta na kuka a ranar ta rantse ba za ta ƙara yin aiki ba,ko da mutuwa za su yi yadda ta shigo Mama ta tsorata.

Bayan ta yi mata bayani tana  kuka Mama sai da ta zubar mata da hawaye ganin halin da take ciki.A ƙalla sai da ta yi sati ta na jinyar jikinta don har sai da ta kwanta ciwo.

Haka rayuwa take tafiya musu yau baƙi gobe tsummma ga ciwon Mama ya yi tsanani.Wani abin ƙarin tashin hankali Ibrahim da dama can ba lafiyayye bane,saboda sikila ne shi jikin sa da ya yi sauki amma a cikin kwana biyun nan jikin ya tashi.

Ciwon shi sai yake son ya danne na Mama amma duk wanda ya ganta ya san ta na cikin tsananin ciwo.Ga kuma Baba Sani da ya sanar da Juwairiya ya yi mata miji wato Alhaji Tanimu.

A ranar da Baba Sani ya gaya mata sumewa ƙau ta yi don ya tabbata Baba Sani ba ya

ƙaunarta,don ita da ya aura mata shi gara ta zauna ba aure ko ace mutuwa ta yi.

Waye a faɗin garin be san Alhaji Tanimu ba wanda ya mai da mace tamkar rigar sawan shi.Mutum ne mara addini ga shi kamar wani hor.Kusan duk shekara yake sakin mace ya ƙara aure bayan ya tabbatar sun sami ciki,don baya son haihuwa a tunanin ta shi kan shi be san iya yawan yaran shi ba,duk da wasu ya na ba ma iyayensu mata kyauta wasu kuma ya kai su almajiranci.

Sannan an sha kama shi ƴara ƙanana ya na musu ya lalata musu rayuwa irin mutumin da Baba Sani yake son ya zama mijinta kenan.Ai Juwairiya ƙaramin hauka ta yi don gara yace ta shiga duniya.

Shiko Alhaji Tanimu se ɗinkirama Baba Sani kuɗi yake yi hankalinsa kwance ganin zai mallaki wannnan zuƙeƙiyar,shi ya sa be damu ba ko sanda ya zo zance taƙi fitowa tallar ta fa aka kawo mishi har gida.

Rayuwa a wannan karan tafi yi wa su Juwairiya illah ga aba abinci sannan dukkanin su ba lafiya,ga Baba Sani da yake ta shirye-shiryen bikin ta don har an kawo kayan sa rana watan gobe biki.

Mama ta shiga tashin hankalin ciwonta ya ninku ga yunwa har takai sai su wuni ba su saka komai a bakin su ba.
Juwairiya ta tsara ma kanta ta gudu amma in ta ga halin da su Mama suke ciki sai ta ji kamar ta kashe kanta ta huta,ita kanta ba lafiya take da shi ba don ta na ganin har tafi su Mama jigatuwa saboda zuciyarta da take ji kamar za ta fashe.

Ganin yunwa zai kashe su sannan duk kuɗin da Baba Sani yake karɓa bai ta ba ba su koda na sabulu ba,ta je gurin Mariya ta ara mata naira dubu biyu ta fara jarin gyada.Da wannan suke samun abinci.

*******
Zaune yake cikin damuwa sai kuma ya miƙe don a yau jin sa yake duk shawarar da amininsa ya ba shi zai iya ɗauka saboda halin da yake ciki.Makullin motar shi ya ɗauka ya nufi gidan A.k. Sai dai cikin rashin sa'a ba ya nan don haka bayan sun gaisa ya fice daga gidan ya samu wani guri mara hayaniya ya tsaya,tare da ciro waya ya kira A.k.

Ba'a fi minti goma ba sai ga A.k akan mashin ya sauka ya buɗe gaban motar ya shiga ya na share zufa."Am sorry aboki motar da ka siya min na kai ta service ba'a gama ba kan dole na baro motar na hawo mashin.Are you under  the weather?"Ya tambayi aminnin nasa ganin yanayin sa.

Yace ya na kallonsa bai tanka ba illa ajiyar zuciya da ya yi ya kauda kansa gefe guda,ganin yadda aminin na sa yake ya san yauma ba lafiya to ko dame yazo oho don ya san dai zancen.

Suka ɗan yi shiru ba tare sun ce uffan ba na tsawon lokaci sannan A.k ya katse shirun da cewa." Lafiya na gan ka wani iri in ce ba mutuniyar bace ta haɗa maka zafi."

"Akan maganar da na nemi shawarar ka yau ma na ƙara bijiro maka da ita.I really need your advise pleese help me out."A.k ya kalle shi yadda idanunsa suka kaɗa suk yi ja ga mamakin sa sai ya ga hawaye ya na sauka da ga ƙuncinsa.
Ya kama hannunsa ya haɗa da nasa ya riƙe sosai ya na kallonsa ya ci ga ba da cewa."I know my wife she is a woman of raging jealousy.Bazan iya haɗa ta da wata mace ba kuma ba yan haka na yi mata alƙawari,amma ina jin zafin rashin yaro da ba ni da shi wanda hakan in ban ɗauki mataki ba zai iya taɓa lafiya ta,domin a yanzu ya kai matsayin da ba na iya bacci.

Tun da ya fara magana A.m ya yi shiru ya na kallon sa a ransa tunani yake to ko amininasa ya ci kai ne ko kuma rashin haihuwar ya taɓa tunanin sa, kamar yadda yace shi dai ya san ta aure ake samun haihuwa ya ba, shi shawara yaƙi bi saboda wani alƙawari na shi na banza to amma bari ya ji me yake tafe da shi.

Ganin ya yi shiru ya dafa kafaɗarsa ya na cewa."Try to be patient  ka san zuriya kake buƙata kuma dole a aure za ka same shi,ba zaka so ka sami ɗanka ta zina ba wanda na san ba halinka bane,amma ni banga dalilin da zai sa kaƙi ƙara aure ba bai ita ta ɓata mahaifinta da kanta ba?"Ya ɗan faɗa da zafi kuma da tsigar tambaya.
" Haka ne." Ya ba shi amsa sannan ya ci gaba da cewa." Duk akai na ne ta samu wannan matsalar gaskiya i can't make up my mind ko zan iya cin amanarta."

Ƙarin takaici maganganunsa suka ƙara ba shi gani yake ba shi da tsayuwa a gidan sa,amma shi bai ga yadda matar shi zai ta  da hankalin shi ba,don kawai zai ƙara aure kuma duk laifin tane. Ya kaɗa kafaɗunsa yace."It is up to you ni dai na gama baka shawara."Yace amma sai kuma ya ga hankalin aminin nasa ba shi a gurinsa wataƙila ma be san me yace ba.

A hankali ya bi gurin da yake kallo shima  Juwairiya ce da tiren gyaɗa a kanta da ga ganinta ka san ta na cikin wani hali, kusan ma ta na tafe ta na share hawaye saboda har Alhaji Tanimu ya kawo kayan auren ta na jin gara ta haƙura ta aure shi,wataƙila shi Allah ya tsara ya zamo mijinta ta san bawa ba ya wuce abin da Allah ya tsara mata,sai dai yanayin halin da Mama da Ibrahim suke ciki ya sa ta zagaya wa da gyaɗar da yau ba ciniki ta haɗa da kuɗin da Mariya ta ba ta ta kai su asibiti.

A.m da ya zuba mata ido ya na kallonta bai taɓa ganin mace me sanyi da wani irin shauki a tare da ita ba sau,haka kawai ya ji ta kwanta mishi a rai ba wai son ya na son ta ba irin zai iya magana da ita har ya ba ta lokaci su yi wasa da dariya,kuma ya nemi shawarar ta kuma zai iya yin komai don ta yi farin ciki,zai iya cewa yau ne rana ta farko da ya ga wata mace bayan Zainab har ya na jin zai iya mata magana.

Wato in ya fahimci zuciyar shi ƙawa yake son ya mai da ita ko ƙanwa." To amma duk tsanar talaka da na yi sai ace na yi ƙawa da ƴar talaka kuma ƙasƙantacciya ƴar talla kai an ya da

wuya.".
Yace a zuciyar a cikin zuciyarsa ya na me ƙoƙarin kauda idanun sa daga gareta don jin hakan bai dace ba ace duk matsayin shi.Sai-dai idanunsa sun kasa ɗauke kan su daga kallonta ya na ƙara zaƙulo kyawunta.

Ta na tafe cike da damuwa har tazo ta gaban su za ta wuce." Me gyaɗa." Kalmar da bakinsa ya furta ba tare da ya ba shi umurni ko tunanin hakan ba.

Juwairiya ta ji wani irin sansanyar murya mai kama da sarewa ta kira ta ta na son ta juya amma sai ta daƙile kanta da juyawar,don ƙila in ta ga mamallakin wannan muryar ba ta san halin da za ta shiga ba sai kawai ta ci gaba da tafiya yayin da aranta take addu'ar Allah ya sa karya ƙara kiranta, don ta san in ya ƙara kiran ta ba za ta iya tursasa zuciyar ta da ƙin juyawa ba.
A.m ransa ya matuƙar ɓaci ƙazama da ita ta na talaka zai kira ta taƙi waigowa ya so yaje ya yi watsi da kayan tallar,ya ga uban wa take taƙama da shi taƙi amsa kiransa amma da ya yi tunanin ko kurma ce sai ƙara kiran ta a karo na biyu.
Cak! ta tsaya amma ba ta wai go ba ta na addu'a a cikin ranta yayin da idanuwanta suka zaƙu da suga wannan mamallakin muryar.A hankali ta tako ta iso gun motar su ta tsaya ta kasa magana kuma ta kasa ɗaga ido ta kalle shi.
Kusan minti goma ta na tsaye ba tare da ya kalleta ba me ya gani oho ganin ita ma ba ta da ninyar ta yi mishi magana kuma ba ta tafi ba A.k dai ya na zaune ya na kallon ikon Allah.

A.m ya buɗe motar da nufin ya yi mata wulaƙanci dai-dai lokacin da idanuwan su suka tsarƙe da na juna.
Kyansa yanayin jikinsa idanuwansa  da yadda yake kallonta suka ruɗa ta ta yi kamar za ta faɗi, amma sai ta dafa jikin motar sa ta na kallon shi cikin wani irin shauki,lokaci guda ta ji abu me kama da guduma ya sauka akanta! Yayin da wani irin shokin na soyaryarsa suka dinga ɗana mata son shi a cikin ranta,har ta ji za ta iya mutuwa in ba ta same shi ba.

Idanun su da suka tsarƙe da juna sai ya tsinci kansa da kasa mata rashin mutuncin da ya yi ninya a yatsine yace."Nawa-nawa gyaɗar."
Ta zuba mishi idanunta sai kuma ta janye ta lumshe su tare da kauda ganin ta gare shi ahankali da sanyaryar murya tace.Hamsin gwagwani ɗaya."
Ya ɗan ƙura mata ido haka kawai kyawunta da muryarta yake ruɗan shi a kanta."Duka buhun nake so nawa."Yace tare da barin kallonta lokacin da ta ɗora idanunta akan sa.
Zare ido ta yi " kwai yawa fa kusan na dubu uku da ɗari biyar ne.Tace mishi hakan sai ya burge shi ya tsinci kansa da yin murmushi.
"Ok bari in ci Allah ya sa da daɗi."Da sauri ta saka hannunta da baya rabo da lalli ta miƙa mishi ta na faɗin." A kwai daɗi kaci kaji."
Yabi hannunta da kallo ya karɓi gyaɗar ya ɓare tare da taunawa,lumshe idanunsa ya yi yace da ita."Gaskiya a kwai daɗi zuba min a leda sauran kiyi sadaka da shi."
Da sauri ta zuba mishi sannan ta kalli gefen A k da ya yi mutuwar zaune saboda tun tarihin rayuwarsa da A.m yau ce rana ta farko da ya siyi abu a gurin masu talla,sai ya yi lakato ya na kallon A.m da ke cin gyaɗa har ya na faɗin ta ƙara mishi ya yi daɗi.

" Yayana kai fa ba ya cine."Ta kalle shi sai kuma ta mai da maganar da tsigar tambaya ta na kallon A.m,kaɗa kafaɗunsa ya yi ya na kallon shi ya ma manta da shi yace."Ba ya ci."
Juwairiya tace " Ka tambaye shi ne?"Sai kuma ta kalli A.k tace."Wai haka Yayana?"
"Yes Am ok."Yace da ita ya na kallonta.
Zuba gyaɗar ta yi ta miƙa mishi ta na faɗin."Kaci a kwai daɗi."Ya ƙarɓa tare da faɗin."Thanks sis."
A.m ya zaro kuɗi da yawa ya miƙa mata. Gashi sis ki cire kuɗin ki sauran ki ƙara jari."Zare kuɗin ta ta yi tace."Siyan da ka yi na gode."
Hakan sa ya yi matuƙar birge shi ya na ta kallonta har ta yi nisa ya leƙo ta cikin murfin motar yace." Manene sunan ki."
Ya ɗan ɗaga muryarsa yadda za ta ji don ta yi nisa,waigowa ta yi ta kalle shi tare da sakar masa murmushi ta tabbata wannan kyakykywa gayen ya yi mata sata mafi girman abu a rayuwarta,wanda ta san ba zai dawo mata da shi ba kawai za ta ci gaba da renon giɓin rashin abin da ya ɗauke mata har iya tsawon rayuwarta!
" Sunana Juwairiya Ahmad."Tace tare da ƙoƙarin ɓullewa a ranta ba ta son ta ƙara haɗuwa da shi don ta san babban goro sai magogin ƙarfe.
A hankali ya kwantar da kan shi akan jikin kujerar da ya saukar da kansa ya na murmushi ya furta.Juwairaaah! Da wata irin murya ya ja sunan ya yi mishi wasali sosai." Ta na da kyau haka kawai sai na ji ta burge ni."

Ba tare da wani shakku ba A m yace."Bayan kyau a kwai hankali da natsuwa .Rayuwarta a kwai tarin tausayi ka aureta kawai ta haifa maka yara.

Da sauri A.m ya buɗe idonsa ya ɗora akansa wani irin ɓacin rai da takaici ta ya ya zai haɗa shi da ita ƴar talaka me talla ita yake nufin ta haifa mi shi yara!Ina imposible wasa yake yi.

Ya buɗe baki zai yi magana sai kuma ya figi motar tamkar zai zubar da su,A.k dai bai ce komai ba koma kashe su zai yi, ya yi amma iyakan shawarar da zai iya ba shi kenan kuma in dai bai ɗauka ba to ba zai ƙara kula shi akan damuwar sa.

Ƙofar gidansa ya ije shi ba tare da yace komai ba bayan ya fito daga motar ya leƙa ta tagar motar yace.Allah ya bamu alkhairi ka yi tunani shawarar da aka yanke ina sauraranka."
Ba tare da ya tanka mishi ba ya ja motar a guje dariya ya saki tare da girgiza kan shi ya shige gidan sa.
A.m da ya koma gida sai yaji wani tashin hankali game da maganar da ya yi mishi,amma ya kasa amincewa wanka ya yi ya kwanta don baya so ya yi tunani akan maganar,sai dai bayan baccin ya kwashe shi sai ya yi mafarkin ga Juwairiya ta na kuka ta miƙo mishi yara guda biyu shi kuma ya na cikin ƙaton rami ya fito da ninyar ya ƙarɓa sai ta ɓace ta na wani irin ihu,ihun da ya fargar da shi ya miƙe a zabur! Ya na salati don har yanzu bai daina jin sautin kukan a cikin kunninsa ba.

" Ita za ta haifa min yara amafarkin da na gani kenan amma a kwai matsala.Tabbas matsala babba don ko ni auren ta zan yi cikin sirri ba tare da sanin kowa ba wato auren wucin gadi,na

ƴanta mata rayuwa na ba ta jin daɗi amma mu yi aure na tsawon shekara ɗaya tazo a matsayin me aikin gidana bayan ta samu ciki, na ɗauke ta na kai ta wani gurin in ta haihu na biyata na karbi yarona na kawoma matata masoyiya Zainab."

Tofa masu karatu kun ji A.m abin da yake so.
*Hakan zai yiwu?
*Ta ya ya A.k zai karɓi lamarin shin zai bashi goyan baya kuwa?
*Wani irin aure yake son yi?
*Shin ya zai yi da Baba Sani da ba shi da buri sai dai rayuwar Juwairiya ta wulaƙanta,zai amince mutum me daraja da matsayi ya aureta?
*In ma ya amince taya za'ai Juwairiya ta yi rayuwa a gidansa a ɓoye a matsayin matarsa amma kuma azahiri ƴar aiki?
*Ta ya ya za ayi auren sirri ba tare da sanin Mama ba?
Ku dai biyo ni a shafi na gaba"SAKACINA KO HALIN MAZA"
NAGA RUWAN COMMENT IN ANA SO NA CI GABA.😘😘😘😘😉😉TAKU JAMILA LAWAL ZANGO💔💔💔💔❤️❤️

Follow this link to join my WhatsApp group:
https://chat.whatsapp.com/G0J8rS0cxTtCCC38iwA3B9
*SAKACINA KO HALIN MAZA?*

*RUBUTAWA:-*
*JAMILA LAWAL ZANGO*

*SADAUKARWA GA:-*

*SUMMY M NA'IGE*
_(Aminiya)_

*FIRST CLASS WRITER'S ASSO....*

*SHAFI NA GOMA SHA BIYU*

Juwairiya ta na ɓacewa ganin sa ta tsaya ta tsuguna tare da sakin wani gigitaccen kuka sosai wanda ba ta san dalilin yin hakan ba,sai bayan tasha kuka sosai zuciyarta ta fara jera mata tarin

tambayoyi."

Me ya sa nake kuka ga mutumim da na san ba zan taɓa samun shi a cikin rayuwata,na sa ni cewar dariya ba so ba ne.! Maganar da ya yi min ba ya nufin zai iya sona a cikin ransa,sannan na tabbata ya yi aure har ma da iyali saboda kamalar shi ta nuna na cikakken mutum me iyali."

Ta tallabe fuskarta da hannunta wani sashi na gefen zuciyarta,ya na ƙara jaddada mata da cewar ko da ya nuna ya na sonta Baba Sani ba zai taɓa  ba shi auren ta ba,mutane wanda ba su kai shi matsayi ba sun nemi auren ta amma ya hana bare shi da ga ganinsa kasan ya jiƙu da nera,da duk wani ababen more rayuwa.

Sai ta share hawayenta tare da ɗaukar tiren jiri na jiri ya na iban ta ta na ji kamar ta haɗiye zuciya ta mutu in ta tuna wannan tsohon ze mallaki jikinta.

Gizo-gizon hoton sa da murmushin da ya yi mata lokacin da ya tabbayi sunan ta idanuwanta suke hasko mata,ta rintse idanunta da ƙarfi ta na son su daƙile mata ganin ta ga mutumim da take jin kamar ya saka ta a aljihun sa su yi ta yawo.

Bayan ta dawo gida ta na zaune jingine da bangon ɗakin su idanunta a sama ta na aikin tunanin da ta ɗaura ɗamara da shi tun lokacin da idanunta suka yi tozali da shi.

Mama dake tsaye ta na karantar yanayin ta tun da ta kawo mata kuɗi tace wani mutum ya siye,ta zauna a gurin ta na kallon sama sai hakan ya tabbatar mata da a kwai lauje cikin naɗi.

" Juwairiya lafiyar ki kuwa."Mama ta kalleta lokacin da ta dafa kafaɗarta,amma ba ta ji ta ba har sai da ta maimaita sau biyar ba ta ji ba sai ta juyo da fuskarta.

Ga mamakin ta sai ta ga ta juyo tare da saka hannunta ta rungumeta ta fashe da kuka,hankalin Mama ya ƙara  tashi dama tun safe take jin wani irin zafi-zafi a ƙirjin tare da sauke wani irin ajiyar zuciya mai kama da zai tafi da rayuwarta.
Yaƙe me kama da murmushi ta yi tace." Akan maganar auren ki ko Juwairiya ya za mu yi da ƙaddarar ubangiji,komai kika ga ya faru Allah ne ya ƙaddara."

Ta sauke irin wannan ajiyar zuciyar da ke barazanar ɗauke numfashin ta sai kuma hawaye suka fara turereniya a kan ƙuncinta.
Ta buɗe baki da nufin ta yi magana amma ta kasa sai ta rufe bakin tare da sakin kuka wanda ya fi na Juwairiya sauti.

Hankalin Juawairiya ya tashi matuƙa!Tun da lamarin ke faruwa Mama ita take kwantar mata da hankali amma yau haƙurin ta ya gaza.

" Don Allah ki de na kuka wallahi na haƙura ba zan ƙara nuna damuwata ba,in dai akan auren nan ne kin san yanayin ciwon ki.

Ta faɗa ta na share hawayen ta don ta na tsoron kar ciwon Mama ya tashi,ga shi aure za ta yi babu wanda zai kula da ita sai Ibrahim wanda ba cikakkiyar lafiya gare shi ba,don har ɗingishi yake yi kafar sa ɗaya ba lafiya.

Mama ta miƙe ba tare da tace komai ba ta fice daga ɗakin ta na jin matuƙar tausayin ta kasancewar ba ta sami bango abin jingina ba.Tanimu ba mutumim aure ba ne ita kuma mace ta na zama zinariya ce in har ta samu miji na gari,ta fauwala ma Allah lamuran sa saboda Allah na iya can za lamuran sa iya addu'ar da take yi wa Juwairiya rayuwar ta ba za ta taɓe ba.

Buta ta ɗauka ta shiga bayi ta tsarkake kanta ta fara kai kukan ta ga Allah Sarki gwani gagara misali!

Ganin haka Juwairiya ta miƙe tare da sakin kuka ta toshe bakin ta bayi ta shige ta saki bakinta ta na kuka mai tsuma zuciyar me sauraro." Me ya sa ka shigo rayuwata a lokacin da nake jin duniya ba ta da muradina a cikin ta gyambo biyu kake so na yi ta jinya a cikin rayuwata! Na rashin ka da auren mutumim da na tsana a rayuwata!"Kuka sosai ta yi sannan ta fito ta yi alwala tabi sahun Mama.

Wunin ranar ta yi shi ne a suku-suku tamkar wacce ba ta da lakka a jikinta,ta kasa cire shi a ranta.Da daddare ta na kwance sai mutsu-mutsu take ta na jin Mama na ajiyar zuciya ƙut!Ƙut! Wanda hankalinta ya tashi kwarai ba ta rintsa ba sai kusan asuba ta ji ɓarawo bacci ya kwashe ta.

Da asuba bayan ta yi sallah ta na karatun alkur'ani ta yi mamakin da Mama ba ta tashi ta yi sallah ba,sai ta miƙe dai-dai lokacin da Ibrahim ya shigo ya dawo daga masallacin dake kusa da su.

" Mama ki tashi ki yi sallah." Amma shiru ba ta amsa mata ba da sauri ta ƙara jijjigata sai dai ta ga Mama idanunta sun ƙanƙance jikinta ya saki da ƙyar take janyo numfashin dake barazanar kuɓucewa gangar jikin ta.

" A'a Mama don Allah karki mutu ki bar mu kin ji Mama!"Kuka take sosai ta na girgiza Mama da ta ƙasa buɗe idanun ta saboda nauyin da sukai mata,a jikin ta ta na jin wani irin zafi me kama da rushi ya na zagaye ilahirin jikinta don har huci yake ya na fitar da tiriri me zafin gaske!

Jin ihun Juwairiya ya sa matar Baba Sani ta shigo wanda hankalinta ya tashi matuƙa ta na tausayin su sosai,sai dai ta san halin tijararren mijinta zai iya shuka mata rashin mutunci koma ya sake ta bare yanzu da yake mata rashin mutunci zai ƙara aure.

Kuɗi ta miƙa ma Juwairiya ta saka yaron ta ya nemo me keke napep aka saka Mama a ciki zuwa asibiti.

*********

Bayan A.m ya fita gidan iyayen shi ya nufa don ya ɗan kwana biyu be leƙa su ba,ya na shiga ya ga ana ta murnar matar ƙaninsa ta haifi ƴan biyu gidan ya cika sai murna ake,saboda daga asibiti nan aka wuto da ita.

Jikinsa ya yi sanyi ya irga yaransa yanzu huɗu kenan sai kawai ya ji zuciyar sa na bugawa,bai ƙara shiga cikin tashin hankali ba sai da aka ɗora masa yaran masu kama da larabawa a kan cinyarsa.

Gidan gabaki ɗaya sun ruɗe suna ta ɗaukar yaran waya kamar zasu ƙarar da jikin su saboda ɗaukar hoton,har sai da ya tsawatar da su bari sannan suka dena suna ta kallon yaran.

Hawaye yaji suna bin ƙuncinsa ya kasa ɗaukar yaran ya na kallon su gunun sha'awa kamar ya kwace yace ƙwansa ne  shine ya haife su.

Ganin ya na hawaye sai dukannin su jikin su ya yi sanyi suka koma suna rarrashin sa,amma ya kasa tsaida hawayen da ke kwaranya kamar an buɗe famfo.
" Zainab an ya kin yi wa rayuta adalci kuwa?"
Ya tamabayi kansa dai-dai lokacin da mahaifiyar sa ta dafa kafaɗun sa ta na rarrashin sa.Bayan ya sawa yaran albarka ya fice daga gidan kai tsaye kampanin su ya wuce tare da jiran A k su haɗu da shi  farfajiyar kamfanin.

A.k ya sanar mishi ya na kampanin in ya iso ya kira shi kawai,amma sai A.m ya nuna ya fito kawai ya jira shi saboda yanayin da yake ba zai iya ƙara kiran waya ba.

Ya na isowa ya same shi tsaye da waya a hannun sa da alama waya yake sai kuma ganin shi ya sa ya kashe wayar,tare da maida ta cikin gabar rigar sa ya ƙarasa gurin da A.m ya yi parking ɗin motar sa.

Ina ga muje farfajiyar da Daddy yake hutawa abin zai fi ko a bisa mu yi magana don nima ina da maganar da nake son mu tautauna akai."A.k yace da shi bayan ya nufi hanyar gurin ba tare da ya ji amsar da ya ba shi ba.

Ganin haka sai shi ma ya bi bayan sa ba tare da yace komai ba.Bayan sun zauna shirun na su na ƴan mintoci ya biyo baya wanda sai da nabi dindigi na gano dalilin shirun na su a duk lokacin da suka haɗu kafin su fara maganar da ta kawo su,wanda suna yi ne don su sami natsuwa tare da nazarin maganar da zasu tautauna a tsakanin su.

A.k ya buɗe baki da nufin zai fara magana amma sai A.m ya hana shi ta hanyar taran numfashin sa tare da gyara zama yace."Abokina ka fara bani dama na yi magana domin na samo mafita a kan damuwata,na yi tunani sosai kan maganar da muka yi da kai na

Juwairaah.Tabbas yarinyar ta kwanta min a rai kuma na yaba da hankalin ta amma saboda alƙawarin da na yi wa Zainab,kuma ita kaɗai nake son takasance matata zan auri Juwairaah mu yi auren
kwangila da ita shekara ɗaya,kamar yadda ka bani labarin ƙanin mahaifinta ni kuma zan siya shi da ruwan kuɗi ya fasa auren da zai yi mata da wannan tsohon."

Ya numfasa ya na kallon sa ko zai fahimci yadda ya karɓi zancen,amma sa ya ga ya na mishi kallo kamar irin amma ka zare ko!

Bai damu ba ya ƙaɗa kansa yaci gaba da cewa."Tunna ka gaya min ta yawon aikatau sai mu ɗauketa akan za ta koya wa matata girki da kula na tsawon shekara guda,kaga a wannan lakacin in ta samu ciki zan ɗauke ta daga gidan na kai ta wani guri,na san yadda zan tsara Zainab ta amince ta karɓi ɗan burina na ga ɗana kafin na mutu.

"Amma baka da hankali ko na ɗauka alkhairi ya sa ka kira ni nan,ashe ka je ka bugu ne ka zo ka ɓata min lokaci."A.k yace tare da miƙewa yayin kamar zai fice daga gurin bayan ya miƙe sai ya dawo ya ƙara zama ya na kallon sa yace." Aikin banza kawai na ɗauka auren ta za ka yi na ɓata lokaci na gurin sanin tarihin rayuwarta! Abin takaici sai ga shi kazo ka na min maganar banza. Shin baka da zuciya ne a ƙirjinka har ka kasa tausayawa rayuwarta na halin ƙuncin rayuwar da take ciki? Ko ƙyamar talaka da kake yi ne ya sa kake son ka cutar da zuciyar ta.

Ya ƙara miƙewa don ji yake kamar ze rufe shi da duka ya na jin zai iya gaya mishi duk maganar da ta zo bakinsa,saboda tun jiya da ya ji halin da take ciki Allah ya saka mata tsananin tausayinta a ranta.

A.m hannun sa ya kama shi ma sai hawaye ya na faɗin." A tsakanina da ita waye yafi kusanci da kai ina cikin wani hali bani da nufin na cutar da Juwairaah wallahi tsananin son ganin ɗana ya sa nake jin zan iya komai.In har ka amince ka bani goyan baya mukai auren sirri da ita na yi maka alƙawari rayuwar Juwairaah sai ya canza daga talauci zuwa mafi ƙololuwar jin daɗi na rayuwa.Kuma ko banza aurena zai zamo katanga a tsakanin da tsohon mutumim nan,ƙanin mahaifinta da yake takurawa rayuwarta duk haɗuwana da ita zai saka ya dena saka mata ƙahon zuƙa."

" Rufe min baki nace! Shashasha!Kawai ka san yadda zuciyar mace take da rauni kan soyayya.Kai fa namiji ne da ko wace mace za ta yi mafarkin samu,ka na tunanin in ka auri Juwairiya za ta iya haƙuri da rashin ka ne,a kan maganar soyayya kuɗi ba ya tasiri mace za ta iya baka rayuwarta kuma ta sadaukar da rayuwarta duka gabaki ɗaya in har ta na sonka,ba za ta taɓa damuwa da halin rashi ko baƙin cikin da za ka saka taɓa."

Ya saukar da zazzafan huci ya ja numfashi sannan ya kalle shi da idanunsa da suka kaɗa suka yi jajur." Ina tunanin yaudarar Zainab kake da kake faɗin ka na sonta don da ka san yadda

soyayya take tasiri da baka buƙaci auren Juwairiya na wucin gadi ba, don na tabbata kafin ku rabu sai Juwairiya ta faɗa kogin son ka koda yankan namar jikinta kake yi ɗanye,bare kuma za ka raba ta da abu mafi girma a rayuwarta kawai za ka rabu da gangar jikinta ne amma zuciyar da da ruhinta duk za ka raba ta da shi.Ba ka san yadda uwa take zama akan yaron ta ba,saboda ba ka haihu ba shi ya sa baka san soyayyar da Allah ya saka tsakanin ɗa da mahaifi b..."

"Ya ishe ka! Rufe min baki nace banza mara mutunci! Har ni za ka yi ma gorin haihuwa na rantse tunna ka yi min gori sai na aureta kuma na raba ta da yaran na kai ma matata,na yi alƙawarin sai kaga ƙwaina a duniya."

Ya matso tare da taɓa ƙirjin shi da ɗan yatsa yace." Saboda nace zan aure ta ka wani tada jijiyar wuya'duk na gane kauce-kaucen ka don ta na talaka ba ka son na aureta.To siyan ta zan yi da kuɗina kai ma ka san in ka yi tunanin zan aure ta na yi rayuwar har abada ka yaudari kan ka, me zan yi da ƴar talaka wanda basu da komai sai tsiya,kuma ka sani ko ban aure ta ba ina da kuɗin da inna ce zan auri ƴan mata waɗanda suka fi ta kyawu da ɗaukaka zan iya auren goma in ana yi."

"To kaje ka auri ƴan matan duniya duka in kana son ɗan ƙaruna amma ba zan haɗa hannu da kai na saka rayuwar ta a cikin matsala."

Ya faɗa tare da ƙoƙarin barin gurin rigar sa ya jawo ya juyo da shi gaban sa ." Ko ka sa min hannu ko ka ƙi sai na aure ta ita kaɗai ce na ji zan iya rayuwar aure da ita ba yan masoyiyata Zainab,don haka in dai kuɗi na aiki ka ba ni sati biyu za ka gan ta a gidana kuma a matsayin me aikin matata za ta shigo gidan."

Ran sa ya ƙara ɓaci da ya tuna ya sha zuwa gidan ya ga Zainab ta daki me aiki,hakan ya na nufin in ranta ya ɓace za ta dake ta kenan aiko in dai haka ne a kwai zalinci.

" Ai kin banza kawai sai dai in zaka ɗauki numfashina ma'ana ba ni a raye,amma ni da kai na zan tona asirin ka kuma na ga uban da zai karɓar maka auren tunna ba ƴar tsana ba ce,sai da waliyin ka za'a baka.Yace a fusace.

" Ok haka kace ko zan nuna maka true color ɗina dama duk abin da aka haɗa da jaki sai ya ci kara,ka haɗa hulɗa da talaka matsiyaci da be da komai sai tsiya na yi dana sanin tarayyata da kai don bi amfana min komai ba,duk halaccin dana yi maka ni da dangina muka ƴanta rayuwarka shi ne zaka saka min da haka!"

To fa ran A.k ya ɓace matuƙa kawai sai hawaye ya kalli A.m da yake ta ga ya mishi maganganu mara sa daɗi da baƙan ta rai,don shi in dai ran shi ya ɓace bai iya magana ba."

" A she haka kake dama na daɗe ina tunanin wannan ranar za ta zo,saboda a gaba na kasha wulaƙanta talawa irin na na gode in sha Allahu daga yau ba ni bakai,ba zan ƙara hulɗa da kai ba kuma na bar muku aikin ku ka sana ni ba jahili ba ne ko yau na yanke alaƙa da ku sai kun yi jimamin rashina."Yace ya na me tabbatar da hakan a ran sa.

Kai ɗin me kai ɗin banza me kake da shi kaje a kwai waɗanda suka fika ilmi da zasu buƙaci gurbin ka.".
Lamarin fa ya yi tsamari gabaki ɗayan su kowa ya hau dokin zuciya duk da zo mu saɓa zo mu zauna,amma ba su taɓa samun saɓani irin na yau ba.

Ko da A.k ya nufi hanyar fita A.m jawo kwalar rigar sa ya yi tare da dawo da shi ya hau shi,da dambe don gani yake ya ma rai na mishi wayo ya na karkashin sa,sai ya manta abokantakar su ya dawo kan matsayi.

Aiko A.k a zuciye ya kai mishi mari ya kauce shi ma ya kai mishi suka rikice da dambe kici-kici.Me ba ma fulawa ruwa ya zo ya gan su da gudu ya ruga ya yi kiran mutane,su raba don ba zai yi gigin shiga tsakiyar su ba su bar shi da jinya yadda suke ji da karfi.

Da ƙyar mutane suka raba su sai huci suke tamkar wasu zakuna.Faruwar lamarin sai ya yi matuƙar bawa mutane mamaki,tuna yadda suka shaƙu kamar wasu ƴan'uwa suna ta jimamin lamarin me ya haɗu ko ma dai mene ne lamarin me girma ne,amma da suka tuna tsakanin harshe da haƙori ana saɓawa sai suka ba su haƙuri tare da ɗauko musu ruwan sanyi,domin ya sanyaya zuƙatan su saboda sheɗan da ya yi nasara haddasa fitina a tsakani aminnan ko nace ƴan'uwa.

A.k da ran sa ya ɓace ko jiran wanda ya nufi zuwa cikin kampanin ya ɗauko musu ruwa bai yi ba ya fice ya na jin a ran sa ya tafi na har abada.

Ko da a ka ɓalle murfin gorar ruwa aka zuba mishi ruwan wurgi ya yi da kofin tangaras ɗin ya nufi motar sa,ya shige tare da figar ta kamar zai tashi sama.

Ko da ya iso kofar gidan ya shiga sakin hon ba ƙauƙautawa.Allah Sarki Audi direba dake cikin bayi da cikin sa ya murɗa ya shiga kenan ya ji hon wanda ya tabbata matar gidan ne me shegen yawon tsiya,amma da ya tuna ya ga ta fito ɗazu sai ya yi maza ya fito ba tare da ya gama abin da yake ba sai dai hon ɗin da ake saki na rashin hankali.

Ya na wangale get ɗin sai yaga megidan sa ne yake ta zuba wannan hon,hankalin sa ya tashi kwarai don a tunanin sa ba lafiya ba.

Ya na shiga ko parking bai yi ba ya fito ya ƙarasa gurin Audi direba dake mishi sannu ya na son

ya kulle get ɗin ya ruga bayi,don har lokacin cikin sa bai dai na murɗawa ba.

Mari ya zabga mishi." Kai wane irin banza ne matsiyaci kawai gidan ubanka ne da zan ɗauki lokaci ina hon baka amsa min ba? Ko kuɗin da nake biyan ka da shi haƙo su nake!"

"Allah ya baka haƙuri ina bayi ne cikina ya lalace."

Bai saurare shi ba ya shige cikin gidan falo ya shiga gibbiyar ta na kwance a doguwar kujera me cin mutum uku da remote a hannunta ta na kallo.

Ba tare da kallon in da take ba ya shige cikin ɗakinsa ruwa me sanyi ya dinga kwankwaɗa har sai da ya cika cikin sa,amma bai ji zuciyar sa ta dai na tafarfasa ba don ji yake kamar za ta fito.

Ya yi cilli da robar ruwan dai-dai lokacin da ta shigo ta na mishi kallon ko ya taɓu ne? Tsaki ta yi kawai ta fice ta san in ta tambaye shi zai iya gaya mata baƙa ita kuma sai ta rama,don haka ba ta tanka mishi ba ta ɗauki wayar ta dake kan gado ta fice a ran ta ta na faɗin." To wa kuma ya taɓo wannan kububuwan?Ba zan yi mishi magana ba ya ƙare a kaina bari na bari ya huce."Ta koma ta yi kwanciyar ta ta na kallo.

Tofa masu karatu kun dai jin yadda ta kaya game da waɗannan aminan juna.Ku ci gaba da bibiyata na gode da yaba lintafina da kuke.

ƊUBBIN GAISUWA GARE KU SABODA COMMENT ƊIN KU YA NA SAKA NI NISHAƊI.

MAMAN SUDAIS
AISHATU MINNA
FATIMA ZARA JOS
SAHURA NURA RABIN RAINA
NABILA MAMAN SAFWAN
HAMDIYA UMMU ABDULHAKIM

Kar dai ku manta sunan labarin "SAKACINA KO HALIN MAZA" Mu haɗu a shafi noma sha uku.Ga masu buƙatar shiga cikin group ɗina na whatsapp ga numba 08144072423_.

Kuma ƙofa a buɗe take na ƙorafi gyara ko ƙarin bayani ga zakakuran marubuta,har yanzu ni mai koyo ce.
Kar dai ku manta da wannan lintafin sadaukar wa ne ga zaƙauran marubuciya,kuma ƙawata (SUMAYYA NA'IGE) Allah ya ƙara fasaha ya sa ki fi haka,ina alfahari dake a cikin marubuta da irin taimakon da kike bani.

COMMENT,READ FOLLOW AND SHARE.

*SAKACINA KO HALIN MAZA?*

*RUBUTAWA:-*
*JAMILA LAWAL ZANGO*

*SADAUKARWA GA:-*

*SUMMY M NA'IGE*
_(Aminiya)_

*FIRST CLASS WRITER'S ASSO....*

*Page 13*

BISMILLAHIR RAHAMANIR RAHEEM

A.k ya na tuki ya na jin zuciyar sa na wani irin tafasa sai dukan sitiyarin yake ya na tsaki ji yake kamar ya je ya shaƙe shi,ya na ji a ran sa ba zai ƙara hulɗa da shi ba don ya tabbata ba shi da mutunci kuma yau zai mayar mishi da motar da ya siya musu a tare da suka je Dubai.

Da sauri ya taka burki ganin ya na son ya buge wani yaro dake sai da rake a tire,ya yi ƙoƙarin janyo natsuwa don ya samu ya isa gida lafiya saboda da ƙyar yake gani.

Matarsa na zaune ita da yaranta suna assigment sai ganin sa ta yi ya shigo kamar an jeho shi,bai amsa sannu da zuwa da suke mishi ba ya shige ɗakinsa wanda ya ɗaga hankalin ta ta miƙe ba shiri ta bi bayan sa.

Ganin yadda ya haɗe kai da gwiwa ta ɗauka rasuwa a kai don haka jikinta a mace ta ƙarasa gun sa tare da dafa shi.

" Lafiya Baban Najwa in ce ba wani abu mummuna ya faru ba?"

Ta faɗa cikin tsoro ganin yadda idanun sa suka canza sannan ta ƙara cewa." Ka yi haƙuri dama haka duniya take ni dai fatana ba mutuwa akai ba,ko wani mummunan lamari ya faru! Don Allah ka yi magana."
Bai amsa mata ko ɗaya ba ya ɗauki ruwa ya na sha.Ganin haka sai ta janyo jikinta bayan ta ƙara A.c ɗakin ta janyo mishi kofa a ran ta ta na addu'ar Allah ya sa lafiya.

Kimanin rabin awa ya ɗauka a cikin ɗakin sannan ya yi wanka ya fito da duguwar farar jallabiya a jikin sa,gefen ta ya samu guri ya zauna ya na kallon ta da ɗan murmushi a fuskarsa.

Sai hakan ya sanyaya zuciyarta da take ta bugawa ta na tunanin ko wani abu me girma ne ya faru.

Ido ya zura mata bai ce mata komai ba hannunsa ta kama tare da ɗora kanta a kafaɗan sa." Zuciyata ta ku san bugawa da na ga ka shigo a cikin wannan halin."

Shafa gashin kan ta ya yi yace a hankali da muryar da har yanzu a kwai ɗan ɓacin rai a cikin ta." Mun yi faɗa ne da A.m kuma me zafi don har na bar mishi aikin sa,zan kuma mayar mishi da duk wani abu da ya mallaka min."

Ya faɗa ya na furzar da wani irin huci mai zafin gaske.

Kallon sa take da irin ba za ku taɓa canzawa ba duk cewar ta san suna faɗa amma wannan

karan da alamar faɗan ya yi tsamari ganin yadda ransa ya ɓace.

" Me kuma ya ƙara haɗa ku?"

Miƙewa ya yi ya ɗauki wayar sa zai koma ɗaki jin tambayar da ta yi mishi wanda ya ɗaukar ma kan sa wargaza shirin,amma kuma bai gaya mata ba sai yace." Wanann kuma sirri ne a tsakaninmu."

Ya ƙarashe shigewa bayan ya riƙe hannun Farha dake ta nacin ya ɗauke ta tun da ya fito daga ɗaki,ya bar ta a tsaye ta na jinjina wane irin rikicine ya faru a tsakanin su har ya yanke barin aikin.

" Ko ma mene ne su suka sani haba! Suna girma suna cin ƙasa." Tace cike da takaicin halin su sai kuma ta yanke shawarar ta kira Zainab ta tambaye ta sai da wayar ta yi ringin sau ku,sannan ta ɗauka tare da sakin wawan ajiyar zuciya.

" Hello sahiba ki yi haƙuri ina falo na bar wayar a cikin na manta da ita,sai da Atine me aiki ta kawo min.Ina yarana?"

Ajiyar zuciya ta yi tace " Ba komai wallahi suna lafiya dama na kira ki na tambaye ki ko A.m ya na nan,na ga aminin na sa ya shigo kamar sun sami saɓani hankalina a tashe yake."

Tsaki ta yi ta taɓe baki." Humh ke kika kula shi ni nawa da ya shigo ko kallon sa ban yi ba,na kyale shi don ba na son ya haɗa min zafi saboda ni ma a cike na ke da wata da ta yi min rashin mutunci a tiktok."Ta ba ta amsa ta yamutsa fuska.

"Zainab!Wai ke ba zaki dai na yin rawa a tiktok ba! A da baki aure amma yanzu ke matar aure ce hakan bai dace dake ba,kin ci sa'a shi A.m sam ba ya yin tiktok amma in Allah ya so ya kama ki sai kiga wani ya tura mishi kuma ba zai ji daɗi ba."

" Umh ke ni kyale ni lokacina ne kin san iya yawan adadin mutanen da suke bibiyata,so kike na yi asaran mutanen da suke zuzuta kyawuna?Ai in kika ga na dai na ƙila na mutu ne."

" To Allah ya shirye ki da masu hali irin naki a matsayin ki na matar aure ji je kina bayyana surar ki ɗora waƙa ki nabi don kawai ki yi suna ko burge mutane,ba yan kin san haramun ne a addini kuma bayan haka malamin ahalari yace.Wal mar'atu kulliha aurati ma adal wajha wal kaffaini.Wato ita mace dukkannin ta al'aura ce sai dai fuska da tafukan hannaye. Gaskiya ya..."

" Wash Allah na! Wallahi Maman Najwa kin cika cika mutum wannan dalilin ya sa ban cika zuwa

gidan ki ba.Ke kullum sai kin yi ma mutum wa'azi,ke da uztazi kika aura sai kin addabi mutum da wa'azi ina ga ko sallah mutum ya yi zaki ce ba dai-dai bane." Ta ɗan numfasa ko za ta ce wani abu sai ta ɗora da cewa jin ta yi shiru ajiyar zuciya ta sauke.

"In kin kira ni ne ki yi min wa'azi ba ni da buƙata matar liman sai kije masallaci ko in da ake buƙata.Ni ya maganar mu na fara yin sana'ar zuwa waje kin yi mishi bayani."Ta canza maganar don ta gundire ta ita ba ta da wani aki sai na yin wa'azi ita kam ba za ta iya ba,ita dai da ta ga za ta iya kashe rayuwar ta da kuruciyar ta sai ta yi Allah ya ba ta sa'a.

Dariya ta yi jin ta canza maganar tace." Na gaya miki tun ranar ni ba zai barni na fita zuwa wata ƙasa saro kaya ba,gara mu dinga basu kuɗin ko mu yi oder kin san yanzu komai a sauƙaƙe yake."

"Taɓ kin yi makaranta amma kamar baki waye ba ok da ma kina jira ya amince miki ne? Dama ba sana'ar kike so ki fara ba,ai koni da kika ji nace zan yi ba zan gaya mishi ba,sai ya ji na fara ke ranar da na ɗan sako mishi maganar Yayyina suna zuwa waje yin business,bai kalle ni ba yace ai da yake mazan na su mahaukata ne basu san mahimancin iyali ba.Shiru na yi bance komai ba ai sai dai ya ga na ɗaware inna dawo koma me zai faru ya faru Am ready for the conseqeuncy."

A ranta ta na girmama irin halin Zainab wacce sab ba ta tsoron miji ga shi Allah ya yi mijinta da son girma,sai dai bai samu macen da za ta ba shi wannan girma ba aiko za'a sha daru don shi ma ba daga baya ba.

" To shike nan Allah ya sa ki gane ni dai ba zan baki kuɗina ba kar mijin ki ya ji na baki,ni ina daraja aurena ke na lalata miki na ki gara na ba shi ya yi min oder hankalina kwance,sannan ki je ki rarrashe shi ki ji abin da ya haɗa su ko ma bai gaya miki ba don Allah ki ba shi kula kina sakaci da mijinki fa kar wata ta yi miki kwace."

Ta faɗa da tsigar tsokana duk da ta san Zainab yanzu za ta harzuƙo mata da shegen baƙin kishinta amma ta kasa kula da shi.

" Kinga ni ko zamu fara Allah babu wata matsiyaciyar mace da za ta shigo min gida,na kuma riga na gaya miki in ta yi wannan kuskuren to ta tabbata ni ce ajalin ta.Kuma hankalina kwance yake ya yi min alƙawari,wace mace za ta aure shi baya haihuwa ko ni haƙuri nake."

Faɗin likita ba Allah bane Zainab in Allah ya so sai ya haihu domin ubangiji yudabbirul amri ne ya na jujjuya lamaruran sa,don haka ban ji daɗin abin da kika faɗi haka kuma kinga ya na iyakan ƙoƙarin sa.

Zainab sai ta ji wani iri a ranta ta na fatan hakan don yanzu yadda A.m yake son ya haihu har yake zubar da hawaye ta na son ko ɗaya ne ta haifa mishi ita fa ba ta son tara yara.
" Ina fatan haka Allah ya amshi addu'armu sannan da kike cewa na je na rarrashe shi Allah ya sauwaƙe haka kawai kema kin faɗa min don ki tsokane ni ne ko?A kan maganar fita waje ai dama ban miki dole ba.Ni na gaji da wayar nan don takaici kike ƙara min zan shigo gidan ki kawai mu tautauna ki gashe min da yara."

Ta maza ta datse wayar ta na baƙin cikin halin da ƙawarta ta ɗaukar ma kanta saboda ta yi aure sai ta hana ci gaba a rayuwar ta?Tsaki ta yi ta ɗauki wayarta ta ta shige ɗaki zuwa can ta fito ta ci ado kamar wacce za ta gasar kyau,ta ɗauki key ɗin motarta da wayarta ta fice ta na ba za ƙamshi mai sanyaya zuciyar duk wanda ya yi katarin shaƙar shi.

A.m riƙe da waya a hannunsa a cikin haɗaɗɗen ofishin sa sai ya duba numbar A.k da nufin ya kira sai kuma ya yi cilli da wayar a kan duguwar kujerar da ke cikin ofishin.

Ya yi haka yafi sau a ƙirga gabaki ɗaya abubuwa sun rikice mishi a kampanin wanda har Daddy ya fara ƙorafi,ya sani A k wani jigo ne a cikin kampanin amma ransa ya ɓace ya je ya gaya mishi maganganu mara sa daɗi ga shi tun ba'a je ko ina ba ya fara dana sani.

" An ya Juwairaah auren ki alkhairi ne?"Ya faɗa da tsigar tambayar kansa saboda ganin da ya yi kan maganar auren ta kawai ya bata da aminin na sa wanda suka zama kamar ƴan'uwa.

Miƙewa ya yi ya tsaya a windon dake ofishinsa ya na kallon waje ganin Daddy ne da ƙaninsa yake tuƙa shi,ya yi maza ya fice daga ofishin tare da shigewa cikin wani ofis wanda ya san ba za su neme shi acan ba ya kulle kansa.

" Wayyo Allah na! Ya zan yi na san Daddy ya biyo ni ne ganin na ƙi ɗaukar wayarsa ga shi kwana biyu A.k bai zo ba abubuwa duk sun caɓe.

Sai ya yi shahadar kiran wayarsa duk da ya san ba dole ba ne ya ɗauka saboda ya yi fushi tunna  mai tsanani da shi.

ilai kuwa wayar ba ta shiga wanda ya tabbatar mishi da ya yi blocking ɗin layin ne,ɗaga wayar ya yi zai yi jifa da ita sai ya fasa ganin kira ya shigo a ransa ya na addu'ar Allah ya saka shi ne,duk da ya san abu ne mai wuya ya kira shi

Ganin kiran Daddy sai hankalinsa ya tashi ya kai hannu zai kashe bai san sadda hannunsa saboda ruɗewa ya danna masa amsa kira ba har kuma ya saka a amsa kuwa.

"Son lafiyar ka kuwa wai me ke faruwa ne?Rejecting ɗin wayana kake yi are you alright kuwa? Ina A.k wayarsa ba ta shiga lafiya yake mai ya faru tsakanin ku mutane suna ta kirana suna complaining tun shekaranjiya na ɗauka ko bai jin daɗi.Gashi gobe ne tafiyar ku chaina.

Daddy ya fara magana ya na jero mishi tambayoyi cikin tsananin damuwa wanda ya ƙara ta da hankalinsa to mai zai cewa Daddy shi kam ya yi nadama sosai ya san ya na da saurin fushi amma nan da nan yake sauka.

"A.k ya yi fushi sosai dama haka yake da ɗaukar abu gaskiya na shiga ruɗani kawai na haƙura da auren bani da rabon haihuwa ne don ba zan iya karya alƙawarin da na yi ma Zainab ba,ba zan iya rabuwa da ita ba don ina son ta na tabbata duk ranar da na kawo wata mace Zainab za ta yi kisa in kuma ba ta yi ba za ta kashe kanta ko ta rabu da ni,ni kuma ina sonki bazan iya rabuwa dake ba."

Sai kawai ya rintse idanunsa ya na jin wani gulululun baƙin ciki ya tokare shi a maƙogaron sa ya duka ƙasa don jin shi yake zai fadi."Hello ka na ji na a kwai abin da kake ɓoyewa son ban yarda yadda yake girmamani,zai daina zuwa aiki ba maza ka shirya muje gidan sa duk in da kake ka dawo ina jiranka ga shi nazo ofis ɗin ka baka nan."

Muryar Daddy ya katse mishi tunanin sa ya firgita lokacin da ya faɗi haka dama ya san babu wanda zai yi gigin gaya masa sun samu saɓani ne in ba so suke su rasa aikin suba.

" Um um Daddy ba ni kusa na fita a mashin zan karɓo tsako bari na dawo sai muje."

" Ok duk ma in da kake yanzu ka yi maza ka dawo."

Daddy ya ba shi umurni tare da katse wayar sa ya bi wayar da kallo ya san dai a kwai abin da ya haɗa su,amma haka kawai A.k ba zai ƙi zuwa gurin aiki ba sanin sa mai ƙwazo da kiyaye halalin sa.

Kamar an ce ɗaga labule sai ya hangi A.m ya zura da gudu ya na sanɗa ya fice daga kampanin kamar wani ɓarawo,kamar yadda mutane suka tsaya suna mamakin haka tare da tunanin lafiyarsa kuwa Daddy sai abin ya ba shi dariya ya kira Mudassir ya nuna mishi shi,dai-dai lokacin da ya fice da gudu har ya na buge kai da get.

Dariya suka ƙara kwashewa da shi." Wai me ke damun son ne ya canza kwana biyu."Daddy yace ya na kallon Mudassir shiru ya yi kawai don ba za'a ji mutuwar Sarki bakin shi ba.

Yafi kusan rabin awa in yakai hannu zai ƙwaƙwasa gidan sai ya janye ya kai ma iska naushi ya na jin tsananin nadamar abin da ya yi masa.

" A'a yallaɓai kai ne a tsaye."

Megadin gidan da ya fito da ninyar ya siyo abu a shago ya gansa tsaye.Jikinsa ya hau rawa don shi bai ji ya ƙwanƙwasa kofar ba ya san zai sha faɗa." Don Allah ka yi haƙuri wallahi ban ji ja ba kuma ba bacci nake ba."

Ganin ya gigice sai ya buɗe baki a wahalce yace." Karka damu yanzu na zo."A taƙaice ya haɗa kalmomin don baya son magana.

" To shigo zan ɗan siyo a bu a shago ne."
Yace ya na waigen in da yabar motarsa amma ganin bai gan ta ba ya wuce abin sa.

A hankali yake taku zuwa cikin gidan ya na isa kofar shiga falo ya ga an buɗe ƙoda tun kafin ya ƙwanƙwasa,matar A.k ne ta na dariya." Hangoka na yi na Zey."Tace masa da masa.

" Uhumh kawai yace ya ƙara sa ciki ya zauna."Ina mijin ki na yi mishi laifi don Allah ki ba shi haƙuri tun kafin ya fito duk da na san ba dole ba ne ya fito."Yace mata cikin damuwa.

" Oh wannan tsakanin ku ne ya dai kama ta ku din ga haƙuri kun girma fa shi ma tun da lamarin ya faru yake ta huci na ba shi haƙuri amma yaƙi."

Tace sannan ta miƙe ta nufi ɗakinsa ba ta jima ba ta dawo fuskarta babu walwala na ƙin zuwa da ya yi duk irin haɗa shi da Allah da ta yi kan ya gane kuran sa.Bayan fitar ta ne A.k ya rintse idanun sa ya na jin ɗacin abin da ya faru tsakaninsu shi da Allah yake son shi ba wai don kuɗin sa ba,amma haka A.m ya rufe idanunsa ya na gaya masa baƙaƙen maganganu kuma sab ba zai goya mishi baya akan abin da yake so ba.

A.m ya canza fuska tun da ta gaya mishi bai ce da ita komai ba idanunsa a rintse ya miƙe tamkar wanda ƙwai ya fashe mawa a ciki ya fice ba tare da yace komai ba,abin da ya sa ya zo tsoro yake kar A.k ya gaya ma Daddy abin da ke faruwa kawai ya haƙura,amma tun da yaƙi fitowa bari ya ɗauko Daddy koma me zai faru ya faru.

Da ya koma hankalin Daddy ya tashi ganin yadda ya ɗan faɗa tsakanin kwana biyu,dafa kafaɗarsa ya yi." Ka na cikin damuwa lafiya wai me faruwa ne?Ina A.k ɗin?"

Ya jera masa tarin tambayoyi a tare ya shaƙi numfashi ya fesar sai kawai ya kwanta akan kafaɗar Daddy cikin muryar kuka ya na hawaye yace." Daddy A.k ya yi fushi da ni mun ɗan sami saɓani ne saboda wata ƴar matsala kuma na je gidan sa na ba shi haƙuri,ni na janye wannan maganar amma yaƙi saurarata har ya ije aiki.Daddy shi ne ya ɓata min rai na kasa riƙe kaina na faɗa mishi baƙaƙen maganganu, amma na yi nadama  sai dai ya datse layina layika na ba ya son magana da ni."

Sai ya sa kuka kawai hankalin Daddy ya ƙara tashi yau shagwabar ta tashi kenan.

Miƙewa ya yi." Oya tashi muje gidan na sa amma ba ka kyauta ba duk da tsaƙanin harshe da haƙori ana saɓawa,nan gaba ka kiyayye ba'a ɓata ma wanda yake kusanci da kai sosai in ma hakan ta faru ƙoƙari ake a riƙe fushi don dole zaku ne mi juna."

Daddy yace ya na shafa bayan sa." Gaskiya ne Daddy na ba shi haƙuri fa kuma na yi nadama.

A lokacin da suka isa gidan da matar shi ta shiga da nufin ta gaya masa,har ya ji muryar Daddy a falo da sauri ya zo ya durkusa ya na faɗin." Da kan ka Daddy ai da ka sanar min ni zan zo."

" Ta ina zan sanar maka bayan ka kashe wayarka.Son ya yi laifi a yafe mishi don kawai kun samu saɓani za ka dai na zuwa aiki, in ka ƙara hakan zan hukuntaka ta hanyar turaka ƙasar waje ka yi wata biyu ba tare da ka dawo gurin iyalin ka ba,saboda ka ɓata min rai kuma na yi fushi da kai."

Jin abin da ya faɗa da sauri maman Najwa ta miƙe tare da ficewa ko gaisuwar da ta tsaya ta yi ma Daddy ba ta yi ba,don ya ba ta kunya duk da ta san in ya yi hakan ya cutar da rayuwar masoya.

" Ka yi haƙuri Daddy na yi nadama hakan ba zai ƙara faruwa ba! Da ma A.m ɗin ne ya...."

" Daddy ya yi haƙuri kawai ya koma aikin sa ni nama haƙura akan maganar da muka yi na fasa na janye."

Yace da sauri ya na kallon A.k don ya tsorata ya ɗauka gaya ma Daddy zai yi.Daddy ya kalle su duka kamar a kwai abin da suke ɓoye mishi wanda shi ne ya kawo musabbabin faɗan.

" To wai me ya kawo rikicin?"

Ai kafin ya rufe bakinsa A.m yace."Daddy ba komai ai mun shirya ya wuce."

A.k dai bai ce komai ba Daddy ya kama hannunsa ya haɗa." Kar na ƙara jin kun yi faɗa ku yi min alƙawari."

"Hakan ba zai ƙara faruwa ba Daddy komai ya wuce."Kamar sun haɗa baki don a tare suka faɗa. " Ok ka shirya ka taho aiki dama ina son na ƙara maka girma."

A ranar dai ba wata magana na amininai da ya shiga tsakanin su,amma tare suka fita zuwa aikin sai dai A.k ko zuwa su tafi cin abinci kamar yadda suka saba bai yi ba,don har yanzu ya na jin haushin abin da ya yi mishi hakan ya sa yake yin azumi don ya rage mishi fushinsa tunna ko Allah muna mishi laifi kuma ya yafe,amma shi mutum ne wanda ya san mahimmancin kansa.

Ƙin zuwa su je suci abinci hakan ya tabbatar ma A.m bai huce ba sai da ya daidaici ya gama tarin aiyukansa da ya jibga ma kansa,ya shiga ya na zaune a kan kujerar ofishin ya rintse idanun shi wataƙila bacci yake.

Shigar shi ya farkar da shi ya tashi ya zauna." Don Allah ka yi haƙuri haba na san ina da fushi,amma ba ni da riƙo na lura kafi son Juwairiya da ni na haƙura da haihuwar don ni ba zan aure ta ba don na rayu da ita har abada,amma tunna ba ka so mu manta da zancen.

Ga mamakinsa sai A.k ya bugi bayan sa ya na dariya yace." Haba na manta da wannan kuma akan maganar Juwariya na yadda ka aure ta Allah zan ba ka gudummuwa in har Daddy zai amince ya nema maka auren ta a sirri."

Ya ɗan kalle shi ko ya yi tunanin wasa yake masa amma bai ga alamun haka ba sai ya rungume

shi ya na faɗin." Na ji daɗin amincewar ka yamzu mu tafi gurin ƙanin mahaifin ta."

Tofa masu karatu kun dai jin yadda ta kaya game da waɗannan aminan juna,Baba Sani zai yadda ya basu auren ta.Ku ci gaba da bibiyata na gode da yaba lintafina da kuke.

ƊUBBIN GAISUWA GARE KU SABODA COMMENT ƊIN KU YA NA SAKA NI NISHAƊI.

MAMAN SUDAIS
AISHATU MINNA
FATIMA ZARA JOS
SAHURA NURA RABIN RAINA
NABILA MAMAN SAFWAN
HAMDIYA UMMU ABDULHAKIM

Kar dai ku manta sunan labarin "SAKACINA KO HALIN MAZA" Mu haɗu a shafi noma sha huɗu.Ga masu buƙatar shiga cikin group ɗina na whatsapp ga numba 08144072423_.

Kuma ƙofa a buɗe take na ƙorafi gyara ko ƙarin bayani ga zakakuran marubuta,har yanzu ni mai koyo ce.
Kar dai ku manta da wannan lintafin sadaukar wa ne ga zaƙauran marubuciya,kuma ƙawata (SUMAYYA NA'IGE) Allah ya ƙara fasaha ya sa ki fi haka,ina alfahari dake a cikin marubuta da irin taimakon da kike bani.

COMMENT,READ FOLLOW AND SHARE.

Follow this link to join my WhatsApp group:
https://chat.whatsapp.com/LQfVU1ABdFI14btWRhUB1K

*SAKACINA KO HALIN MAZA?*

*RUBUTAWA:-*
*JAMILA LAWAL ZANGO*

*SADAUKARWA GA:-*

*SUMMY M NA'IGE*
_(Aminiya)_

*FIRST CLASS WRITER'S ASSO....*

*Page 14*

BISMILLAHIR RAHAMANIR RAHEEM

Sakamakon aiki da ya yi musu yawa sai hakan ya hana su zuwa kamar yadda suka shirya a ranar,saboda ba su tashi daga gurin aiki ba sai bayan sun yi sallar magariba daga nan kowa ya nufi gidan sa.

A.m ya ji daɗi sosai ranar kasa bacci ya yi gani yake kamar ya auri Juwairah ya gama

musamman da aminin sa ya amince,duk da a cikin zuciyar sa har yanzu ya na tunanin mai ya saka A.k ya sauko har ya amince duk da dokin naƙi da ya hau daga farko.

A haka dai ya yi ta saƙe-saƙen shi amma ya rasa gano komai daga ƙarshe ya janyo bargon da Zainab ta rufe jikinta da shi ta na bacci,ya rufa da shi tare da juyawa dai-dai fuskarta ya rungumeta ya na shaƙar daddaɗar ƙamshi daga gareta,yayin da hankalin sa yake kwance kamar ya yi baƙo ya mutu a ransa duk ya ƙosa gari ya waye su ji yadda za su kaya da ƙanin mahaifin Juwairah.

A.k kuwa ko da ya koma gida hankalinsa a tashe gani yake kamar ya aikata zunubi me girma akan amince masa da ya yi,amma da ya auna a mizanin hankali  sai ya ga da ta auri wannan tsohon rayuwar ta ta shiga garari gara A.m da ko ba komai za su samu ci gaba a rayuwa,duk kuma abin da zai faru wannan kuma ya bar ma Allah lamuran sa shi yake da iko akan komai,kawai abin da zai yi shi ne ya gaya ma Juwairiya kar ta yadda zuciyarta ta fara son A.m.

Ya daɗe sosai ya na shawara kafin ya furta ya amince da auren musamman da ya ji mahaifiyarta ba da lafiya,a taƙaice dai tsotsan tsamiya suke yi a rayuwar su tare da alhini.

Washegari da safe A.m ya yi mishi dirar mikiya ko karyawa a gidan sa ya yi,wanda Maman Najwa ta yi mamakin sammakon sa amma sai ta yi tunanin ko ya na son A.k ya manta komai.

Bayan sun gama karyawa suka nufi gidan su Juwairiya.

Baba Sani ya na ƙoƙarin fita gurin aiki da ƴar ƙaƙuran motarsa da yake riƙe da makullin ta a hannun sa ya na karkaɗawa.

Ganin su a kofar gidan sai ya yi turus ya na tunanin mai ya kawo waɗannan larabawan kofar gidan ko sun yi makuwa ne,saboda ya na da ɗagawa sai ya ɗauke kansa  zai shige cikin motar sa ba tare da ya kalli in da suke ba,duk da tunani ya cika ran shi ganin sun tunkaro sa.

"Assalamu alaika Malam barka gurin ka muka zo,don Allah ko zaka ba mu lokacin ka duk da ba ka san da zuwanmu ba,amma in ka bamu ƴan mintuna zamu tafi musammam in ka yi ma abin da ke tafe damu kyakykyawar fahimta."

Yace da shi da murya mai sanyi duk ƙoƙarin sa ya tabbatar masa da baƙin sa ne saboda fuskar sa ta nuna kokwanton  ko sun yi makuwa ne,duk da ya san ya na da ƴan mata amma ko kaɗan bai yi tunanin za su zo neman ɗaya da ga cikin su.

Ya kalli A.m da ya ɗaure fuskar sa kuma bai ce komai ba ya lura wamda ya yi mishi magana ya fi shi sakin fuska,sai ya mai da hankalinsa ga A.m yace a cike da shakku don shi har yanzu bai yadda gurin sa suka zo ba.

" An ya gurina kuka zo ko kuma kun yi makuwa ne wataƙila tambaya ce da ku."

" Ka na shakkun mun zo gurin ka ne mu ba mutane ba ne? Ko aljanu ka gani." A.m ya ce mishi ba tare da ya kalle shi ba hankalin sa na gurin wayar sa dake hannun sa ya na daddannawa.

Baba Sani nan take ya ji ran shi ya ɓace ya kalle sa a ran sa ya na faɗin." Ba ka sanni ba kenan amma bari na ji da wanne kuka zo."

" Gashi kuma sauri nake zan tafi aiki sai fai ku dawo wani lokacin." Ya ce fuskar sa a ɗaure ganin A.m ya zo da rainin wayo.Am ya buɗe baki zai yi magana sai A.k ya watsa mishi kallo kuma aka ci sa'a ya yi shiru ya ci gaba da kallon wayar sa.

" Don Allah ka yi haƙuri ka bamu ƴan mintina kamar yadda na buƙata da farko ka saurari abin da yake tafe da mu."

A.k ya ce cikin marairaicewar fuska ya kuma haɗa hannun sa biyu ya na roƙon sa.A.m kuwa kofar gidan ya din ga bi da kallo ya na jin wani tsigar jikin shi na tashi,wai shi zai haɗa jini da ƴar wannan wulaƙantaccen gidan mai kama da bola,duk da Baba Sani ya na ƙoƙarin gyarawa amma abincin wani gubar wani.

" Ok to muje in har zaku taƙaita maganar da ta kawo ku a cikin lokacin da kuka iba."

" In sha Allahu."

A.k ya bashi amsa a lokacin da suka shiga cikin gidan zuwa ɗakin Baba Sani A.m ya na ta wulƙita ido ko zai ga Juwairah don shi yanzu ma ya manta da kamannin ta.

"Maza ku gaya min mai yake tafe daku da farko ina fatan ba laifi na yi ba kuka zo kama ni."Ya faɗa kamar kuma ya ji tsoro a fuskar sa.

Hakan ya sa A.k ya murmusa shi ko A.m ko kallon sa bai yi ba.A.k ya gyara zama ya kalli Baba Sani ya ma rasa yadda zai fara ya na son ya ce A.m ya faɗi buƙatar da ta kawo su,amma ya san dunƙula maganar zai yi ta yadda ma ba zai fahimce shi ba ya lalata abin,bayan dai in ina da ya yi,ya kuma shiga ƙumbiya-ƙumbiya daga ƙarshe ya faɗi abin da ya kawo su don barin kashi a ciki baya maganin yunwa.

Alokacin da Baba Sani ya ji maganar da A.k ya faɗa sai ya ji kamar bai fahimci maganar ba kuma har ga Allah a cikin zuciyar sa ya gasgata hakan da bai ji ba.

" Ikon Allah bayin Allah don Allah ka ƙara maganar wallahi ban ji me ka ce ba yadda ka san ciwon kurumta ya kamani,a lokacin da ka yi maganar sake faɗi kamar yadda ka faɗa kuma da Hausa don Allah ba turanci ba.

A.k ya so ya yi dariya jin ya ce ya yi magana da Hausa ƙila in ya ƙara maganar da larabci zai ce ya yi mishi,A.m ya mai da wayar sa a aljihun rigar sa shi bai ga dalilin da A.k zai tsaya ya na ɗan waken zagaye ba,ya san a ran shi irin abin da suka zo mishi da shi bai isa ya hana auren Juwairah ba

" Auren Juwairiya kuka zo nema!" Ya maimaita hakan ya fi sau ba adadi daga bisani ya miƙe zubbur ya na faɗin." Haba dama na yi tunanin a lokacin da na ganku irin yaran manya ne da suke shaye-shaye su yi ɓatan kai su dami mutane,kun ga tunanina ya zama gaskiya ga ku kamar mutanen kirki ta waje amma ta ciki ba hali."

Ya numfasa sannan ya ci gaba da cewa ba tare da ya ba su ikon koda jan numfashi ba." Wallahi na ɗauka wani abin ya kawo ku ko ba sa rana akan Juwairiya a bazan taɓa yadda ta auri wani daga cikin ku ba,bare na ba da Juwairiya yanzu haka bikinta saura sati ɗaya don haka ku wuce ki bani guri ƴan ƙwaya kawai."

A.m ya harzuƙo ya na faɗin." Wa kake ce ma ƴan ƙwaya kai ne mugun ɗan ƙwaya da ka kasa gane mutanen kirki da na banza,ba giya muke sha ko kuma kamfanin ƙwayar muke haɗiya."

"A.m ya kamata ka saukar da fushin ka kasan me muka zo nema."

A.k ya ce mishi tare da kama shi ya zaunar ya na dafa kirjin sa.
" A'a ka barshi ya yi min rashin kunya ya biyo ni har gida zai gaya min magana,a ɗakina fa kake.To bari kaji ko mutuwa za kai sai dai ka mutu, kai ko maka mutu ne aka fito da kai a ƙabari,a ka ce na baka auren Juwairiya numfashin ka zai dawo wallahi sai dai a turbuɗaka a cikin ƙasa ta rufe maka ido."
" Wai tsaya kun ma san me kuka zo min da shi?Juwairiya da na tsana a rayuwata shi ne zaka kazo ka na da kuɗi ka aura taɓ wallahi ina."

Da aka kai wannan gabar sai A.m bai ce komai ba ya rintse idanun shi kawai don aikin A.k ne.Amma sai ya ji A k ya yi shiru ya na kallon Baba Sani da yake faɗin ƙiri-ƙiri ba ya son ƴar wansa ta ƙaru,kai wannan wane irin mutum ne an ya a kwai zumunci a duniya saboda son duniya ko ya ce son kai,mutane sun manta zumunci bayan Allah ya gaya mana zamu tsallaka siraɗi mara zumunci ba zai sha ba.

A.m ya buɗe baki zai yi magana ganin A.k yaƙi magana dai-dai lokacin da Baba  Sani ya sausauta murya ko me tuna ya sa ya yi sanyi ya ce." To kai in ban da ku me za ku yi da mace irin Juwairiya yarinyar da ta gama zagaye duniya ta na yawon aikatau kuma duk mazan gidan sun san ta,sam ba ta da hali mahaifiyarta ta koya mata bin maza har sata take yi ka tambaya har kulle ta a ka yi a prison."

Ya ƙara sausauta murya ya matsa kusa da A.k don ya fi A.m sauƙi ya fara magana kamar zai yi mishi raɗa amma A.m ya na jin me yake faɗi." Ina da yara sun yi karatu na boko in kuma so Juwairiya ba ta san komai ba har talla yi take yi,ai da ka aure ta gara na yi maka fatan ka mutu ba aure.

" Juwairah nake so kuma zan aureta ko da ace duk mazan duniya sun san ta a matsayin ƴa mace."A.m ya ce ransa a ɓace.

" To ba zan ba da ba kuma kamar maganar ta ita matar wani ne na rantse,a yau zan ɗaura mata aure ba sai an jima ba don ina zargin ku za ku iya sace ta.To ni sai in ce kamar an yi maka baki kamar ka mai zai saka ka auri Juwairiya uban ta har ya mutu faskare yake yi, a gurin faskaren ya sara ma kansa ya mutu shi ne za ka ce ka na sonta.

" Nima ba son ta nake ba ban taɓa jin ina son wata ƴa mace bayan matata ba,kai ma in ka furta ina sonta ka yaudari  kan ka don duk faɗin unguwarku ban ga macen da zan ji ina son ta ba."

Kawai sai ya yi galala ya na kallon shi a ransa tunani yake to uban me zai yi da ita,koma dai mene ne ba za ba shi ba in ma ya na son ya yaudare shi ne ya ba shi aurenta,yadda ya rantse Juwariya ba ta ba jin daɗi a duniya tun da ta kange kwaɗinsa a kan ta gara ya ba ma wannan tsohon ya wulaƙanta rayuwar ta.

" Ku faɗi ko me za ku ce ni ba yaro ba ne kuma ba zan baku auren ta ba yanzu ma zan ɗaura mata aure don haka ku cire wanann tunanin."

A.k ya karkace ya zaro makullin mota ya ije masa a gaban sa sannan ya janyo cek da ga aljihun sa ya ije na kimanin miliyan biyar.

Wayyo Allah zo ka ga ido sai ya zare ido can kuma ya fara mitsinan kansa ya gane ko mafarki yake." Ka bar cutar da kanka ta hanyar mintsnin kanka ba mafarki ba ne a zahirin gaskiya lamarin ke faruwa,in har ka bamu haɗin kai  har gida zan canza maka rayuwar ka ta dawo sabuwa in har zaka ba ni auren ta."

A.m ya ce da shi ya na kallon sa yadda ya ruɗe kamar zai zare." Ikon Allah don Allah in mafarki nake ku dake ni sai na farka wai ni ne zaku ba wannan kuɗin don ku auri Juwairiya an ya ku ba ƴan cin kai ba ne?"

Ya faɗa ya na ƙarewa A.m kallo tunanin sa shi ne babba  a wurin cin kai saboda ya fi A.k jiki da faɗi."Ko ma duniya muke ci ba ruwan ka in mun cinye ta tunna ba ƙaunarta kake ba."

A.k ya ba shi amsa amma kuma sai A.m ya kalle shi ya ce.

"Ka daina danganta mu da wannan mu mutane ƙwarai ne kawai fatanmu ka amince da buƙatarmu."

Ga mamakin su sai suka ga ya tattara kuɗin ya saka a aljihun wandon sa har da makullin motar ya fara zare ido. " Duk da cewar na tsane ki saboda wani ƙudiri na wa ba na fatar in da za ya huta ta ji daɗin aure,amma ba zan bari wannan damar ta wuce ni ba Juwairiya sai dai wallahi ina tsananin baƙin cikin faruwar lamarin da na ɗaya daga cikin ƴata kuka nema Allah bari na kira ta sai dai Juwairiya ta nuna mata kyawun halitta amma ta na da hali."

Miƙewa ya yi sai A.k ya kamo hannunsa ya zaunar da shi." Ka barshi ba buƙata ita dai Juwairiyar ya gani yake son ya aura na wucin gadi,shekara ɗaya tak za ta yi zai rabu da ita don a cikin sirri za' a ɗaura auren."

Ya ɗan kalle su a fakaice ya tabbatar da gaske suke yi ko fim suke son shirya wa suka yaudare

shi haka." Tabbas haka maganar abokina yake ni zan aureta na shekara ɗaya matata ce ba ta haihuwa,shi ne nake son ka aura min ita bayan ta haihu zan ɗauke ɗana na sake ta ita ma zan biya ta kamar yadda da na yi maka."

Wani irin daɗi ya cika mishi rai ya kama hannun A k ya riƙe ya na faɗin." Kasan Allah ko auren kwana ɗaya kake son yi da ita zan baka, kai duk abin da za ka yi da rayuwar ta ba nida matsala in har za ka bani kuɗi sai dai da sharaɗin komai  ya din ga biyo wa ta hannuna."

" Wannan kuma ba zai yiwu ba za mu baka duk jin daɗi na rayuwa,amma Juwairiya na cikin wani hali a yanzu ina da labarin mahaifiyarta da ba lafiya kuma za 'ayi mata aikin zuciya kaƙi ka taimaka,ga ƙaninta da yake da matsala tun mahaifinta na raye yake da burin a yi mishi aiki don haka zamu fitar da shi da mahaifiyarta,ita ma mu saya mata gida,sannan ba su da cin yau bare na gobe ka ga ya dole mu inganta rayuwarta wanda da shi zamu ci ƙarfin ta har ta amince da auren."

Baba Sani take ya haɗe rai jin baza a ba shi na Juwairiya ba da ya rantse ba zai ba ta da yawa ba,amma sai ya ɗan saki fuska ya na ce wa." Ni ma ki yi min uzuri ba ni da shi ne da na taimaka mata,wannan aikin wahala kawai nake yi ai nima abin a taimaka min ne."

A.k tsaya wa ya yi ya na mamakin sa ya sani ce wa a kwai mutane masu son kuɗi amma wannan ya wuce tunanin sa an ya na da imani kuwa.

Yauwa a matsayin ƴar aikin gidana za ta zo wanda za ka gaya ma mahaifiyarta za ta aiki na tsawon shekara ɗaya ta koya wa matata girki,wanann dalilin ya sa na ingamta rayuwar ta haka."Ba ka da matsala in ma a matsayi ƴar gadi za ta zo ai wallahi sai an yi auren,na san yadda zan yi da su duka hatta mahaifiyar ta tunna ka ba ni kuɗi ba ka da matsala.

Yace ya na tare da zaro makullin motar ya kalla sai kuma ya maza ya mayar lokacin da A.m ya miƙe a tunanin sa ƙwacewa zai yi don ya ga ba shi da kirkin ɗaya.

" Oh Juwairiya ban sani ba a she ke jarina ne mahaifin ki ya mutu ya bar min dukiya nima na yi kuɗi!Ai wallahi ƴan mata biyu zan gallo a rana ɗaya wayyo Allah!Ashe dama zan yi kuɗi Wallahi mutane za su ga rashin mutunci ehe."

" Yauwa ina motata kuma a ina gidan yake sannan kamar yadda ba ka son matar ka ta sani haka iyayenka kenan ni ne waliyin ku duka ba matsala in ma ka na son a ɗaura yanzu ba

matsala."

Tsabar takaici ya sa A k yaƙi ce wa komai don ya fahimci jahili ne ku kuma son kuɗin ne ya rufe mishi ido yake faɗin ya zama waliyin su duka,sai shi ma ya miƙe ba tare da ya ce mishi komai ba A.m ne ya miƙa mishi takadda ya ce ga shi duk abin da kake son ka sani ya na ciki.

Zai fita A.k ya kalle shi ya ce " Ai ya kama ta a kira Juwairiya mu gaya mata ko in ce ka yi mata bayani ka san waƙa a bakin me ita tafi daɗi."

A.k ya ce mishi cikin gatsali shi har ya fara jin kunyar ta tun kafin ta fito haka kawai daga haɗuwa sau ɗaya sai su zo mata da wanann tatsuniyar.

" Baku da matsalar ga ya mata ita ɗin banza ai gaba ta kai ta."Ya ɗan matso ya na cewa." Dama wannan ɗan iskar tsohon ba ya bani wasu kuɗin kirki yau zan mayar mishi da kayan tsiyar shi,ana harkar kuɗi me za' ayi da tsiya ai ni mutuwar mahaifin ki gaba ta kai ni gobarar Titi a Jos."

" Ga ra dai ka kira ta shi ya sanar mata."A.k ya ce shi dai A.m bai ce komai ba sai dai ya ji wani iri lokacin da Baba Sani ya fita daga ɗakin ya na faɗin bari na dubo ta shegen yawo ne da ita ai kai da zama za ka yi da ita sai ince baka dace mata ba."

Juwairiya ta na duƙune a murhun gawayi ta hira wutan yafi sau ba adadi amma da ta hura sai ya mutu muɗis,kusan kuka take son ta yi don har ta fara hawaye ganin wutar ta taƙi kamawa ta miƙe tsaye tare da zura mata ido,ji take kamar ta ɗora hannu aka ta yi ta ihu.

Ta takaici ta kalli ledar taliyar da take son ta dafa ma Mama ba ta jima da dawowa daga asibiti ba take son ta ɗora musu abinci da ruwan zafi ta kai musu.

Kawai sai ta ki muryar Baba Sani ya na magana tare da ƙoƙarin shigowa duk da ba ta ji me yake faɗi ba,amma ta tsorata matuƙa gani take kamar zai ce ta dafa taliyar ya ɗaura aurenta.

" Juwairiya ina kike ashe dama ke jarina ne?Oh ikon Allah dare ɗaya Allah kan yi bature."Oya maza biyo ni kika abin mamaki aike kin samo mana can jin rayuwa Juwairiya yarinya ɗiyar albarka."

Cikin rashin hayyaci ta tsaya ta na kallon shi sam taka sa fahimtar wai yau Baba Sani yake ce mata ƴar albarka,sai ta fara shakkun ko ya zare ne jikinta ya fara rawa ta matsa nesa da shi,ta na karanto duk addu'ar da ta fito bakinta.

" Ke ban san hauka maza wuce kina da baƙi a falona kuma wallahi in kai min hauka,zan iya ajalin ki kin san bani da wasa akan kuɗi gara ma ki kiyaye!Maza wuce."

Da sauri ta ruga zuwa shashinsa jikinta na kyarma haka kawai jikinta ya ba ta Alhaji Taminu ne ya zo,sai ta rintse idanunta ba ta son ganin shi a haka ta faɗa ɗakin tare da sallama wanda na yi tsammanin a zuciya ta yi,don ko ita kanta ba na tunanin ta ji.

Tsayawa ta yi a ɗakin ta kasa buɗe idanunta sam ba ta son ganin fuskar sa mai kama da biri.

Wani ƙamshi wanda ta shaƙe shi a rayuwarta wanda ba za ta taɓa manta mamallakin ƙamshin, ba har iya tsawon rayuwarta,tun daga ranar da ta shaƙe shi take jin ƙamshin a jikinta har zuwa yau da ta haƙiƙance ma kanta lai-lai wannan mamallakin ƙamshin,mai sanyaya zuciya da kawo nishaɗi ga duk wanda ya shaƙesa ya na kusa da ita,musamman da ta ji sautin da zuciyarta take ta na bugawa da ƙarfi kamar za ta fito fat!Fat!!Har sai da ta dafe gurin.

A hankali ta sauke idanunta da suka kaɗa sukai jajur saboda wahalar hura wuta da tasha,duk da taji an kira sunan ta wanda ta gane ba muryar sa ba ne saboda ko tari ya yi za ta gane muryarsa,amma sai ta tsinci kanta da ɗora idanunta a kansa yayin da idanunnata sukai rau-rau sun canza kala suna ba da wani tarwatsi a cikin su.

A.m da ya ji shigowar ta duk da ba ta yi sallama ba amma ya ji an buɗe kofa an shigo,sanann kiran sunan ta da A.k ya yi sai ya kasa ɗaga idanunsa ya kalleta,duk da ya na son ya kalli wacce yake so ta zamo ɗa ga abu ɗaya tal mafi soyuwa a gareshi don ko sun rabu aba' a sake ma tuwo suna.

"Ya ilahi! Allah na roƙe ka ka farkar da ni daga mafarkinsa da nake,kuma wanann ya zama na ƙarshe tunna na kusa zama matar wani."Ta faɗa aranta ta na ƙoƙarin mai da hawayen da suke son bayyana ɓoyayyaen lamarin da ke cikin zuciyarta.

" Juwairiya ki zauna mana."

A.k ya ce ganin hankalinta ya tafi wani gurin ga mamakinsa sai ya ga ta nemi ƙasa ta zauna tare da saukar da kanta ƙasa.

Gaishe su take son yi amma ji take kamar babu harshenta a cikin bakinta ta ƙara buɗe bakinta

amma ta kasa.

Ganin sun yi shiru duka sai ta ƙara ƙasa da kanta ta na kallon kafen ɗin dake ɗakin tamkar ta na son ta gano ko an maguɗi gurin yin sa.

A.k ya miƙe ya kalli A.m da yake ta danna wayarsa amma a zahirin gaskiya bai san me yake dannawa ba, tunanin sa ta ina zai fara kuma ta fahimce shi,shirun da ya yi ya na son ko A.k zai yi mata bayani  amma sai ya ga ya miƙe.

" Bari in jira ka a mota in kun gama tautaunawar ina mota."

Ya fice ya na girmama lamarin da suka zo da shi. " Juwairaah! Babu gaisuwa wataƙila kin manta ni ko."Ya faɗa don rashin sanin ta in da zai fara.

Ta ɗago idanunta ta zuba mishi amma ba ta ce mishi komai ba,sai dai a ranta ta ce." Ta ya ya za'ai na manta da kai bayan ka tafi da zuciya da ruhu gangar jikina kawai ka barmin,amma to mai ya kawo shi gidammu wanda har Baba Sani ya yadda na zo gurin sa.Aurena yake son yi?".

Ta tambayi kanta sai ta yi saurin kawar da wannan bahagon tunanin ta ce " Kai ina wutsiyar raƙumi ta yi nesa da ƙasa."

"Wai ni kurma kika zama bayan rabuwarmu?Ko kina mamakin ganina ne"

Ya ɗan tambaye da hasala a ranshi ganin yadda take basar da shi kuma ya tsani hakan.

" A'a ai ba'a mamaki da ikon Allah."

Iya abin da ta ce kenan ta ƙara naɗe bakinta ta yi shiru tanani fal a zuciyarta.

Ganin ta tafi wani tunanin daban sai ya ce " Haka ne ba'a mamaki da ikon Allah don haka kar ki yi mamakin na zo nai man aurenki amma fa na kwangila auren shekara ɗaya nake son mu yi dake kuma cikin sirri."

Juwairiya ta ɗago kanta da sauri ta kalle shi a wannan karan ba tare da ta ji nauyin sa ba." Aurena zai yi amma na kwangila mai hakan yake nufi?Sannan kuma cikin sirri to suwa ye ba' a son su san auren?"

Tambayar da ta yi ma kanta kenan a cikin zuciyarta wanda ba ta san maganar ciki ta fito fili ba.Ya gyara gilashin idanun sa ya miƙe tare da juwa mata baya.

" Yes abin da kika ji hakan nake nufi kin san ke ba sa'ar aurena ba ne,na tabbata kina tunanin me ya sa zan aure ki?Kamana ɗan gayu kuma ɗan masu da shi yayin da ke kina talaka kucaka dake.Ki kalle ni mai aji kama na ban yi kama da wanda zai aure ki ba."

Ya numfasa ya juyo ya na kallonta ganin yadda ta saki baki hanci ido ma'ana ta yi galala ta na jin tatsuniyar da yazo mata da shi.

" Matata Zainab wacce nake so fiye da komai rayuwata mace mai aji yarinya ƴar babban gida,Allah bai nufe ta da haihuwa ba ni kuma bazan iya haɗa ta da wata ƴa ɓace ba don na yi mata alƙawarin bazan yi mata kishiya ba,ga shi ina son na ga ƙwaina a duniya shi ya sa nake son na aure ki a sirri ki haifa min ɗa ɗaya na ba ta amma a gidana zaki zauna amatsayin ƴar aikin ta."

Wani irin hajijiya ta ji ya ibeta sai ga shi a gabansa ta zare ido jin a bin da ya faɗa,take ta ji wani hajijiya zai yarda ita ƙasa ta rintse idanunta,hawaye suka fara turereniya a kan fuskarta da ta shiga da tashin hankali.

" Allah na roƙe ka ka farkar da ni daga wannan mummunar mafarkin na farka ba tare da na gan shi kamar yadda yake tsaye a gabana! Ya Allah ka ɗauke ganina da shi na har abada da kunnuwana su ƙara ji min abin da yake faɗi ba,Ai gara na auri Alhaji Tanimu da na amince na auri mutumin da nake jin,bayan shi babu wani ɗa namiji a duniya shi ne yake son na yi rayuwa a gidan shi a matsayin ƴar aikin matarsa.

Wayyo Alla!gara na ga ranar mutuwata don zan fi samun maslaha a cikin ƙabarina da na amince da buƙatarsa.

Tofa ga dai Baba Sani ya amince shin Juwairiya za ta amince ya auren zai kaya?Ku dai ci gaba da bibiyar lintafin SAKACINA KO HALIN MAZA.

ƊUBBIN GAISUWA GARE KU SABODA COMMENT ƊIN KU YA NA SAKA NI NISHAƊI.

MAMAN SUDAIS

AISHATU MINNA
FATIMA ZARA JOS
SAHURA NURA RABIN RAINA
NABILA MAMAN SAFWAN
HAMDIYA UMMU ABDULHAKIM

Kar dai ku manta sunan labarin "SAKACINA KO HALIN MAZA" Mu haɗu a shafi noma sha huɗu.Ga masu buƙatar shiga cikin group ɗina na whatsapp ga numba 08144072423_.

Kuma ƙofa a buɗe take na ƙorafi gyara ko ƙarin bayani ga zakakuran marubuta,har yanzu ni mai koyo ce.
Kar dai ku manta da wannan lintafin sadaukar wa ne ga zaƙauran marubuciya,kuma ƙawata (SUMAYYA NA'IGE) Allah ya ƙara fasaha ya sa ki fi haka,ina alfahari dake a cikin marubuta da irin taimakon da kike bani.

Follow this link to join my WhatsApp group:
https://chat.whatsapp.com/LQfVU1ABdFI14btWRhUB1K

*SAKACINA KO HALIN MAZA?*

*RUBUTAWA:-*
*JAMILA LAWAL ZANGO*

*SADAUKARWA GA:-*

*SUMMY M NA'IGE*
_(Aminiya)_

BISMILLAHIR RAHAMANIR RAHEEM

A karo na biyu ta ƙara gwalalo idanunta." Ina hakan ba zai taɓa yuwu ba!Gara na rayu a cikin talauci na kuma mutu a cikin sa.Anya ya san me yake faɗi kuwa.
Sai kawai ta nufi hanyar fita ba tare da tace mishi komai ba.
Juwairaah!"

Ya kira sunan ta da sauri tare ƙofar ya kama hannunta wani irin hajijiya ya kama ta wani abu mai kama da shokin,ya na zagaye jikinta yayin da yake fitowa daga gurin da ya riƙe ta ya na ƙara wutar sonsa a cikin zuciyar ta.

" Don Allah ka cika ni ba zan iya abin da kake faɗi ba,hakan ya tabbatar min da ka tsane ni ba ka son ganin farin cikina dama na san ni ba'a sa'ar auren ka ba ne, to amma kaje ka auri mata masu aji irin matarka ta yadda za ka samu ƴara daga gidan kuɗi,ba irina wanda mahaifina ya mutu bai bar min komai ba.

Ta faɗa tare da fisge hannunta da sauri ya sha gabanta ya toƙare kofar da take son ta fice, jikinsa ya yi sanyi ganin kamar ba za ta yarda ba,amma kuma ya zama dole ya san yadda zai yi ya shawo kanta,saboda amincewar ta ne kawai zai sa ka ta jure duk wani abu da za ta gani a gidan.

" Nima na so haka na sami mace mai aji kama ta, amma kin san babu wata mace mai aji wanda zan nema ta yadda da hakan.Kasancewa ta ɗa namiji da kowa ce mace za ta yi burin samu shi ya sa naƙi nai mar me aji iri na, don na san ba za a kwashe dai-dai da ita ba,kuma kema fa so nake na ceci rayuwarki daga ƙangin talaucin da kike ciki.

Ya ƙarashe maganar da murya na salon yaudarar shi ya na son ta amince.
Hawaye suka ƙara turereniya a fuskarta ta kalleshi da nufin ta saka wani mugun tsanar shi a cikin ranta,amma sai ta ji wani madarar son sa ya na ƙara shiga cikin bargon jikinta a duk sanda ta yi kuskuren haɗa ido da shi.

" Sai ni talaka ko?Ni da Allah bai saka min zuciya na so ba.Ko naƙasun talauci ya na yin tasiri a

zuciya duk lokacin da ta ke son wani?Shi ya sa za ka zo ka cuci rayuwata ta ɗa na kake son  na haifa na ba wata mace na har abada?Don Allah ka fita daga cikin rayuwata na roƙe ka na san ba za ka samu matsala da ƙanin mahaifina ba,amma ni ba zan amince da mugun nufin ka a kaina ba.A yau na yi burin dama ban taɓa sanin ka a cikin rayuwata ba."

" Ke ya ishe ki ƴar talaka kawai zaki zo ki na jera min wasu maganganu kamar wani ɗan ki!Dama ban yi miki dole ba."

Ya faɗa tare da kaucewa ya ba ta hanya ganin hakan ya sa ta zura da gudu za ta fita,dai-dai lokacin da Baba Sani ya yi gyaran murya."Ya kamata ka wuce abokin ka ya na jira,kawai ka nemo waliyin ka a duk sanda kake son a ɗaura auren kar ka damu da ita ko amincewar ta"
Da ido ya kalleta ya na gasgata abin da yake faɗi." Kin ji da kunninki abin da kwaɗayayyen ƙanin mahaifin ki yake cewa?Don haka ina tambayar ki ne don kar ayi ba tare da yaddar ki ba kizo ki ɓata komai."

Ya zaro waya mai kyau da tsada ya ije mata." Ga shi zan wuce na gaji da wannan kukan nan naki da kika tasa ni da shi.Fisabilillahi sai kace na zo  gidan ta'aziya,duk abin da kika yanke zan kira sai ko gaya min." Ya miƙa mata kuɗi masu yawa." Ga shi ki je ki yi ma marasa lafiya siyayya.Ina ƙara gaya miki ɗa ɗaya kawai nake son ki siyar min bayan nan zaki iya auren namiji wanda ya fini,domin zan ƴanta rayuwarki zan gina ma mahaifiyarki gida na ba su duk wani jin daɗi na rayuwa.

Shekara ɗaya ne fa kawai za ki yi kina ma masoyiyata aiki in ma kin sami ciki, da wuri zan ɗauke ki daga gidan kin ga kin huta kenan,sannan ki iya takun ki ba da sani ta zan yi komai ba."

Ya numfasa ya na kallon ta yadda ta yi zuru ta na kallon shi,yayin da zuciyarta ta ci gaba da bugu cikin tashin hankali.
"kamar yadda na gaya miki haka za ki yi don haka ko kallona kar ki yi in dai ta na kusa da ni.Kasancewarta ba mai zaman gida ba ne kinga haka zai bamu damar aurenmu ya tafi cikin sirri."

Ya ce da ita sannan ya  fice ya barta a tsaye tamkar gunki  sai da ta ɗauki tsawon lokaci sannan ta yi zaman ƴan bori a ƙasa tare da fashewa da kuka.
" Don Allah karfa ku yi min ƙarya ku dawo fa in ba haka ba wallahi sai na nemo ku duk in da kuke don ba zan ga samu na ga rashi ba.

Motar su na ɓacewa ya ruga da gudu ya shige ɗakinsa alokacin Juwairiya har ta miƙe ta share hawayenta za ta fice." Ƴar albarka Juwairiya zo mai ya baki."

Sai kuma ya hangi damin kuɗin da ko ta kan shi ba ta bi ba, ai da sauri ya dafe ya na washe baki sannan ya miƙa mata dubu biyar ya ce." Gashi maza ki tafi Juwairiya ya gaya miki komai ko?Ai Allah ya tarfa ma garin ki nono kin huta da auren wannan mutumin,dama ɗan iskan tun da ya ga na ba shi auren ki ya dai na bani komai,duk da na yi baƙin ciki amma ko ba komai ai

na samu ta sanadin ki rayuwata za ta shiga cikin jerin masu da shi."

Juwairiya ba ta ce komai ba har ta kai ƙofa za ta fita, sai kuma ta dawo ta ce." Ni fa ba zan aure shi ba haba Baba ka ji tausayina mana!Wallahi in..."

"Rufe min baki banza shashasha!Don ma kin samu zai aure ki wallahi da bai zuba uban kuɗin nan  ba, to ko megadin gidansa yake son ki yi masa ba zan bari ba,ai ke gaba ta kai ki ko banza a shekara ɗaya zaki rayu cikin daula,ko banza za'a sha zaƙi da maiƙo a rabu da tuwo wanda shima ba kullum ake samu ba."

Da sauri ta fice jin maganar da yake mata wanda duk cin fuska ce.

Juwairiya ta shiga cikin tsananin hankali tun lokacin da ta fito da ga ɗakin Baba Sani ta kife kanta ta na wani irin kuka mai tsuma zuciyar mai saurare.

Yayin da tausayin kanta ya rufe ta ganin mutumin da take matuƙar so ya zo neman ta akan auren kwangila."Yanzu inna auresa shekara ɗaya za mu yi? Shima tsakanin mu tamkar mage da ɓera tunna matarsa ta yi katanga a tsakanin."

Abin da take ta faɗi a ranta kenan sai kuma ta share hawayen da damuwa cike a zuciyarta,don ta rasa yadda za ta kwatanta wannan auren da yake son su yi,amma a ranta ta ƙudira koma me zai faru sai dai ya faru don ba za ta aure shi ba,ai gara ya barta  a cikin tsananin talauci saboda in talaucin bai kashe ta ba,tsananin son da take mishi da kishin matarsa zai kai ta lahira!

Ko da ta isa asibiti ba yan ta gama girki abin mamaki sai ta ga Baba Sani zaune a can,ya dage sai zuba ruwan surutu yake yi tamkar wani aku.

Sai Juwairiya ta kasa shiga ta tsaya ta na kallon shi da mamaki ganin yadda yake ta magana har da dariya ga uban leda da ya siyo musu abu.

Mama shiru ta yi ta na kallon shi da mamaki."Oh ikon Allah duniya juyi-juyi!" Abin da ta ce kenan cikin tsananin mamakin sa.

"Ƙaraso mana Juwairiya kin ga har na riga ki ai daga gurin aiki sai na taho,ban san kina gida ba."

A sanyaye ta shigo tare da ije abincin dai-dai lokacin da Baba Sani ya tashi tare da yi musu sallama ya tafi.

Da sauri Juwairiya ta bi bayan sa ya na ƙoƙarin shiga motar sa ta riƙe murfin motar idanunta na zubar hawaye " Ba zan aure shi ba gara ya barni a halin da muke ciki,amma ba zan yi aure ba wanda mahaifiyata ma ba'a son ta sani!Tun wuri ka mai da masa da kuɗin sa ni zuciyata ba irin naka ba ne!Na san mutuncina ai talauci ba hauka ba ne "

Kau ya gaura mata mari " Baki da hankali kina wasa da ni ke baki san halina,ni murucin kan dutse ne! In har kika ce ba za ki yi wannan auren ba,kin ji na rantse miki Juwairiya zan iya kashe ki har da mahaifiyar ki.Don haka in baki bi umurnina ba ki kuka da kanki."

Ya ja motar sa ya barta a nan tsaye cikin tashin hankali sai kawai ta rushe da kuka,sai da ta yi mai isar ta sannan ta yi shuru ta wanke fuskarta ta shiga cikin ɗakin da Mama suke.

" Ikon Allah abin duniya ba ya ƙarewa kin ga abin mamaki ko.Ai addu'a takobin mumuni ne." Juwairiya ta ce."Umh Mama."Sannan ta ɗauki filet ta zuba mata abinci.
"Juwairiya bayan fitar ki likita ya zo  ya ce in dawo ki je ki same shi,sannan ya ba da takadda kamar na magani ne."

Ta ce cikin damuwa da murya ƙasa-ƙasa kai da ga ji ka san ta na cikin jinya mai tsanani.
" To Mama bari na je na same shi."
Ta miƙa mata abincin sannan ta fita zuwa ofishin likitan.
"Ok zauna"

Ya ce da ita bayan ta ƙwanƙwasa ta shigo a hankali ta zauna cikin tsoro-tsoro don ba ta san dalilin da likitan ya kira ta ba.

Ga sakamakon gwajin da muka yi ma mahaifiyar ki nan gaskiya ta na cikin matsala ya kama ta a canza mata asibiti,saboda zuciyar ta ta kumbura dole a yi mata aiki.
Da sauri Juwairiya ta miƙe tare da zare idanun ta jin abin da likitan ya faɗa." Na shga uku Allah ka kawo min ɗauki!Mama za'a yi wa aiki!"

Sai hawaye shar-shar a fuskarta ta koma ta zauna kamar yadda likitan ya umurce ta ganin ta tada hankalinta.

" Ki yi haƙuri! Jarrabawa ce amma kar ki yadda ta ji lalurar da take da shi wannan dalilin ya sa na so namiji ya zo na gaya mishi,amma sai ta nuna ke ɗin dai zan gaya ma wa."

Da sauri ta miƙe tare da ficewa daga ofishin har ta kai ƙofar ɗakin da Mama ke kwance, sai kuma ta ja da baya ta tsaya kamar wata zararra!Tuna likita ya ce kar ta gaya ma Mama komawa ta yi wani guri ta na son ta yi kukan amma ba hawaye sai tuƙuƙi da zuciyarta take yi mata.

Ta ɗauki tsawon lokaci sannan ta koma cikin ɗakin.Da daddare Juwairiya ta kasa bacci sai juye-juye take,abin duniya ya haɗu ya yi mata yawa ji take kamar ta ɓace a cikin duniyar.

Kwana biyu kuma sai Ibrahim ya fara ciwon ƙafa wanda in ya na yi yake fita cikin hayyacin sa,don har tsuma yake na tsawon lokaci bai farfaɗo ba.Abin duniya ya yi mata yawa ga tunanin A.m da yake son ta baƙunci kabarin ta kafin mutuwarta,duk ta yi fari ta rame kamar wacce ba ta da jini a jikinta sai ƙashi da ya zama ado a jikin ta.

Zaune take a gefen Mama ta zura mata ido ta na tausayin halin da suke ciki,don ko wannen su da jinyar da yake yi.Hannu ta sa ta yarfe zufan dake goshin ta,wanda yake tsatstsafo mata duk sanda ta tuna da A.m.

" Inna lillahi."

Ta ce tare da miƙewa ta tsaya bakin windo sai hawaye." Wai dama haka ciwon so yake?Allah na roƙe ka ka cire min soyayyar son maso wani a cikin rayuwata,yayin da nake tsananin son sa shi haɗuwar mu ya zama dama a gare shi ya faranta ma masoyiyar sa rai.

Likitan ne ya yi sallama ya shigo wanda ya saka Juwairiya ta juyo da hawayen dake zuba a fuskarta,ya tausaya mata sosai amma sai ya miƙa mata takadda ya ce." Ga shi Juwairiya an baku sallama duk da jikin mahaifiyar ki bai warke ba,amma baku da kuɗi kuma mai asibitin ya na buƙatar kuɗi."

Juwairiya da ta ji ta daskare amma sai ta kai hannu ta ƙarɓa jikinta a sanyaye ba tare da tace mishi komai ba,ita zuwa yanzu hawaye sun ƙare da ga fuskarta sai wani azaban raɗaɗin baƙin ciki da take kurɓar ruwan sa mara daɗi a cikin zuciyarta wanda yafi na guba illah.

Sai ta fara haɗa kaya dai-dai lokacin da likitan ya fice daga cikin ɗakin.

Kwana biyu da dawowar su jikin Mama ya rikice Juwairiya a daren ranar ta ɗauka ba za ta kwana ba,da safe ta sami Baba Sani ta na kuka ya taimaka ma Mama da ranta yake tsakanin mutuwa da rayuwa.

"Kin ji na rantse miki Juwairiya ko mutuwa za ta yi sai dai ta yi matuƙar ba za ki amince da auren A.m ba.Ya faɗa ya na zare ido sannan ya ɗora da ce wa."Ai dama ba son ta kike ba in banda ƙashin tsiya ne dake Juwairiya irin A.m ko auren kwana ɗaya yace ki yi,ai na ɗauka jikinki na rawa za ki amince."

Haka ta dawo jiki a sanyaye ta zauna ta tare da zuba ma Mama ido ta na hawaye.Sai ta ji ɗakin ya ɗauka da wani irin abu kamar na vibration,da sauri ta miƙe don ita tsoro ta ji sai da ga baya ta koma ta zauna tuna wa da ta yi A.m ya ba ta waya,wace tun ranar ta ije ta amma abin mamaki cajin bai ƙare ba.

Sau uku ana kira amma ba ta tashi ba ta na kallon Mama dake bancin wahala,sakamakon rashin baccin da ba ta samu ba daren jiya,yayin da kiran ya ci gaba da shigo wa sai hakan ya ƙular da Juwairiya ta miƙe da sauri ganin Mama ta fara mutsu-mutsu za ta farka.

Waje ta yi da wayar ta kai hannu da nufin ta kashe don ta tabbata shi yake kiranta sai kuma ta fasa tuna da halin Mama take ciki,ta saki nauyayyar  ajiyar zuciya.

Wata gefe na zuciyar ta ta bijiro mata da ta amince da auren A.m don ta ceci rayuwar mahaifiyarta duk da ta san ba ta yi ba Mama adalci ba,amma halin da suke ciki zai saka ta

amince ba tare da ta yi tunanin komai ba.

Sannan ko ba komai ai auren sa ya yi mata katanga da auren tsoho a lokacin da suka rabu,ta na matsayin bazawara ba wanda ya isa ya yi mata karan tsaye a rayuwarta.

Sai dai da ta tuna tsananin son shi da take da kuma ɗanta da za ta ba ma matarsa,wacce take jin yanzu bayan mutuwarta babu abin da ta tsana fiye da ita.

Ta na wannan tunanin ne ta ji muryarsa ta daki dodon kunninta ya na faɗin." Hello Juwairaah ki na ji na?"

Bata san ta danna wayar ba ashe ta amsa kiran da sauri ta kanga wayar a kunninta ba tare da ta yi shirin hakan ba,jin daddaɗar muryarsa da ya saka ta manta komai ta ji kamar ta zuƙo shi ta wayar saboda wani irin ƙaiƙayi na son ganin sa da idanuwanta suke mata.

" Ina jinka."

Ta ce jin ya maimaita maganar har sau uku.Ba tare da ya yi wata doguwar magana ba ya ce." Ya maganar mu kin yanke shawara? Saboda zan yi tafi zuwa India kin ga sai na gama komai kafin na tafi."

A hankali ta sauke ajiyar zuciya ta sauke cikin baƙin cikin daina magana da ya yi,saboda jin muryarsa take kamar ana busa mata sarewa.

Sai kuma ta fara sheshsheƙar kuka ta buɗe baki za ta yi magana sai kuma ta fasa tare da kecewa da kuka.

" Oh my God! Ni fa ba na son mace mai saurin kuka haka kawai ki dinga kuka,in dai kuka za ki dinga min zamu tsamu matsala dake."

Ya numfasa ko za ta ce wani abu sai ya ji ta yi shiru sai ɗan sautin kukan dake tashi a ajiyar zuciyar da take yi.

" Na amince!"

Ta furta tare da ƙara sakin sabon kukan duk da gargaɗin da ya yi mata ya shiga jikinta don umurnin sa kamar yankan wuƙa ne,sai da ta kasa hana kuka a ranta ta na tunanin yadda za su yi a tsakanin su ba a lokacin da aka ɗaura auren.

Ta ƙara buɗe bakinta da ƙyar ta ce " Don Allah ka kawo ma mahaifiyata ɗauki ta na cikin wani hali diɓ!."Ta kashe wayar tare da tsugunawa a gurin ta na jin wani hali wanda duk ƙwaƙwana na kasa gane halin da take ciki domin ita kaɗai ta san halin raɗaɗin da take ciki.

A.m ya ji wani sanyi a zuciyarsa waya ya ɗauka ya kira A.k nan take ya fara shirye-shiryen yi ma Mama biza.

A lokacin da aka fita da Mama ba ta san halin da take ciki ba Juwairiya har ta cire ran zai kawo ma Mama agaji,saboda da ta ga kwana uku da maganar su bai kira ta ba wanda hankalinta ya

tashi sosai.

A ranar na uku Baba Sani ya sanar ma Juwairiya su fara shiri har sujjada shukuriya sai da ta yi gani take kamar Mama mutuwa za ta yi.

Ba ƙaramin mamaki ta ji ba lokacin da Baba Sani yake gaya mata har da Ibrahim za'ayi tafiyar,zuciyarta ta hakiƙance mata Allah ya kawo mata A.m a cikin rayuwarta don ya fitar da su halin da take ciki,sai dai in ta tuna son shi da ya mamaye mata zuciya ta na jin tausayin ranar da za su rabu watakila shine sanadin ta.

Su Juwairiya na ƙasar waje A.m da A.k suka shirya zuwa gidan Daddy domin su shawo kansa ya amince ya ƙarɓar mishi auren Juwairiya.

Gabansa ne yake faɗi ras! Har suka isa gidan maigadi ya wangale musu get,A.k da shi yake tuƙi ya shigar da motan.
Daddy ya na falonsa ya na ganin A.m ya tashi ya rungume shi tare da jawo A.m suka zauna a kujera me cin mutum biyu." Na yi kewar ka son ya kuka dawo? Wannan mutumim ya kirani don Allah son ka rage zuciya ka san harkan kasuwanci sai an yi haƙuri."

Sumar kan shi ya shafa tare da sakin murmushi duk da mutumim ya ɓata mishi rai matuƙa,amma yanzu ba shi ya kawo su ba.

Bayan sun ci abinci wanda A.m bai so ya ci ba amma Daddy ya matsa mishi,duk yadda yake da hope a kan sa sai gashi ya kasa sanar mishi ya na ta tunanin yadda zai fara magana.
A.k kuma ya yi banza da shi ya na ta kwasar girki shi ko tun da ya kai loma biyu wanda ya ci ne saboda takurawar da da Daddy ya yi mishi.

" Am Daddy don Alah a kwai abin da yake tafe damu,amma muna roƙon ka ka fahimci abin da ya kawo mu don Allah Daddy."
Ya yi ƙundumbalar faɗi da fuskar tausayi ya na hararar A k da ya manta da shi ya na ta aikawa cikin sa bayani,kamar da ma abin da ya kawo su kenan.
" Ina jin ka son dama har a kwai abin da za ka kasa sanar da ni?"
" Aure nake ne ma amma a kwai ƴar matsala."Ya ce ya na kallon Daddy ya ga yadda zai karɓi zancen.
Daddy kuwa tsananin tausayin shi ya kama shi da ya tuna shi ma haka ya din ga aure-aure don ya samu ɗa,amma kuma shi ne ba ya haihuwa ba matarsa ba me ya sa yake son ya ƙara aure.
" Son mata biyu anya za ka iya zama da su kai da baka da haƙuri,ɗayar ma ya ka cika bare ka tara fiye da ita.Amma tunna zaka iya faɗa min ƴar wacece kuma su waye ahalin ta?"

Wannan karan A.k ne ya ce." Ba ƴar kowa ba ce asalima mahaifinta ya mutu ƙanin mahaifin su yake riƙe da su."

" Son ƴar talaka matsiyata kake son aure ka manta Zainab ko ƴar wace ce ita?"
Ya miƙe tsaye tare da furta hakan ya na mamakin A.m da ya canza duk yadda yake nuna tsanar talaka sai ga shi ya jajibo auren ta.
Ya shafa kansa ya na faɗin." Karka damu Daddy auren nawa na wucin gadi ne,sannan saboda ita Zainab ɗin zan ƙara aure."Take ya kwashe komai ya gaya masa.

Sosai yake kallon sa ya na mamakin wai Zainab ce ba ta haihuwa amma ya ce shi ne baya haihuwa.Lai-lai ya tabbata ya na shaye- shaye.
" Ka yaudare mu Abdurrahman an ya ka yi m kanka adalci ka n ganin in kai ne ba ka haihuwa za ta yadda ta zauna dakai?Ka san ciwon rashin ɗa har yau kuka nake kan ban taɓa haihuwa ba duk da mahaifin ka ya ba ni kyautar ka.Wallahi da sake dole kowa ya sani sannan ka canza mata ba ƴar talaka ba don ba ma haɗa dangi da matsiyata!"
Ya ce tare da miƙewa zai fice ga mamakin sa sai ya ga A.m ya yi sauri ya kama ƙafafunsa ya riƙe ya saka kuka kamar wani ƙaramin yaro ya na roƙon sa,wanda magana uku ya yi masa har ya saka ya zauna jikin sa sharɓar da zufa ya na kallon su.
" Daddy ka tuna Zainab ƴar amininka ne kuma a saboda ni ta kamu da wannan ciwon,Zainab ta rantse in har na haɗa ta da wata mace za ta rabu dani,rayuwata ba za ta yiwu ba in babu Zainab ina sonta raina fansa ne akan duk abin da take so."

Waɗan nan kalamai ya gaya masa ya na kuka wanda hakan ya sa ya zauna don ya saurare su." Na ji to yanzu ya kuke son ayi ni fa ba mahaukaci ba ne kuma ni soyayya ba ta mai da ni zautacce ba,kar na zo na biye maka mu aika ta hakan lamari ya caɓe mu rasa yadda za mu yi." Ya tambaye shi ganin A.k ya miƙe ya ba su guri saboda yadda Daddy yake kallon sa kamar ya na buƙatar hakan.

" Saboda haka ya sa na zaɓi ƴar talaka wanda ba su da komai ka ga ta gurin ta hankalinmu ba zai tashi ba,kuma ni na tallafi rayuwar ta.Matsiyata ne basu da komai sai talauci da garari a rayuwa sannan ƙanin mahaifinta wani irin mugun me son kuɗi ne ya kuma tsane ta don haka kar ka damu."Ya ce ya na kallon shi don duk wani kalamai da zai gaya mishi ya ƙare shi dai burin shi ya amince.

" Kai ku tashi ku tafi kai son ka je ka yi tunani na baka nan da sati biyu,in baka sanar da mahaifin ku gaskiyar lamari ba to ni zan fasa ƙwai maza tashi ka wuce!
Hankalin A.m ya tashi matuƙa ko kaɗan bai yi tunanin zai yi kafiya akan lamarin ba,saboda yadda ya ga baya son ya ga ɓacin ransa,ƙara riƙe ƙafar sa ya yi ya na kuka da roƙon sa,amma haka Daddy ya janye ƙafarsa ya shige ɗakin sa duk da kukan shalelensa na yi masa ƙuna sai dai lamarin da ya kawo mai girma ne.

A mota suna tafe babu mai yi wa juna magana A.m tunanin kuɗin da ya kashe take yi,sai ya ji ya ƙara samun ƙarfi wanda washegari Daddy na fitowa daga masallci ya gan su a tsugune.

A ƙalla sun ɗauki tsawon wata suna jerangiya amma Daddy ya hau dokin naƙi,cikin ikon Allah A.m har ya haƙura sai ga kiran shi ya sanar masa su shirya yau zai je a ɗaura aure.

Haka kuwa aka yi bayan an idar da sallah aka ɗaura auren Juwairiya Ahmad da Abdurrahman Dawood akan sadaki naira dubu ɗari biyar wanda Baba Sani ya dage hakan zai ba da,ba tare da damuwa ba ya amsa wanda Daddy ne ya biya kuɗin.

Tofa masu karatu ga shi Allah ya kawo mu an ɗaura aure kuci gaba da bibiyar lintafin domin mu ji yadda za ta kaya.

SHIN JUWAIRIYA ZA TA IYA DANNE SON DA TAKE MASA TA ZAUNA DA SHI KAMAR YADDA YA BUKATA?NI DAI NASAN SON GASKIYA BA YA ƁUYA WAƊANDA SUKE CIKIN SO SUNE KAWAI ZASU AMSA AMIN TAMBAYAR NAN.

TAKU JAMILA LAWAL ZANGO

Follow this link to join my WhatsApp group:
https://chat.whatsapp.com/LQfVU1ABdFI14btWRhUB1K

*SAKACINA KO HALIN MAZA?*

*RUBUTAWA:-*
*JAMILA LAWAL ZANGO*

*SADAUKARWA GA:-*

*SUMMY M NA'IGE*
_(Aminiya)_

*FIRST CLASS WRITER'S ASSO....*

*Page 16*

BISMILLAHIR RAHAMANIR RAHEEM

Jikin Baba Sani ya na rawa ya dawo gida don murnar kuɗin da Daddy ya biya a matsayin sadakin Juwairiya,da ga gurin ɗaurin auren ɗakinsa ya wuce sai da ya yi fasalin kuɗin ya cire kuɗi kaɗan da nufin zai bawa Juwairiya sadakinta,wan da sauran ya saka su a aljihunsa murna cike  a zuciyarsa, ganin irin yadda rayuwarsa ta canza lokaci guda kuma duk a saboda Juwairiya.

Ya yi kiran Juwairiya da take girki duk da damuwar da yake ranta amma ta na jin daɗin yadda Mama ta samu sauƙi jikinta ya yi sauki,ga kuma Ibrahim da shi ma an yi masa aikin a ƙafar sa ya samu sauƙi sai wani daɗi ya mamaye mata zuciya har take girkin da kula ta na son Mama ta ci abincin sosai.

Kiran da Baba Sani ya ƙwala mata ya sa ta ji gabanta ya faɗi ras!Don ta san yanzu in dai zai kira ta to akan maganar auren ne.Cikin saiɓin jiki ta amsa tare da saurin zuwa gurin sa.

" Amaryar shekara ɗaya yaufa an ɗaura  auren ki da A.m ɗazu."Ya faɗa tare da miƙa mata kuɗi. Wani irin zufa ya keto mata da sauri ta dafe ƙirjinta." Na shiga uku."A bin da ta ce kenan sai hawaye suka fara turereniya a ƙuncinta.

Miƙa mata kuɗin ya yi amma sai ta ƙi amsa tare da shigewa cikin gida hankalinta ya tashi sosai ganin da ga yau ta zama matar A.m.
Tun da ya gaya mata maganar ɗaurin aurenta ta shiga cikin wani hali na rashin natsuwa gabaki ɗaya ta ruɗe,ta na cikin waswasin tunani sai ga kiran sa ya shigo da ta tuna yau a matsayin mijinta ya kira ta kuma ba ta san me zai ce mata ba sai ta ƙara ruɗewa.
Daga bisani kashe wayar ta yi gabaki ɗayan ta ta kai ta ɗakin ta in da take ɓoyewa kar Mama ta gani.Ta koma gurin girkin ta da take tunanin kar ya ƙone.
Sam ta manta ta saka gishiri a girkin ba tare da ta tuna ba kawai ta ɗauki gishirin da nufin ta zuba ba,ta sai ta gishirin a tukunya wanda hannunta ya zame ta juye shi duka sannan kuma a lokacin ta tuna ta riga ta saka gishiri.

Kawai sai ta fashe da kukan da ta kasa gane saboda juye gishirin ne take kuka,ko kuma a kan maganar da Baba Sani ya gaya mata ne oho.

Mama da ke falo ta na shan magungunan ta sai ta ji kukan Juwairiya da ƙarfi ta na rera shi kamar wata ƙaramar yarinya duk da jikinta ba ƙarfi, amma hakan nan ta daure ta fito ta na dafe bango a ranta ta na mamakin mai ya saka ta kuka haka.

"Lafiyar ki kuwa?"
Ta ce a lokacin da ta ƙaraso gurin sai ta yi turus! Don ita hankalinta ya tashi ta ɗauka ƙone wa ta yi,amma ganin lafiyarta ƙalau sai hankalinta ya kwanta
Ganin ba ta amsa mata tambayar da ta yi mata ba.

Kama ta ta yi ta riƙe tare da shigar da ita cikin ɗaki saboda kukan da take yi ya tsorata ta." Ki yi shiru don Allah ki dai na kuka kin san abin da likita ya gaya min,yanzu haka dalilin kukan ki ba ki ji yadda zuciyata take bugawa ba."Ta faɗa tare da dafe ƙirjinta da yake harbawa da ƙarfin gaske.

Ganin haka hankalinta ya tashi da sauri ta share fuskarta duk duk yadda ta so ta ƙaƙaro murmushi a fuskarta,amma hakan ya faskara wasu sabbin hawayen da suka ƙara yin matsuguni a fuskarta.

" Mama don Allah kar ki saka damuwa  a ran ki.Girkin ne ya bani haushi saboda na manta na zuba gishiri kuma na zo na ƙara shi ne hannuna ya goce na juye duka."

Dariya Mama ta yi ta ce." Juwairiya wacce ta iya girki komai auna wa ake shi ne yau ta yi juye lailai yau hannu ya ƙwace kenan.To ai ni ban ga abin kuka ba sai dai in a kwai abin da kike ɓoyewa."

Gaban Juwairiya ya faɗi jin Mama ta na so ta ɗago ta sai ta yi sauri ta tsaida hawayen ba shiri."Iya kan abin da ke damuna Mama kenan haba dole na yi kuka bayan tsawon jinya da kika sha a ƙasar waje,yau za ki ci girkina ga shi hannu ya ƙwace min."

Mama ta koma ta zauna ta ce " To ba sai ki ɗora wani ba."Ai da sauri ta miƙe tare da faɗin."To." ganin yadda Mama ta kafe ta da ido haka kawai sai wani irin kunya ya lulluɓeta har ta ji ta kasa haɗa ido da ita.

" Ok bara na je na ɗora na san yunwa kuke ji."Ta faɗa ta na shafa kan Ibrahim da ke zaune ba ya tafiya saboda likita ya ba shi lokacin da zai fara tafiya.

"Juwairiya dawo magana zan yi dake."Mama ta faɗa tare da lumshe idanunta da su kai mata nauyi.
"Mama don Allah bari na gama girkin kar yunwa ta dame ku ga Ibrahim har ya fara yaushi."
Ta ce cikin in ina ta na son ta kauce ma idanun Mama." Kar ki damu da dawo kawai akan mutumim nan bawon Allah da ya ke taimakonmu,na ke son mu yi magana ni fa kullum tunanin sa nake yi ga shi ya ƙi bayyana kan shi,bare mu yi masa godiya an ya saboda Allah yake mana ni fa na fara shakku a raina.".
Juwairiya ta firgita da maganar da Mama ta yi mata ta san da ma dole ta yi mata waɗannan tarin tambayoyin game da kuɗin da A.m yake kashe musu ya wuce misali.

Ganin Mama ta fara zargi a zuciyarta sai ta daure ta kauda duk wani tsoro da shakku a ranta,ta kalli Mama da natsuwa ta koma ta zauna ta ce." Mama ki yi masa kyakykyawar fahimta kin san irin tarin kuɗin da suke da shi,sannan da zai cuce mu kuɗin ba zai biyo ta hannun Baba Sani ba.Don Allah ki kauda komai a ranki kuma in ma sabon gidan da ya gidan da ya siya mana ne ba kya so sai a mayar masa."
Da ƙwarin gwiyarta take magana saboda ta yi tunanin yanzu ita ace za ta din ga buga ƙwallon a

raga kuma in ba ta jajirce ba Mama za ta ɗago ta wanda hakan zai ɓata shirin su.

"Lamarin duniya a kwai tsoro ke yarinya ce amma ba zaki gane ba kuma da kike maganar Baba Sani ai duk kanwar ja ce,ke sheda ce akan halin sa kin san irin halaccin da mahaifin ku ya yi mishi amma ya manta ya kasa tallafar rayuwarmu,shirun da kika ga na yi hakan ya samo asali ne saboda alƙawarin da na yi ma mahaifin ki wanda ya tilasta min na yi masa daga baya na zo ina dana sani,amma wallahi kin ji na rantse da ban yi ma mahaifin ki alƙawari ba da na ɗauki mataki akan yadda ya hana rayuwarmu saƙat."

Ta ce ta na kallon Juwairiya da ta firfito da idanunta ganin yadda Mama take magana, saboda tsawon rayuwarta fa ita ba ta taɓa jin ta ɗaga harshe ba,sai yau lamarin ya matuƙar razana ta har ta fara dana sanin amincewarta don da wuya shirin su ya tafi ga shi A.m ya kashe kuɗin sa. Mama ce taci gaba da magana ganin ta yi shiru ta na zare ido sai ta ce." Wa ya sani ko kuɗin kammu muke ci."
Yayin da tsoro ya ƙara kamata tuna yanzu duniya ba gaskiya.

" Da ma Baba Sani zai yi miki bayani Mama ni ne na ce ya bari ki ƙara samun sauƙi Wato shi mutumim da yake taimaka mana ya auri matarsa wacce ƴar majalisa ce. To gabaki ɗaya rayuwarta  ƙasar waje ta yi karatu,ta samu gata sosai wanda hakan yake saka suna samun saɓani ga shi ba ta iya girki ba komai ba ta yi."

Ta yi shiru ta na son ta ji ko me Mama za ta ce amma sai ta ga ta tsaya ta harɗe hannunta a ƙirjinta ta na sauraren wannan tatsuniyar ita tunanin ta to meye haɗin ta da wannan dogon labarin wanda take ganin ina ruwan ta da labarin sa.

Juwairiya ta rasa in da za ta kama ta ci gaba da zancen a wannan lokacin ji take kamar ta ɗora hannu ta yi ta kuka ganin yadda Mama ta  kafe ta da ido.

" To saboda wannan ne ya na son a koya mata abubuwa da girki yake son ya s..."Juwairiya da ta ci gaba da magana sai kuma ta tsaya tare da sakin kuka wanda hakan ya ta da hankalin Mama, amma sai ta yi shiru ta na kallonta yadda take kuka mai sauti.

" Shi ne yake son mace wacce za ta zauna a gidan shi na shekara ɗaya ta koya ma matarsa girki da yadda ake kula da gida,na tsawon shekara ɗaya kuma duk wacce ta amince za ta yi zai tallafa ma rayuwar su,ban san tsinannen da ya gaya  masa halin da kuke ciki ba har ya zaɓi Juwairiya a matsayin wacce za ta yi,don wallahi da na sani ba zan bari ba ai gara na saka ƴata."Muryar Baba Sani suka ji ya na magana a bakin ƙofa.

Mama ta ji wani irin juwa ya kamata murna za ta yi ko farin ciki amma kuma Juwairiya ta din ga yawon aikatau kenan?Juwairiya a yanzu ya kama ta ace ta na ɗakinta,sai dai kuma mutumim ya yi hidima ga rayuwar su wanda wani ɗan'uwan ka ba zai iya haka ba.

Ta buɗe baki da nufin ta nuna rashin amincewarta amma sai ta kasa saboda ya yi musu halacci haka kawai sai ta ji ba za ta iya musawa ba,amma ranta ta saka dole in Juwairiya ta gama aikin ta za ta yi aure da irin mijin da take so ko da hakan zai saka ta karya alƙawarin da ta yi ma marigayin mijinta ne don za su raba abin faɗi ƙila kutu za ta raba su,saboda haƙurin abin da yake mata wanda sakamakon hakan ya sa zuciyarta ta buga.

Juwairiya ta shiga tsananin mamaki gani Mama ba ta ƙara ce mata komai ba ta takure gefe zuciyarta cike da tashin hankali,wani irin zazzaɓi ya rufe ta sai makyarkyata take hawaye ya na zuba a ƙuncin ta.

Mama ta yi jim da kofi a hannunta bayan ta ba ta magani tasha." Ni fa hankalina ya tashi Juwairiya ke ma kin yi gangancin karɓar wannan kwangilar duk da hakan ya tseratar da ke da ga auren wannan tsohon,amma kin manta irin wulaƙancin da dukan da kika sha a dalilin aikatau."

Juwairiya ba ta ce komai ba sai hawaye da suke shatata fuskarta.
Mama tace ta rasa wani irin tunani za ta yi akan maganar aikin Juwairiyar da za ta yi,kuma da ta nemi sanin waye hatta ita Juwairiyar ba ta gaya mata ba sai wani lulluɓin biri suke yi wa kare an ya? Akwa lauje cikin naɗi!Ta faɗi a zuciyarta cike da shakku.
Ta zauna a gefen gadon da take kwance tare da janyo mata bargo." Allah ya baki lafiya."Ta ce tare da zabga tagumi.

Wa su irin zafafan hawaye suka wanke mata fuska sai ta canza kwanciyarta saboda ta juya ma Mama baya." Ki yafe min Mama na san ban yi miki adalci ba,amma na yi hakan ne saboda na ceci rayuwar ku duk da hakan ni zai kai ni kushewata saboda ƙara kusanci da na yi da shi,shi zai jagoranci ruhina zuwa mutuwa.Allah na roƙe ka ka cire min son sa a cikin zuciyata."

*****

A.m zaune a tanƙamemen falon sa da remote a hannun sa gefe kuma Zainab ce take aiki da computa da ta ɗora a cinyarta,saboda gwanancewa da aiki da ita da ta yi ba tare da ta kalle abin da take daddannawa ba take aikin ta,yayin da hankalinta ya na kan A.m da yake ta jan tsaki ya na juyi a kujerar.

Talatu mai aiki wacce take sabuwar ƴar aikin da Mominta ta kawo mata saboda halinta sam ba ta daɗewa da me aiki.Ita ce ta yi sallama ta shigo idanunta akan A.m saura ƙiris ta yi ɓari amma sai ta ije ta ci gaba da kallon shi.

A.m wanda da ma hanya yake jira miƙewa ya yi ya kwasa mata mari ya ce." Wai ke wace irin mayyar yarinya ce ba na hanaki kallona ba!Banza ƙatuwa da ke maza fice min daga falo! Kuma yau zaki bar gidan nan."

Da sauri ta ruga ta na shafa gurin da ya mare ta don ta ji zafi sosai jikinta har rawa yake saboda ita duk ta gan shi,sai ta ji ta na  son ya kula ta duk da ta san shi ba san ta bane amma ya na da kyan da duk mace za ta yi mafarkin samun shi.
Zainab kuwa tsaki ta yi  a ranta ta ce." Haka kawai duk ka tsani ƴan aiki kullum cikin canza masu aiki muke wannan karan sai dai ka yi haƙuri amma ba zan canza ba."
Juya wa ya yi ya kalli Zey da ta daina aikin da take yi ta na kallon shi ya ce." Allah na tsani yarinyar nan ke duk masu aikin ki dangin mayu kike ɗauko wa,gaskiya ki sallame ta ni sam ma abincin ta ba ya min daɗi."

"To ni ya kake son na yi ko ni kake son na dun ga yi maka girkin?"Ta ɗan saki dariya ta  ci gaba da magana ta na ce wa." In haka kake tunani gara ma ka cire har na yi aure ban taɓa shiga kicin da nufin na yi girki kai ko ruwan zafi ban iya dafawa ba,ka ga ya zama dole ka ci na ta in ba so kake ka ɗauko kuku namiji ba wanda da ma kafiyarka na tsiya da baƙin kishi ya hana ka,amma ni ban ga dalilin da ya sa ka za ka ƙi ɗaukar kuku namiji ba a gidammu su suke girki ni kai na na gaji da cin abincin masu aiki."

Wani kallo ya watsa mata ya ce." Zainab ki kiyaye ni da maganar kuku a haka yadda kike zama kusan naked ne zan ɗauko kuku,matan ma da suke kallon ki ni na san baƙin cikin halin da nake shiga sai dai na lura shashasha ce ke kin ɗauki rayuwar yahudu da nasara ba ki san darajar kan ki ba."

"To aiko ka na ruwa wallahi tunna duk yawon duniya da ka yi baka waye ba ni ban ga dalilin da zai saka kasa na din ga ɓoye kai na ba kamar wata ƙonannniya."
Ta ba shi amsa cike da gatsali ta na girgiza ƙafa.

" Karyar iskanci kike tunna kin nuna ba za ki canza ta ba sai dai ki zaɓa ko aikin ko ki zauna ki rinƙa dafa min abincin da kanki,tun da na tashi na ga iyayena suna girki a gidammu amma ke saboda sakarci ki ce ba ki iya ba.Ki na ganin ƙannina duk sun iya girki ke na rasa wani irin tarbiya kika samu. "
Ta katse ta hanyar ɗaga masa hannu ta ce."Ka dakata kar abin ya zama cin fuska kuma da kake wannan maganar ai ka san wacce kake aure da matsayin ubana."

"Dallah rufe min baki ke ma kin san sai dai ki yi min gori na mahaifin ki ya riƙe muƙami,amma ba wai ko kun fi mu kuɗi ba iya tarbiya ne kawai da muka hora su da shi, saboda arzikin da muke da shi bai saka ya sa mun yi watsi da al'adarmu ta yi ma miji girki."

Tsaki ta saki ta ci gaba da aikinta ta na faɗin." Ai sai ka yi ba ka da aiki ne ni ina da abin yi kamar yadda ka gani."Ta ɗan ƙara sakin ƙaramin tsaƙi  a hankali ta ce." Jarababbe kawai."

Ya kalle ta ya na baƙin cikin halin ta don shi bai yi tunanin halinta haka yake ba."Mu zuba da ni dake tunna baki da mutunci kuma da ga yau in kika ƙara zuwa wani guri bayan akin ki Allah

y...."

Da sauri ta tashi ta waurgar da ƴar mini system ɗin dake hannunta tare da faɗawa jikin shi ta rufe bakin shi jin zai kafa mata dokar fita,in ta bari hakan ya faru ita kuwa ya za ta yi da zuwa pati da yawaon da suke da ƙawayen ta.

" Haba mai sanyina don Allah ka yi haƙuri karka faɗi haka kai ma ka san wallahi ban saba zaman gida ba,in ka hanani fita ya zan yi kuma ka san kai ma zaka saka Allah ya yi fushi da ni ne,amma na riga na saba da yawo ba zan iya zama guri ɗaya ba ko da ka rantse."

Ya kalleta da mamakin abin da ta ce ba yan Allah ya jarabce shi da sonta ya riga ya rufe mishi ido da sai ya ce bai yi dacen macen ƙwarai ba,amma so makoho har zuciyarsa ta sauko ya kalleta da shauki ya haɗa hannunta duka ya na murxawa da hannunsa don ya na ganin damar sa ne yanzu ya ce.

" Na lura don kin ga  ina son ki shi ya sa kike wahalar da zuciyata Zey amma ba komai  ina fatan Allah ya saka miki irin son, da nake miki a zuciyarki nawa zaki gane halin da na ke ciki."Ya faɗa ga mamakin ta sai ta ga yana hawaye.
Hankalinta ya tashi ta ƙara maƙalƙalewa a jikinsa ta na share masa hawaye saboda jikinta ya mutu murus da son sa.

" Ni ma fa ina sonka hubby kai ɗin ne ka cika faɗa ba ka min uzuri duk da ƙoƙorina da nake kuma ka san yanayin aikina.

Janye hannunta ya yi akan fuskarsa aran sa ya na faɗin." Na sani amma kuma hakan bai hana ki fita ba."

A fili kuwa sai ya saki ɗan murmushi kamar ba shi ya gama hawayen baƙin cikin Juwairiya za ta shigo duniyar auren su ba wanda ya ɗora laifin duk akan Zainab amma sai ya ce.
" To ki canza me aiki ni bana son wancan yarinyar k..."

Ta ƙatse shi ta na faɗin ."Na ji zan canza amma kuma Momi ta ce in dai muka kori wannan ba za ta ƙara ne mo mana mai aiki ba tunna ba ni da haƙuri."

" Kar ki damu dama tuntuni nake son na tambaye ki na yi ma Atine mai aikin gidammu ta kawo mana macce matashiya wacce ta iya girki sosai,in kin bani dama sai na gaya mata ta nemo mana kuma ba za'a daɗe ba, za ki ga ta kawo mana tunnna ita ma ta na irin kawo su kusan family mu ita take kawo musu masu aiki."

Ya ce tare da rungumeta ya na goga fuskar shi a na ta."Ok ba komai sai ta kawo mana amma ba za mu kore ta ba sai an kawo mana wata."

A.m hamkalinsa ya kwanta ganin bai sha wahalar samun haɗin kanta ba miƙewa ya yi ya shige ɗakin sa,ya gallah wanka ya fice kai tsaye gidan su ya wuce ya sami Atine mai aiki ya ce." Ina son in kika tashi zamu fita da ke zuwa wata unguwa amma ya zama sirri a tsakanimmu in kika yi min hakan zaki samu alkhairi."

"Ka faɗi ko mene ne in sha Allahu zan yi maka."

Ta ce cikin mamakin in da za su kuɗi ya zaro masu yawa ya ba ta.Atine jikinta na rawa ta karɓa ta na kallon shi." Wata yarinya nake son na nuna miki ki kaiwa Zainab a matsayin ƴar aiki.Shikenan buƙata ta kuma ba na son kowa ya sani kawai ki bar shi a matsayin ke kika kawota."

Duk da mamakin maganar da ta yi amma tunanin ta bai kai ko ina ba,ta amince masa akan sai ya zo daga ƙarshe watsar da tunanin ta yi don ta san ya wuce ƙarfin ya kula ƴar aiki ,kasancewar yadda ta ga ya na hantarar su bare ma ta yi tunanin wani abin.

********

A ranar da Juwairiya za ta tafi hankalinta ya tashi matuƙa wanda da Mama ta so taƙi kan ta din ga kwana duk da a kwai nisa sosai ta so Juwairiyar ta din ga zuwa ta na kwana har shekara ɗayan ta yi,amma sai Baba Sani ya kafe dole sai dai ta din ga kwana tunna kuɗi ya biya.

TO MASU KARATU GA DAI AMARYA JUWAIRIYA ZA TA TAFI GIDAN ANGONTA KO YA ZAMAN SU ZAI KAYA ?SAI KU CI GABA DA BIBIYAR LINTAFIN SAKACI KO HALIN MAZA

.
Follow this link to join my WhatsApp group:
https://chat.whatsapp.com/LQfVU1ABdFI14btWRhUB1K

*SAKACINA KO HALIN MAZA?*

*RUBUTAWA:-*
*JAMILA LAWAL ZANGO*

*SADAUKARWA GA:-*

*SUMMY M NA'IGE*
_(Aminiya)_

*FIRST CLASS WRITER'S ASSO....*

*Page 17*

BISMILLAHIR RAHAMANIR RAHEEM

Juwairiya ta yi tsuru da jakarta ta na kallon Mama da ke tsaye a gefen ta riƙe da hijabin ta a hannu ta na ƙoƙarin saka wa a kanta sai ta ji hawaye sun ƙara wanke mata fuska,ta share da sauri domin Mama tun ɗazu take mata ƙorafin kuka yanzu ma da taga ta na hawaye sai ta yi tsaki ta ce." Gaskiya kukan nan na ki ya fara siƙe ni Juwairiya na ga ke da Baba Sani kuka shirya hakan,amma kin bi kin dame ni da kuka in da kin san ba za ki iya ba uban wa ya ce ki amince."

Sai ta rungume Mama ta ƙara fashewa da kuka ta na jin wani irin baƙin ciki da fargaba ga gabanta da yake faɗuwa a kai akai don ji take kamar ta ce a ta fasa.
"Mama akan ki sami lafiya na amince amma ki yafe min in na ɓata miki na ga kamar ran ki ba ya son na tafi."Ta ce da ita cikin hawaye fuskarta ta tura shi a jikinta.

" Ki na ganin in da bai yi wa rayuwarmu halacci ba wallahi Baba Sani bai isa ya saka ki ƙara wani aikatau ba,don kullum na yi sallah sai na roƙi Allah ya raba ki da shi saboda irin cin mutuncin da kika fuskan ta."
Share hawayenta ta yi ba ta ce komai ba ta shafa kan Ibrahim tare da riƙe hannun sa suka fito tare.

" Mama ji nake kamar kar na tafi sai kun tare a sabon gida."Ta faɗa tare da fuska.
Mama ta kalle ta ta ce " Gara ki tafi Juwairiya saboda yau aka yi zaki tafi kuma kin ga mutumim nan ya yi ma rayuwarmu hallaci wanda dalilin haka ina matuƙar girmama shi."

" Humh." Ta ce a cikin zuciyarta sannan ta ɗora da ce aranta jin abin da Mama ta ce." Da kin san abin da ya ƙulla da ba ki girmama shi ba,shi ɗin macuci ne sosai ya fiye son kan sa da rayuwar matar sa da kin san dalilin da ya sa ya yi mana wannan abubuwan da kin tsane shi har iya ƙarshen rayuwar ki."

A lokacin da suka yi nisa mama ta kama hannunta ta riƙe sai hawaye ta ce." Juwairiya ki riƙe

mutuncin kan ki a duk in da kike kuma, duk abin da ki kai kin san Allah ya na kallon ki mutunci na ƴa mace shi ne zai zama ado a rayuwarki,ba wai ina zargin ki ba ne a' a ina miki nasiha a matsayina na uwa wacce ƴarta za ta yi nesa da ita,sannan ya zama dole na saki a hanyar daidai don kar ki ga mutum zai aikata abu a ɓoye,ya na tunanin ya kauce idon mutane bayan ya manta mahaliccin sa ya na ganin duk abin da ke"

Jikin Juwairiya ya ƙara sanyi kamar ƙanƙara haka kawai sai ta ji ta fara tsarguwa yadda Mama take ta mata wasu irin maganganu, wanda take shan jinin jikinta don in ta yi mata irin waɗannan maganganun ko kallonta ba ta iya wa.
Yanzu haka ta kasance ta yi ƙasa da idanunta ta ce."Mama an ya ba zan."
Katse mata hanzari ta yi tare da taran ɗan mashin ta karɓi jakarta da ta riƙe da ta yi tsumu ta ɗora a kan mashin ɗin sannan ta kalle ta ta ce." Ma za ki tafi Allah ya tsare da kin sami lokaci ki leƙo."

Juwairiya ta haye mashin jikinta babu karsashi hawayen fuskarta sun ci gaba da kwaranya yayin da ɗan  mashin ɗin ya fara tafiya a kan titi.
Wani ƙarin abin da ya ƙara zubar hawayenta cikin ƙunar rai da ta tuna yau gidan mijinta za ta akan mashin da ƙullin kaya a jaka, ba tare da an kawo mota kamar yadda ko wace mace mai gata wacce mijinta yake son ta ake mata,duk lokacin da ta tuna wannan sai ta ƙara sakin kuka har ɗan mashin ɗin ya juyo ya kalle ta ya na faɗin."
Lafiya Hajiya?"

Amma ba ta kula shi ba kuka sosai take har suka isa gidan Atine,a lokacin da ta isa ba ta nan sai da ta jira ta sannan ta dawo sallah ta yi suka kama hanya.

Wani irin faɗuwar gaba take yi har sai da ta dafe ƙirjinta.Kasancewar a kwai tazara sosai da gidan Atine sai da suka hau nafe.

A lokacin da suka iso ƙofar gidan da Juwairiya ta saka a ranta na A.m ne hankalinta ya yi matuƙar tashi matuƙa gaya.Kawai sai ta ji ƙasa ba za ta iya ɗaukar ta ba ta sani A.m suna da kuɗi amma ko kaɗan ba ta taɓa tunanin haka gidan sa yake ba.

" Dole ka ce baka sona kuma ba zaka taɓa sona ba saboda ba mu dace ba ni kai na sheda ne."

Ta furta cikin karayar zuci don ta san ya fi ƙarfinta na har abada.Gaskiya fasalta gidan sa abu ne da zai ɗau lokaci saboda gida ne mai matuƙar girma, da tsari ga shukoki masu kyau waɗanda suka ƙara ƙawata gidan,don haka mai karatu na bar maka aikin tsara fasalta iya tsaruwan gidan,A.m a hannun ka don in na ce zan yi zan ɗauki lokaci ni dai na yi wa gidan suna da aljarnar duniya.

Lokacin da suka shiga cikin falon Juwairiya ku san neman numfashinta ta yi ta rasa, don barazanar shiɗewa yake yi saboda tsaruwar falon da ke ɗauke da ku san set huɗu na kujeru mabambanta.

Duk lokacin da ta ƙara taku a cikin falon zuciyarta karaya take da son A.m da ya shige zuciyarta saboda ta hakiƙance ma kanta da yaudarar kanta take yi A.m babu abin da zai yi da ita.

A ƙasar kafet ɗin dake zagaye a tayas ɗin da ya sha guga ya na ta ƙyalli da ɗaukar ido ta zauna tare da rintse idanunta,hakan ta ji ba ta son idanuwarta su yi tozali da matar A.m don ta san zuciyarta za ta buga.

Atine ta zaro wayar ta ta yi kiranta sai dai cikin takaici ta ije wayar ta kalli Juwairiya ta ce." Ba ta dawo aiki ba amma ta ce mi jira ta za ta duba patient ta dawo."

Sai Juwairiya  ta sauke idanunta daga kallon Atine saboda kiran sunan ta da ta yi,ta ci gaba da kallon ƙasa yayin da zuciyarta yake bugawa tamkar za ta fito.

Kusan waya biyu suka shafe suna zaune a falon sai kowa shiru jefi-jefi Atine take sakin tsaki,amma Juwairiya iya tsawon lokacin ko tari ba ta yi ba sai sautin bugun zuciyarta da yake ta ƙara tsanantuwa.

Ƙwas!Ƙwas!!Ƙwas!!! Suka ji sautin takalmi wanda Juwairiya ta sadaƙar da matar gidan ce ta dawo,bayan iya tsawon lokacin da ta ɗauka ta shanya su zaman jiran ta kamar wasu dussa.

Bugun takalmin Zainab ya na tafiya tare da bugun zuciyar Juwairiya da take jin tamkar za ta fito,ta rintse idanunta ta na burin a ce ba Zainab ɗin ba ne take ƙoƙarin shigowa,domin tsoro ya bayyana a fuskarta sai take ganin kamar za ta gane dalilin shigowar ta gidan.

Koda ta shigo waya take yi zama ta yi ba tare da ta ce musu komai ba ta ci gaba da wayar ta.

Juwairiya ta kasa ɗago idanunta ta ga matar mijinta na wucin gadi wanda take cikin zuciyar sa yake fifita ta fiye da komai har ya zaɓi ya cutar da rayuwarta duk akan ya farnta mata.

Amma idanuwanta sun kasa haɗa ido da ita hasalima ko ɗagowa ba ta yi ba, duk da ta  fahimci ta gama wayar da take yi bayan ta ɗauki rabin awa.

" Am Atine na ɓata miki lokaci ko?"

Tambayar da ta yi mata kenan ta na kallon matar da ta kusa jika da ita a yatsine.
" Ba komai Hajiya dama me aikin ne da muka yi magana da megidan ki na kawo miki."Ta ce mata ta na kallonta.
" Ok."

Abin da tace kenan ta janyo wayarta ta kunna data yayin da tsaƙwanni suke ta shigowa ta na duba wayar har na tsawon lokaci,daga bisani ta kashe ta kalle su duka daidai lokacin da Juwairiya ta yi sa'ar yaƙar idanunta, na tsoron haɗa ido da ita da suke ta kalle ta, don ta ga

wannan mace mai ji da kanta da wulaƙan ta mutane.

Karab idanun su duka suka haɗu da juna Juwairiya da ƙyar ta yi nasarar daƙile gangar jikinta da yake shirin tashi da zura da gudu ganin kalar matar da A.m yake aure.
" An ya ƴar Nigeriya ce?"

Ta tambayi kanta cikin tsananin mamaki domin yanayin ta da kyanta surar ta gabaki ɗaya ya tsorata ta,saboda hasken ta har wani kashe ido yake yi sosai da ta yi duba ga kalar fatar jikinta sai ta ga ta yi baƙa wuluk kamar gawayi,duk da ya ba kyan fatarta da ƙawayenta suke yi.

Zainab kuwa wani irin tsanar ta ya shiga ranta haka kawai sai ta ji ba ta kwanta mata ba,ba wai kuma kyan da ta gani ba ne ya tsorata ta a'a ita sheda ne akan A.m ko ƴan mata larabawa za ta kawo mishi ba zai yi dubi garesu ba, duba ga yadda ta sha wahala kafin ya amince da ita sannan tun da su kai aure ba ta taɓa jin ya yi maganar wata ko wata ta kira shi ba.

Amma sam Juwairiya ba ta yi mata ba saboda daga ganin ta za ta yi munafunci ganin yadda take duƙar da kanta ƙasa-ƙasa.
" Atine an ya wannan ƴarinyar kina ganin ta yi?Kin san A.m a kwai shi da ƙyanƙyani ji yanayin shigar ta da wani zumbulelen hijabi kin san ya na da tsafta, kar ta zo ta na ma na girki ya na shiga sannan wallahi zubin ta bai yi min ba don ni na daina ɗaukar ƴan aiki gidahumai ƙauyawa,bai gaya miki ɗakin sa da komai na shi ita za ta din ga gyarawa ba?A can zo wata kawai."

Juwairiya ta yi ƙasa da kanta jin abin da ta faɗa duk da ranta ya ɓace,amma ta yi tunanin fiye da hakan a gurin ta saboda ta karance ta tsaf mace ce mai ɗagawa da nuna ta isa,musamman ga talakawa ƙasƙantu irin ta.

Sai kuma ta ji daɗin abin da ta ce ranta ya yi fari ko banza ba za ta zauna  agidan wannan mai kama da canis ba sai ya zo ya san yadda zai yi da ita,ai dama abin da ya shirya a yi mata kenan shi ya sa ya aure ta ya kawo ta kuma ita ta sai ma kanta don in da ƙwaɗayi a kwai wulaƙanci!

Atine ta ji jikinta ya yi sanyi sosai har ta fara tunanin in da za ta samu kuɗin A.m ta mayar masa don ya na ba ta ta kai ma mai kujeru akan bikin ƴarta marainiya wanda mijinta ya mutu ya bar mata.

Sai ta ji kamar ta ce ai mijin ta ne ma ya buƙaci ta kawo ta,amma da ta yi tunanin ba ta san dalilin da ya sa ka shi ya buƙaci hakan ba sai ta kama bakinta ta guntse ta ce." Ai Hajiya Juwairiya a kwai aiki da tsafta sosai ta yi aiki da dama shi ya sa na kawo ta,kuma za ki ya ba sosai sai kin gode min,amma ki gwada ta in ba ta yi miki ba sai a kawo wata.Kin sai an gwada akan san na ƙwarai.

" In ko haka ne ta na buƙatar gyara don sai na canza mata tufafi ba za  din ga mana girki da shi

ba,ni ban san daƙiƙanci da rashin wayewa."

Ta ce ta na kallon Atine da ta yi hamdala a ranta jin ta amince da ita,sai kuma ta kalli Juwairiya ta na mata kallon tsaf irin na ciki da waje har mutum ya gano munin ka.

" Ina yini"

Juwairiya ta ce mata ganin ta na mata kallon ke ba kya gaisuwa ne.

Ɗauke idanunta ta yi ba tare da ta amsa gaisuwar ba duk da ta tabbata ta ji gaisuwar da ta yi mata.
Sai ta miƙe ta kalli Atine ta ce."Wash na gaji ba ri na shiga ciki."Har ta fara tafiya sai ta tsaya.
" Ina fatan Atine ta yi miki bayanin aikin da za ki din ga yi a gidan nan? Ina da da tsohuwa da take share-share da ƴan abin da ba'a rasa ba.So ke aikin ki kula da ɗakina da na mijina da wankin underwears ɗin mu da girki.Kasancewar ba zama nake ba don yanzu waje zan fara fita na baki amanar gidana, da mijina duk sanda ba na nan ki rinƙa kula da abincin sa ruwan wankan shi kayan sawan shi da wanda ko ina nan ke zaki kula da wannan."

Ta ɗan numfasa ta ɗora da ce wa " Game da kayan sawar shi irin wanda yake so ina fatan ke ba daƙiƙiya ba ce kuma  ba' a yi asaran tara ba na yi mishi time table a ɗakin sa na kayan da yake saka wa sai ki din ga dubawa ki na cire masa."

Wani iri Juwairiya ta kanta ya yi mata take wani irin zafin kishin mijinta A.m ya taso ya mamaye zuciyarta,har ya hana ta jin abin da Zainab take ce wa sai kuma tausayin sa ya kamata matuƙa jin irin ballagar mace da yake aure.

Ta ƙara rintse idanunta ta na jin kishin iya adadin masu aikin da Zainab ta yi waɗan da suka gama kallon mata miji,kuma a haka yake iƙirarin ya na sonta lallai ta yadda  so halitta ce kuma makaho ne.

" Ki na ji na ina magana kin yi banza da ni!"

Zainab ta daka mata tsawa ganin ta tafi duniyar tunani.

" Yi haƙuri ina sauraren ki ne."

To ba na son shashanci in ina magana duƙar da kunnin ki saitina za ki yi kuma duk na yi magana ki ɗaga kanki."
Ta ce sannna ta ci gaba da tafiya ta na faɗin." Atine ba ri na ɗauko miki abu."

" Kut! Na shiga uku A.m ya san halin matar sa ya kawo ni cikin gidan nan."

Ta faɗi ta na jinjina kanta tare da tunanin irin zaman da za su yi da ita .A jiyar zuciya ta saki mai

ƙarfi jin sakacin da Zainab ta yi da mijinta.

Kuɗi masu yawa ta miƙa ma Atine wacce ta sandare da jiranta,saboda har wanka ta yi ta saka kaya shara-shara wanda al'dar ta ce zama da irin wannan kayan a gida.

A lokacin Juwairiya ta gaji har ta fara gyangyaɗi ga yunwa dake ta ƙwaƙwular cikinta.

" Kin ga na jima ban dawo ba ruwa na watsa ga shi ki yi haƙuri."

Ta ce da Atine sannan ta kalli Juwairiya ." Ke ki tashi ki fara aiki kuma na manta ban gaya miki ba! Ba na son raini da ƙazanta."

Sai kuma ta ƙwala ma Baba mai aikinta kira da gudu sai ga shi ta ƙaraso mari ta zabga mata.Banza daƙiƙiya ba na ce miki za'a yi sabuwar mai aiki ba? Da kika gan su sai ki fara nuna mata aikin gidan ko sun yi miki kama da irin baƙin da zan yi ne?"Ta tambayeta ta cikin zafin rai.

"Ki yi haƙuri Hajiya ai ba ki bani umurnin haka ba kuma..."

" Rufe min baki banza maza ki je ki nuna mata."

" Allah ya huci zuciyar ki."

Ta ce tare da kallon Juwairiya sannan ta ce ." Mu je na nuna miki aikin."

Juwairiya da ta yi mutuwar tsaye ta dafe ƙuncinta don gani take kamar ita ta mara.Zainab ciki ta koma tare da ɗaukar wayarta ta yi kiran rabin ranta.
Tsananin tashin hankali Juwairiya ta shige shi ji ta yi tamkar ba za ta iya rayuwa a cikin gidan ba,a tare suka share hawaye da Baba suka kuma kalli juna.

" Ki yi haƙuri Baba haka matar gidan take miki?Gaskiya ba ta da mutunci a matsayin ki na wanda kika haife ta.Wai mai masu da shi suka ɗauki talaka shi ba mutum ba ne don kawai ya na nema a ƙarƙashin wani sai wulaƙanci."

Baba ta share hawayenta ta kama hannun Juwairiya ta ce " Humh ba zaki gane ba ne!Hajiya Zainab ta wuce tunanin ki ina tausaya miki wallahi Allah ya sa kin iya girki."

Ta ɗan ƙara matsowa kamar ta na tunanin Zainab za ta yi musu laɓe ta ce." Ina gaya miki wacce ta kora ta kawo ki da ta yi abinci juye mata ta yi a jikinta,ta rufe ta da duka wai mijinta ya ce ba ta iya girki ba.Ni fa ban taɓa ganin mutum irin maigidan nan ba,ya tsane mu sai dai shi baya duka."

Duk da Juwairiya ta san matsayinta a gidan amma sai da gaban ta ya faɗi ras!Shiru ta yi ba tare da ta ce komai ba.

Da Juwairiya suka shiga kicin kusan ruɗewa ta yi kamar za tai hauka,irin dukiyar da aka narka da kayan na'ura,duk da ta yi aikatau gidan masu kuɗi ta san yadda ake sarrafa na'ura amma a ranar yar ƙauye ta dawo.

Abinci mai rai da lafiya Juwairiya ta shirya sannan ta shiga ɗakin da aka ba ta wanda Zainab ta yi mata umurnin duk ta yi girki ta yi wanka.

Juwairiya ta da fari kasa amfani da kayan bayin ta yi sai daga baya a hankali ta fara gane yadda ake amfani da shi bayam ta ɓata lokaci ta na ƙauyanci.

Juwairiya ta yi mamakin irin kayan da ta jibga mata da sunan ta dun ga amfani da shi,haka dai ta shirya ta na ta tunani barkatai a ranta yayin da kewar su Mama ya kamata, matuƙa har ta ji hawaye na zuba a ƙuncinta.

Juwairiya na zaune a ɗakin da ya zama mallakinta bayan ta idar da salla sai kuma ta miƙe da sauri jin kamar Zainab na kiran ta.

Ta na baƙin ƙofar fita daga ɗakin suka yi kicibis da ita za ta shigo." Ke kurma ne ina kira kin yi banza dani."

Ta faɗa cikin ɗaga murya." Ki yi haƙuri ban ji ki ba ne."
Ta ce ta na kallonta amma kuma a tsorace take saboda kar ta kai mata mari.Tsaki ta yi." Maza ki je ki shirya dinning za mu ci abinci mijina yanzu zai shigo.Kuma ki cire wannan ƙazamin hijabin na ki don na san ina ya gani ba  zai iya cin abincin ba."

Juwairiya ta ji jikinta ya yi sanyi jin umurnin da ta ba ta domin ba za ta iya fita a haka ba,amma sai ba ta ce komai ba ta saɓule hijabin ta koma ciki.

Hankalinta ya kwanta da ta tuna a kayanta a kwai hijabi wanda bai kai wancan tsawo ba,da sauri ta ɗauko ta saka a jikinta bayan ta saka turare kamar yadda ta murceta.

Juwairiya na gyara dinning ta ji dirin mota alamun an shigo da mota,gaban ta ne ya faɗi ras! Don jikinta ya ba ta masoyin ta ne ya dawo haka kawai sai ta ji gaban ta na faɗi.

Da sauri take shirya dinnnig ɗin saboda ta gama ta kauce ma ganin sa,amma sai kafin ta gama ya riga ya shigo ya na takun sa da sarsarfa irin na ingarmar namiji mai jini a jika.

Shigowar sa ya yi daidai da fitowar Zainab daga cikin ɗakinta cikin wata irin shiga ta alfarma,amma fa a gurin sa wanda kuma Juwairiya ta ga bai kamata ta fito da irin wannan

shigar ba,sanin a kwai ta a cikin gidan don har tafi shigar ɗazu rashin kyan tsari.

Da gudu ta faɗa jikin sa ta na dariya cikin farin ciki.
Shigowar sa ya sa Juwairiya ta gane ashe tafiya ya yi saboda direban sa da yake janye da troley ɗin sa guda biyu kuma masu girma.

Duka suke dariya sannan suka faɗa kan kujera suna bayyana iya kewar da sukai ma junan su.

A hankali A.m ya zura ma Juwairiya ido shi har ya manta sun yi da Atine yau za ta kawo ta.Ya ɗauke idanun sa da sauri ganin Zainab ta bi in da yake kallo.

" Hubbina sabuwar mai aikin da Atine ta kawo mana ne,Allah ya sa ta yi maka sai dai na ganta kamar gidahuma ce ko ina yawo da hijabi,amma haka zamu yi haƙuri da ita don gaskiya na gaji da ɗaukar masu aiki."

A hankali Juwairiya ta ɗago idanunta  ta ɗara su akan A.m duk da ba ta son hakan,amma ta na son ta ji mai zai ce mata.

Ga mamakinta sai ta ga ya taɓe bakin sa ya kalle ta kamar ya ga kashi ya ce." Uhm na gan ta sai dai ki yi mata magana ta kiyaye sosai in kuma taƙi dole ki canza wata don kin san halina."Ya ce a taƙaice sai kuma ya canza maganar ya na kallon Zainab ya ce." Na yi missing ɗin ki babyna sati ɗaya da na yi kamar na yi shekara,yanzu haka ma ban gama abin da na ke yi ba na baro A.k a can na dawo na ga kyakykyawar fuskar ki."

Ya faɗa kamar zai yi mata kuka yayin da idanunsa suka bayyana hakan ga Zainab da take kallon sa da wani irin murmushi ta na kashe masa ido.

" Allah ko zauji ka san ni da kai kamar hanta da jini ne ɗazu ina ma wani operation, ka san Allah saura kaɗan na yanka sa ba in da ya kamata ba kuma fa kai na ke tunani."

Dariya suka yi duka ya riƙe hannunta ya ce." Na san za ki yi fiye da hakan akai na amma ki kula rai ya wuce wasa."

" Ke banza wawiya!Ba ki da tarbiya ko?Ko baki ko ya a gida ba in ma'aurata suna magana ki ba su wuri maza wuce daga nan stupid kawai!"

Juwairiya da ta yi mutuwar tsaye tun lokacin da A.m ya shige ta nemi hankalinta ta rasa ji take kamar ta ruga da gudu ta faɗa jikinsa.
Gabaki ɗaya ta manta a wace duniyar take wasu irin zafafan hawaye ta ji ya wanke mata fuska, saboda tsananin son da take masa wani irin kishin sa ya tokare mata maƙogaronta, har ta ji ta na son ta yi aman sa don ta na jin ɗacin sa ya na hawowa bakinta.

Muryar Zainab da ta daka mata tsawa ya fargar da ita halin da take cikin da sauri ta ruga da gudu,ta shige ɗakinta har ta na bugewa da bango ƙum!Amma ba ta kula ba don tsoron Zainab take yi sosai a ranta.

Ta na shiga cikin ɗakinta ta fasa kuka sai kuma ta toshe bakinta tuna ko a ina take daga ƙarshe toleit ta shige, ta kulle ta ƙara sakin kuka ta na buga kanta a bango amma ba ta kula ba ko kaɗan.

" Na shiga uku a haka zan rayu a gidan nan? Na tabbata zuciyata ta kusan kamuwa da hawan jini!Allah na roƙe ka ka yafe min laifin da na yi maka ka haɗa ni da A.m wanda da ma burin sa ya kawo ni gidan sa kishin sa ya yi ajalina!"

TO FA JUWAIRIYA AN YA DAI? GARA DAI KI TSAYA A MATSAYIN KI KISAN KE FA AUREN GWANGILA CE AKAN KI AMMA BA MATAR SO BA.INA JIRAN COMMENT TSAKANIN FANS ƊIN ZAINAB DA JUWAIRIYA.

TAKU

JAMILA LAWAL ZANGO

ƊUBBIN GAISUWA GARE KU SABODA COMMENT ƊIN KU YA NA SAKA NI NISHAƊI.

MAMAN SUDAIS
AISHATU MINNA
FATIMA ZARA JOS
SAHURA NURA RABIN RAINA
NABILA MAMAN SAFWAN
HAMDIYA UMMU ABDULHAKIM

*SAKACINA KO HALIN MAZA?*

*RUBUTAWA:-*
*JAMILA LAWAL ZANGO*

*SADAUKARWA GA:-*

*SUMMY M NA'IGE*
_(Aminiya)_

*FIRST CLASS WRITER'S ASSO....*

*Page 18*

BISMILLAHIR RAHAMANIR RAHEEM
Tun daga wannan ranar Juwairiya ba ta ƙara saka shi a idonta ba wanda hakan ya tabbatar mata da tafiya ya yi tafiya, ita ma kan ta mai gidan ba zama take ba tun safe in ta fita sai dare za ta dawo,ta kwashi abincin da Juwairiya ta dafa,wanda tun daga ranar farko ta yi amanna da abincinta mai shigen daɗin tsiya,don ko A.m da ya ci ya yaba sosai ji ya yi abincinta ya yi kama da wanda yake ci a gidan iyayen sa.

Rashin zaman mutanen gidan haka ya ba Juwairiya damar sakewa a gidan kamar na ta ba ta da wani matsalar takura.

Juwairiya a ɗan zaman da suka yi da Zainab ta gane ko ita wace ce mace mai son hutu da gata,ga shi ta tsani zaman gida ko da ace mijinta na nan ga ta da shegen son ƙwalama kullum ta na yawon siyo kayan daɗi da ciye-ciye.

Juwairiya ta ɗauki tsawon wata ɗaya a gidan a cikin wata ɗaya ta ƙara kyau da kuma irin mai da cimar da take yi,ita kanta in ta kalli kanta a madubi sai ta ƙara juyawa ta kalli kanta cikin jin daɗin yadda ta sauya,wanda har take zolayar kanta da in ta je gida Mama ba za ta gane ta ba.

Juwairiya ba ta da son jiki ku san duk wani aikin gidan ta ɗauke shi shi ya sa kullum gidan ya ke cikin tsananin tsafta da ƙamshi, ita kan ta Zainab kullum yabawa take sai dai tsabar girman kanta ba ta taɓa nunawa ba.

Aiki ɗaya da yake ɓata ranta shi ne gyaran ɗakin A.m wanda kullum ta shiga sai ta yi kuka sosai,musamman da Zainab komai ba ta ɗaukewa sai ita take gyarawa cikin kuka da zafin kishi.

Ganin yadda Juwairiya take da hankali da natsuwa ga shi mijinta ya yaba kuma har ya yi tafiya bai ce komai ba,sai Zainab ta ɗan saki jiki da Juwairiya kaɗan duk da ta san rabuwa za su yi saboda ta isa aure,don haka ta yanke shawarar za ta ɗauko yarinya ta haɗa ta da Juwairiya ta din ga koya mata girki da yadda take gyaran gidan,saboda ko baƙi ta yi sai sun ya ba gidanta.

Ta na tsaye a kicin ta na tunanin abin da za ta dafa sai ta ji Zainab ta ƙwala mata kira,da sauri ta ruga kamar yadda ta buƙata duk lokacin da ta yi kiran ta.

Ba tare da ta kalle ta ba ta na riƙe da jaka ta ci uwar gayu ta ce " Fi ta zan yi yau zauji ya na hanya don haka ina son ki shirya abinci masu daɗi."Fita ta yi ba tare da ta ji mai ta ce ba.

Kwan biyu da dawowar shi da rana ta na shirya abinci a falon cikin sauri take son ta yi ta kammala kafin ya fito,wanda ta yanke shawarar haka ya dace ta din ga kauce mishi ƙila zuciyarta ta huta da raɗaɗin son da take mishi.

Ta na cikin shirya abinci kan dinning ta ji ƙarar kiran waya ya shigo sai ta shiga dube-dube a tunanin ta wayar Zainab ce ta manta fa ita,don sam ba ta kula da A.m da yake bacci ta bayan ta akan doguwar kujera.

Sai dai jin ƙarar wayar ya sa ta gane ba ta Zainab ba ce, wanda kuma haka ya ba ta damar fahimtar a kwai mutum a cikin falon.
Kiran wayar ya sa shi juyawa da nufin ya kashe wayar saboda a gajiye yake matuƙa! Kwanan nan sam bai samu ya huta ba,ya laluba wayar sa da nufin ya janyo wayar ya kashe bai jita in da yake tsammani ba,tunawa ya yi da jifa da ita da ya yi lokacin da ya shigo cikin falon.

Sai ya buɗe idanun sa a wahalce ya na waigen in da yake jin ƙarar ta amma tsabar gajiya ya saka shi kasa motsa jikin sa ya ɗauko wayar.

Ganin haka sai ta nufi in da wayar take ta na neman agaji ta ɗauko masa tare da miƙa masa,yayin da idanunta suke cikin na sa kuma ta kasa ɗauke ƙwayar idanunta ga barin kallon sa.
Idanu suka zuba ma junan su na tsawon lokaci wanda hakan ya sa Juwairiya ta rasa natsuwarta,shi ya fara ɗauke idanun sa ya lumshe su.

A hankali Juwairiya ta tako ta miƙa masa wayar da ta ƙara rurin neman agaji.

Idanun shi ya ƙara maida wa kanta ya na mata kallo ƙasa-ƙasa ya na son ya gano halittarta,don shi zai iya rantsewa bai taɓa yi mata kallon cikakke ya san ya take ba,shi dai ya san ya yaba da ita har ya ji zai iya aurenta matsayin matar da zai iya aure na kwangila ta haifa mishi yaro.

Wayar da ta miƙo masa ya kai hannun sa zai ƙarɓa ya haɗa har da hannunta ya na ƙare mata kallo tun daga sama har ƙasa,da sauri Juwairiya ta janye hannun tare da fara tafiya a hankali da nufin tabar gurin don jin wani irin tsau  da ta ji jikinta ya yi,yayin da take jin wani ƙarin saƙo daga zuciyarsa ya na aika mata cikin zuciyarta.

" Juwairaah."

Ya kira sunanta ba tare da ya miƙe ba cak tsayawa ta yi ba tare da ta jiyo ba,haka shi ma ya na kwance ya na kallonta kusan tsawon minti biyu,sai ta jiyo gabanta ne ya buga ras!
Da sauri ta ruga zuwa ɗakinta tare da faɗawa kan gado ta saki gwauron numfashi idanunta ta rufe cikin wata irin murya ta ce."Allah na roƙe ka kasa na zama jaruma na gama kwangilata na bar gidan nan kamar yadda na saka ma raina."
Ta nisa tare da ƙara juyawa ta kuma ce wa." Haka kawai ka shigo cikin rayuwata ka hana zuciyata sukuni."

Idanunta ta buɗe suka tsarƙe a na A.m da yake tsaye a gefenta ya na jin abin da take faɗi,ya kai hannu ya fi sau uku da nufin ya riƙe ta amma sai ya kai ma iska nushi don ya na ganin in ya taɓa wata ƴa mace bai yi wa Zainab halacci ba.

Ganin ta buɗe ido sai ya ja baya ya haɗe rai hakan sai ya ɗan tsorata har sai da ta ja da baya ta na kallon shi don ba ta san ya shigo cikin ɗakin ba.

" Ji nan Juwairaah! Ko kaɗan kar ki saka a ranki zan iya rayuwa dake kin ga matata kuma iya ɗan zaman ki a cikin gidan nan,kin ga irin tsananin son da nake mata don bai kamata sai na gaya miki zaki fahimta ba,don na faranta mata na aure ki don haka ki kiyaye duk wani abin da zai sa ki yaudari kan ki,don kin san haka ba mai yuwu wa ba ne sanin kan ki ne ruwa ba tsaran kwando ba ne?"

A hankali ta ɗaga mishi kai ganin ya tsare ta da ido ya na son ya ji amsar tambayar sa.
" Sannan kar ki ɗauka ko na manta dalilin da ya saka na aure ki ne.".
Ya juyo ya na kallonta ya ce da ita." Wallahi na rasa yadda za' yi na fara ɗaukar ki a matsayin matata don ba mu dace ba,ni sai yanzu nake dana sanin da idona da ya rufe na yadda na aure ki,amma duk da hakan zan daure na aiwatar da shirina da zarar kin sami ciki na kai ki wani gurin ki haihu na karɓi yarona mu shafe babin rayuwarmu."

Ya na kai nan ya fice ba tare da ya lura da kukan da take yi ba na baƙin cikin tsanar ta da ya yi,sai dai kuma daga ba ya ta dai na jin haushin kalaman da ya faɗi saboda duk abin da ya faɗa gaskiya ne,ita ma ta karɓi auren sa ne saboda ta ta ceci ran mahaifiyarta da ɗan'uwanta.

Washegari da safe Juwairiya na kwance hayaniyar masu gidan ya tashe su wanda ta kasa gane ko menene,amma ta tabbata ba lafiya ba jin yadda suke magana sama-sama musamman muryar Zainab wacce har kukanta ta ji.
Matuƙar tsoro ya kamata ji ta yi ta ƙara mugun tsoron A.m don ba ta san haka yake da tsiya ba.

Ta na zaune a ɗakinta ta yi tsumu so take ta haɗa abin karyawa amma ba zata iya fita ba jin yadda suke ta ɗaga murya kamar za su dambace.

Mamaki ya kama ta sosai wai masoya ne suke irin wannan faɗar,ganin sun ƙi yin shiru da sauri ta shige kicin ba tare da sun gan ta ba,ta fara ɗora abinci jikinta na rawa gani take kamar a kanta faɗan zai ƙare.

Ta na shirya a binci a dinning ta ga A.m da ƙatuwar troley ɗin sa ya na ja, ransa kamar an aiko masa da mala'kan mutuwa, ba tare da ya kalle ta ba ya fice daga gidan.

Ba'a jima ba sai ga Zainab da na ta jakar ta na waya bayan ta gama wayar ta kalli Juwairiya ta ce " Ke wai me sunan ki baki gaya min ba?Ko ki na jiran na tambayeki ƙila uwar ki zan ci da sunan."

A hankali Juwairiya ta furta." Juwairiya sunana."Yayin da hawaye suka fara turereniya a fuskarta.

Tsaki ta saki." ko ma mene ne ni tafiya zan yi kuma ƙasar zan bari, ban ce kije ko ina ba kar a kwashi kayana akai gidan matsiyata,ki kula min da gidana duk abin da kike so ga waya ki kira ni in da matsala."

Jefa mata wayar ta yi a jikinta ta fice ba tare da ta yi tunanin za ta iya fashewa ba.

Tsananin mamaki ya kama Juwairiya yanzu ne ta gane musabbabin faɗar su.Da sauri ta leƙa ta windo don idanunta su fita da shakkun kayan da ta saka za ta ƙetare wata ƙasa a matsayin ta na matar aure.

Haka ta wuni sukuku daga kallo sai kwanciya tunna ba masu gidan da za ta yi musu girki.Da daddare sai ta kasa bacci saboda ita kaɗai ne sai masu gadi,Baba in ta gama ayyukanta gida take tafiya saboda ba ta da nisa sosai da gidan.

Kasa bacci ta yi ta na ta juye-juye girman gidan yake matuƙar tsorata ta, sai take ganin kamar wani zai shigo ga ihun karnikan gidan da suka hana kunninta saƙat!

Da ga ƙarshe ma tashi ta yi ta ɗauro alwala ta yi sallah sannan ta ɗauki alkur'ani ta na karatun suratul Ali imran don ta samu ta yi bacci.

A ƙalla mutane gidan sai da suka yi sati biyu ba su dawo ba.A.m ya fara dawowa ranar talata da rana dama tun da safe Zainab ta kira Juwairiya ta gaya mata zai dawo ,don haka ta shirya abinci wanda Zainab ta saka direba ya siyo duk kayan buƙata na girki.

Misalin biyu da rabi ya shigo da jakar shi rataye  a kafaɗar sa,sai dai kamar mahaukaci ya shigo saboda zargin sa da yake na Zainab ta yi tafiya zuwa Dubai saro kaya duk da ya hana ta.
Duk da cewa ta ji shigowar shi sai ba ta fita ba ta yi zaman ta a ɗaki ta na jan carbi,domin ta sama ma kanta natsuwa.

" Ina Zainab?"

Muryar sa ta ji lokacin da ya banko ƙofa ya shigo da sauri ta matsa ganin kamar zai kai mata

duka lokacin da yake tambayarta.

Ba ta ba shi amsa ba amma yanayin da take kallon sa ya tabbatar masa da Zainab ta tafi duk da gargaɗin ta da ya yi,cikin ɓacin rai ya lailayo ashar zai yi ko me ya tuna sai ya fasa ya fita cikin ɗakin da sauri.

Juwairiya da sauri ta bi bayan sa saboda tashin hankalin da ta ga ya shiga,abincin da ta girka masa ya yi jifa da kwanonin da suke jere a dinning ɗin,ya zaro wayar sa ya kira ta sai dai har ta gama ringing ba ta ɗauka ba.

Jifa ya yi da wayar ta faɗi a kan tayas ta fashe ya dunƙule hannun sa guri ɗaya ya furta." Zainab ki na son sa min hawan jini sai dai wannan karan ba zan ɗauki wannan iskancin ba,ina mijin ki ki tsallake ki tafi wata ƙasa hakan ba zai yiwu ba.

Idanun Juwairiya suka kawo ruwa sai hawaye ganin ita kuma haka Allah ya ƙaddara rayuwar ta su dun ga sauke fushin su akan ta.

" Ke!"

Ya daka mata tsawar da ya firgita ta sannan ya ci gaba da magana da ce wa." Wallahi yanzu jikin ki zai gaya miki dukan ki na yi zaki saka min kuka bayan na gaya miki na tsani kuka a rayuwata,maza fice ki ba ni guri sannan ki ƙara min wani abincin.

Hakan ya ƙara saka ta sakin wani kukan tuna yadda ta sha wahalar girkin ya zubar kuma yake buƙatar ta ƙara yi masa.
Da sauri ta wuce kicin ta bar shi a falon ya kai gwauro ya kai mari da ga ƙarshe wayar sa ya ɗauka da nufin ya kira A.k,sai dai kuma ya ga aika-aikar da ya yi tsaki ya yi da nufi ɗaki don ya ɗauko wata.

Bai jima ba ya fito bayan ya yi wanka ya canza kaya ko kallon abincin da ta girka bai yi ba ya fice daga gidan.

A haka suke ta zama na rashin daɗi duk da A.m na buƙatar ya kawo ƙarshen zamanta a gidan amma ya kasa,haka dai yau ya daure da nufin zai yaƙi zuciyar sa don ta bar mishi gidan sa saboda ba ya son ganin ta a ciki.

Da misalin biyar da rabi ya dawo gida Juwairiya na falo ta na kallo da ƙaton hijabin ta,ya na hango ta ya tsaki wawan tsaƙi saboda shi haushin hijaban da take sawa yake yi bayan ta san ko shi wanene a gurin ta.

" Wawiya ƙazamiya a haka yadda kike ɓoye jikin ki ko uban me take ɓoyewa shi bai ga abin sha'awa a jikin ta ba."

Ganin sa ya sa ta miƙe da sauri za ta shige cikin ɗakin ta.

"Ke."

Tsayawa ta yi ba tare da ta kalle shi ba don ta san wani wulaƙancin zai yi mata.
Hararar ta ya yi ya zauna akan kujera tare da ɗaukar remote ya canza tasha,sannan ya kalle ta ya ce " Gidan uban wa za ki saboda dodo ya dawo ko?Wai haka kika ga matan aure suna rayuwa a gidan mazajen su kullum cikin hijabi ke sam baki da wayewa ne?"

Juwairiya ta yi sororo ta na kallon shi jin wani sabon salon da ya fito da shi,amma ba ta ce masa komai ba sai kallon shi da take tamkar baƙo a gare ta.

" Maza ki je ki kawo min abinci."

Ya ce ganin ta kafe shi da ido ba ta san shi ma ransa a ɓace yake maganar ba saboda tsanar ta da yake ji kuma wai ta na matsayin matar sa.

Juwairiya ta so ta bi umurni n shi ta cire hijabin sai dai ina sam ba za ta iya ba,don tsananin kunyar shi take da ke,don haka ta ƙi cire hijabin ta ɗauko abincin ta na ije mishi ta ruga zuwa ɗaki.
Bayan ya ci abinci ya na zaune a falon har aka kira magariba ya yi sallah bai dawo ba sai da aka kira isha'i,sannan ya dawo gida ya rufe gidan duk da ran sa a ɓace yake akan Zainab kuma ya rantse in ta dawo sai ta ga abin da zai yi mata,amma sai ya daure ya ɗauki wayar sa ya shiga ɗakin.

" Ki biyo ni ɗakina kin san ba zan iya kwana a ɗakin ƙasƙantu ƴan aiki ba."

Ya fice kallon sa kawai ta yi amma ba ta ce mishi komai ba har ya fita ta gyara kwanciyar ta tare da karanto addu'ar bacci ta janyo bargo ta kwanta.
" Wataƙila maganar Baba Sani ta yi tasiri a  zuciyar sa ya yadda ba ni da kamun kai ne har yake tunanin na bi shi ɗakin sa a she zai bushe da jira na.

Washegari da safe bai ci ko abincin karyawar da ta yi masa ba ya fice daga gidan, don ko da ta gaishe shi harara ya banka mata.
Sai abin ya ba ta dariya kawai ta ruga da sauri ta laɓe a ƙofar falon ta na kallon sa har ya fice saboda wankan da ya yi ya tafi da imanin ta.

Sakin labulen ta yi ta zauna a falo tare da ɗaukar filo ta rungume a ƙirjinta ta na jin wani irin nishaɗi, don ko kaɗan ba ta yi tunanin rayuwa tare da shi ba ko da kuwa a matsayin matar sa kuma ƴar aikin matar sa.
Bai shigo gidan ba sai da daddare tare da A.k suka shigo  suna ta hira abin su.
A.k na ta baza ido ya gan ta bai gan ta ba musamman da ya ga Zainab ba ta nan,kallon A.m ya yi da yake ta aika ma cikin sa abinci saboda tun zuwan Juwairiya gidan hankalin sa ya kwanta

na rashin samun abinci.

" Kai wai ina maryar ka ne ?Tun na yanzu madam ba ta nan na san ƙila an samu baby?"

Ya faɗa ya na kallon shi ya na dariya tare da kai mishi duka a kafaɗan sa.Taɓe baki ya yi ya ce.Ina zan sani kai kyale ni da wani amarci Juwairiya muguwar bagidajiya ce kullum cikin hijabi ka san kuma ba haka Zainab take min ba."

Ya ɗan kalli A.k da ya daina cin abincin ya na sauraron sa ya ce."Jiya da na kira ta ɗakina ƙin zuwa ta yi ban san tunanin ta a kai na ba."

" To kai in ban da abin ka A.m ai kai za ka bi ta kuma kuma mace take Hausa dole ta ji kunya."
A k ya ce da shi ya na kallon sa.A.m ya ƙara taɓe bakin sa ya ce." Ok ka manta abin da ƙanin mahaifinta ya ce a kan ta ni ban ga abin kunya ba."
"A haba A.m ka san halin sa kar ka yadda da maganar sa kuma koma mene ne kai ka amince za ka aure ta sai ka ba da azama mu sami baby.".
Dariya suka yi duka daga bisani A.k ya matsa mishi ya kira ta su gaisa ya na zaune ya ƙwala mata kira ba ta jima ba sai ga shi ta fito,kamar dama laɓe take musu ta na jin maganar da suke yi.

A.m tashi ya yi ya nufi ɗakin sa zai ɗauko tsaƙon da A.k ya biyo shi ya karɓa ba tare da ya kalle ta ba.

Da ladabi ta  gaishe shi ya amsa ya na ta tsokanar ta dai murmushi take masa.
" Na so mu haɗu kafin ayi auren ki da shi sai dai kuma Allah bai nufa ba ko Juwairiya?"

Ya faɗa tare da mai da maganar ta tsigar tambaya.Ɗaga masa kan ta ta yi ta na kallon shi " Ok ba komai da ma na so na ɗan miki wata magana ne Juwairiya don Allah duk yadda zuciyar ki za tai ki karki yadda ki saka son A.m a ran ki kawai ki sama ran ki zaki ci arziki ki tafi ne.Ki ɗauke ni a matsayin Yayan ki duk lokacin da wata matsala ta haɗa ku ki sanar da ni."

Ya yi maza ya ƙarashe maganar jin takun A.m daga matakalar bene.Kallon sa ta yi sai kuma ta ji ya burge ta sosai yadda bai ɗauki rayuwar sa da zafi ba.
Ɗaga masa kanta ta yi alamun ta ji amma kuma a cikin zuciyarta sai ta ce.
" Ka makaro A.k da ce wa ka yi na yaƙi zuciyata da take son sa ƙila da na karɓi shawarar ,amma na riga na daɗe da shiga cikin kogin son sa."

Sai da A.m ya yi masa rakiya sannan ya dawo ya tsaya ya na kallon Juwairiya da ta kasa tashi ta na ta tunani a ranta." Me hawayen banza maza ki tashi ki gyara min  ɗakina saboda yau haushina da kike ji sai kika huce akan ɗakin,sam gyaran bai yi  kuma ki ƙara wanke bayi."
Ya faɗa tare da zama a falon kamar ya na son ta gama sai ya shigo.
Wucewa cikin ɗakin ta yi ba tare da ta ce masa komai ba amma ya faɗi son ransa ne kawai duba ga yadda take ba da dukkan lokacin ta in ta je ɗakin sa gyara.

A.m ya na ganin ta shige ya bi ta tare da tura ƙofar a hankali ganin ya shigo ta tsaya dama tun da ta shigo ta rasa mai za ta gyara saboda ɗakin ya na tsaftace da kyan sa.

" Ki zo mu kwanta a gadon da baki taɓa hawa ba amma albarkacin aurena zai saka ki din ga moresa in matar so ba ta nan."

Hawaye suka wanke mata fuska ba ta ce mishi komai ba kuma ba ta motsa ba bare ya saka ran za ta hawo,asalima gaban ta ne ya faɗi ras!

Hannunta ya jawo ya na faɗin." Na lura kuka shi ne farin cikin ki to ki sani ba zan taɓa buɗe bakina rarrashe ki ba,ko na ɗauki hannuna na share miki hawaye da su.

Yanayin da suka shiga a ranar yanayi ne mara fasaltuwa da bayyanuwa a gare su musamman Juwairiya da ta sha kuka har ta gode ma Allah,domin kwana ta yi ta na kuka ko kaɗan ba ta bar shi ya rintsa ba,wanda in ta tuna dalilin kukan na ta biyu ne sai ta ƙara sakin wani kuka.

A.m da bacci ya fara ɗaukar sa a hankali bayan wata sabuwar duniya da ya shiga kuma ya kasa fahimtar wace duniya yake ciki,kukan da take yi ya na ɗaga masa hankali ya yi maganar duniya taƙi yin shiru,har ya gaji ya ƙyaleta ya rintse idanun sa da ƙarfi ya na son bacci ya ɗauke sa.
Ganin taƙi dai na kukan ya janye bargon da ya ƙudundune kan sa da shi ya kunna fitilar ɗakin."

Ke wai ke."

Sai kuma ya yi shiru daga ninyar faɗar da yake ya yi mata ya ɗan sausauta murya ganin dare ne ya ce." Ko fa wace mace da kika gan ta  a gidan mijinta da haka ta fara.Kuma idan bakya son haka ba sai ki gaya min ki gode ma Allah auren kwangila muka yi so ba daɗe wa za ki yi da ni ba."

Hakan sai ya saka Juwairiya ta ƙara fashewa da kuka ganin ta ba ma mutumim da ya tsane ta rayuwarta,ga shi bai san mahimmancin ta ba bayan wahalar da ta sha yake gaya mata waɗannan kalamai.

Bakinta ta murguɗa a ranta ta ce." Mugu kawai azzalimi."sai kuma ta ci gaba da kukanta wanda A.m ya lura harda shagwaɓa don shi ya gama fahimtar ta shegen shagwaɓa ne da ita shi ya sa da an yi magana sai kuka.

Wani irin walƙiya a ka saki lokaci guda aka fara tsawa nan ne A.m ya fahimci garin hadari ne ya taso,da sauri ya sauka don ya duba ko windina a kulle ne kawai sai ya tsinci kan shi da jin daɗin ya na yin garin har ya buɗe labule ya na shaƙar iskar gurin.

Iskar ya ƙara ma Juwairiya zazzaɓin da ta ji ya saukar mata ganin haka sai ya rufe windon ya

na addu'ar Allah ya sa ta yi shiru kenan,jin ta sassauta sautin kukan da take yi sai ya koma ya zauna.

Wayar sa ta fara ruri da sauri ya ɗauka don gabansa ya faɗi ya na tunanin waye da daddare zai kira shi,ganin numbar masoyiyar sa ya sa shi miƙewa da sauri take ɓacin rai ya bayyana a fuskar sa.

A wannan lokacin da yake duba wayar sa aka tsuge da ruwa sosai kamar da bakin ƙwarya. Zubbur ya miƙe ganin numbar Zainab ce ya yi kamar ba zai ɗauka ba,saboda tun da ya gaya mata zai dawo ta de na ɗaukar wayar sa ashe mara mutuncin tafiya ta yi tabar ƙasar.Sai kuma ya kanga wayara  a kunnin cikin tsanani ɓacin rai a ransa ya na tunanin Allah kawai zai raba ta da shi.

" Hello zauji don Allah gani a airport ka zo ka ɗauke ni kuma na samu ƴar matsala da kayana har mutumim ya na min barazana.Ga kuma ruwa da ake yi kazo ka ji zauji."

Wani irin tashin hankali ya ziyarce shi ya kalli Juwairiya da take cikin wani hali don shi kan sa ya san ya wuce gona da iri,kuma ba tare da sanin haka ba ya kuma kalli kansa da har yanzu ya kasa tantance duniyar da yake ci.

Tunani ya fara yi ko Zainab ta hauka ce ne da za ta dawo da tsakar dare sai ya ɗauki wayarsa da nufin ya duba lokaci, ai wallahi ba zai fita yanzu ba sai dai koma mene ne ya faru musamman da ta ɓata masa rai ta yi tafiya ba tare da izinin sa ba.

Tsananin mamaki ya kama sa da agogon wayar sa ya nuna mishi ƙarfe biyar da mintuna,ya na cikin kokwanton ko wayar sa ce saitin ta ya goce sai ya ji ladani ya kwaɗa kiran sallah.

Da sauri ya yaye labulen ɗakin don ya ƙara tabbatar ma kansa take kuwa ya ga har hasken alfijir ya keto gari ya fara wayewa..
Sai hankalin shi ya ƙara tashi musamamn da Zainab ta turo masa tsaƙon ba sai ya zo ba,don sun
 Anan na gama reposting na "SAKACINA KO HALIN MAZA". Duk wacce take son complete ɗin sa an kammala littafin za ta iya siya a kan naira 600 ta wannan asusun bankin 08144072423 Jamila Lawal opay. Littafin an riga an kammala shi reposting na yi. Littafin "RANAR WANKA, BA A ƁOYEN CIBI" Ya zama complete za a same shi a 600 ga mai buƙata sau ya tura ƙudinsa ya sha karatu lafiya. Akwai kuma "KURA DA FATAR AKUYA 600

daidaita da mutumim yanzu haka ma suna hanyar gida,saboda mijin Anti Fati ya turo direba ya ɗauke su kuma duka za suzo gidan.

Anan na gama reposting na SAKACINA KO HALIN MAZA. Duk wacce take son complete ɗin sa an kammala littafin za ta iya siya a kan naira 600 ta wannan asusun bankin 08144072423

Jamila Lawal opay. Littafin an riga an kammala shi reposting na yi.

TO FA JUWAIRIYA GASKIYA NA TAUSAYA MIKI DA RANAR KI TA KASANCE A HAKA KOMAI DAI MENENE ALLAH YA BAKI HAƘURI DA JURIYA.KUCI GABA DA BIBIYAR LINTAFIN SAKACINA KO HALIN MAZA

NAƘI YIN TYPING DA YAWA SABODA GASKIYA FANS BA KWA RUWAN COMMENT SAI DAI KU YI TA BIYO NI TA PC KUNA FAƊIN ALLAH YA ƘARA FASAHA INA GODIYA AMMA NI NA FI SON NA GA RUWAN COMMENT YA NA TASHI DON GAKA IN KUNA SON NAADIN GA TYPING DA TSAWO KU DIN GA COMMENT.

TAKU

JAMILA LAWAL ZANGO

ƊUBBIN GAISUWA GARE KU SABODA COMMENT ƊIN KU YA NA SAKA NI NISHAƊI.